wanka yasa kananun kaya masu kyau da sneakers akafanshi dawata jaka na LV abayanshi sai key mota kaganshi sak ubanshi yana zuwa gaban Abee yace “good morning Abee” “morning Abdallah what time kakeda lectures yau” yana gyara agogon hannunshi yace “Abee by 8 ne yanzu 7 harda minti goma bari nai sauri idan lecturer ya shiga baya kara bari wani yashiga” yay maganan yana mikewa zai wuce Abee yace “go and have breakfast kafin kafita” strictly Abee yay maganan daidai nan Hajiya tafito tace “Alhamdulillah ai yau uban naka nagida naga ta yanda zaka tafi makaranta bakai kari ba yaro kwata kwata bayason cin abinci” turo baki yama Hajiya yajuya yawuce dinning danyi kari Abee yadauke idanunshi daga kanshi yajuya yakalli Hajiya data zauna kan 2 sitter dake facing nashi ahankali yace “ina kwana Hajiya” “mun tashi lpy Imran” ahankali yace “Alhamdulillah Hajiya” yadanyi shiru sai chan yakalleta yace “me kuke bukata agidan”? Anatse Hajiya tace “fruits ne kawai babu amman akwai kayan abinci da komi lastweek ai kasa Hamza yayo chefene” gyadamata kai yayi yace “magungunan kifa”? Tana kallonshi tace “basu kareba har yanzu” daidai nan su Anty Binta suka fito daga kitchen zasu fara jera abinci a dinning Hajiya tace “ku kawo nan muci anan dan Allah ni wlh bason cin abinci wajen nan nakeba” kawo abincin sukayi duk suka gaida yayan nasu Sajida yafara kallo batare daya amsa gaisuwanta ba yace “when are you going back to your husband house”? Murmushi tayi tace “Yaya dazaran yadawo daga lagos zaizo yadaukeni next week yace zaizo ni wlh banma gaj…..” mugun kallon daya mata yasa tahadiye maganan yakalli Zainab kafinma yayi magana da sauri tace “Yaya Imran ni sai ranan Friday kaga yau monday” dan dariya Hajiya tayi tace “yara duk sun zo sun taremini gida sun hanani sakat” turo baki Zainab tayi tace “bamason rabuwa dake Hajiya” dasauri Hajiya tace “aure kam yagaji haka ingayamuku” daidai nan Anty Binta takalli Abee tace “mezan zuba maka akwai waina da pepper soup na cowtail, saikuma chips da egg, akwai kuma dumamen tuwo da kuka sai shayi da kunun gyada” ahankali yace “I want masa da shayi” murmushi tayi tashiga zubamai daidai nan Hamza ya sauko ya shirya cikin suit yayi kyau Hajiya dake kallonshi tace “kai lpy kaci suit yau”? Murmushi yayi yakalli Ya Imran da ake bama abinci yace “yau zamuyi baki a office za’a kawo wasu yan makaranta excursion suga company namu idan Ya Imran yayi welcoming nasu nine let’s just say tourist dinsu to kinga I need to look good” tabe baki Maman Aneesarh tayi yadaga mata gira daya Hajiya ta kalli Abee daya fara kurban shayi ahankali anatse tace “zakuyi baki shine kai me kampani gabaki daya ko shiryawa bakayiba” ahankali yazare kofin shayin daga bakinshi yace “idan nagama zan shirya” zama Hamza yayi yakarbi abincin da Anty Binta ke bashi yace “wlh yaran nan naku suyi sauri inba hakaba babu makarantan dazan kaisu saidai ku ku kaisu” Hajiya ta dubi Anty Binta dake bama yara abincin tace “wai ina jikata Kausara ne jama’an gida”? Dan dariya daga Binta, Sajida, Zainab da Maman Aneesarh sukayi, Maman Aneesarh tace “Hajiya kin manta shiryawan Kausar ne” Zainab tace “manyan yammata yan 100 level JJC saida gayu” daidai nan Abdallah yatashi daga dinning yace “nina tafi” atare kowa na dakin yace “Allah kiyaye hanya, Allah bada sa’a Doctor” karasowa wajen Abee dahar lokacin shayi yakesha baima taba wainar da aka zubamai ba yace “Abee natafi” hannu Abee yasa a aljihu 10k yaciro yabashi dasauri yakarba yana murmushi yace “thank you Abee” ahankali yace “drive safe” murmushi yayi yace “I promise Abee” yajuya dasauri yawuce daidai nan Kausar ta sauko tana sanye da doguwan rigan atampa mai kyau tasaka bakin safa akafanta da flat shoe sannan tarike milk hijabinta ahannu, da dankwalinta a hannu, da jaka da ribbon a hannu tana shigowa ajiyesu tayi akan kujera tazo wajen Abee da sauri tabashi ribbon din tace “Abee kamamini gashin” baki Hajiya

tasake tace “yanzu kiwuce duka matan dake dakin nan kitafi wajen ubanki yamiki parking gashi dakecin abinci” turo baki tayi tawuce tabama Zainab tace “samin Anty” murmushi tayi takama gashin da baida wani tsawo tace “kawo kallabin na daura miki shima kawowa tayi tadaura mata sannan tazauna tana breakfsat dasauri sauri hada ido tayi da Abee dake kallonta, kallon daya mata kadai yasa ta faracin abincin ahankali anatse dan yahanata cin abinci da sauri adolenta ta natsu ta cinye tass sannan ta tashi tasaka hijabinta itada sauran yaran sukabi Ya Hamza dazai kaisu sukabar gidan.

2 slice na waina yaci acikin hudun da aka sakamishi sannan yatashi yawuce sama dan shiryawa, tsaf ya shirya cikin black suit dayasaka wata farar Riga aciki mai shegen kyau, baisa boturin jacket na suit dinba hakan yasa kana iya ganin farin, yasa black Wandon suit din daya tsayamai a idon sahu as usual yanda tsayin wandunanshi suke, covershoe yasaka na gucci dake wani shining, wannan karan babu any hula akanshi hakan yasa gashin kanshi yay wani kalan kyau ya kwanta lub sai kyalli suke, ahankali yake saukowa rikeda wata jakan laptop a hannunshi daga Hajiya har duka matan ta duk suna falo da Matan Ibro itama yanzun nan tashigo tanacin ragowan waina dan tsohon ciki ne da ita bata iyacin abincin data dafa, ganin Abee yasa akunyace ta sauke kanta dan kowa nauyin Abee yakeji cikeda kunya tace “ina kwana Abee” kallo daya yamata yadauke kai yace “Alhamdulillah” yakalli Hajiya yace “natafi Hajiya” dan murmushi tasakin mai tace “ubangiji Allah yabada sa’a yakara daukaka” ahankali yace “Ameen” su Anty Binta atare sukace “Allah bada sa’a Yaya” bai amsasu ba yafice suna sonshi bana wasaba Ya Imran shine komi nasu, ci sha sutura, duka kanninshi dukansu duk wata kowacce yana bata kyautan kudi hatta matan Ibro, banda Ibro da Hamza da suma tunda sun gama makaranta duka yasasu a company shi duk suna aiki awajen, school fee na marayun yaran Maman Aneesa na kanshi magani komi, sai su Abdallah da Kausar dake university Kausar this year tafara tana 100level tana karantan Mass com, shikuma Abdallah na 300 level medicine, Abdallah nada bala’in kokari da kwazo ga natsuwa da tausayi da kirki saisa Abee yabashi motan kanshi dudda he’s 22yrs dan yawanci early morning lectures yake kuma bayida gara gara, itama Kausar tana kokari ba laifi amman ba kaman Abdallah ba randa sukeda lectures lokaci daya da Abdallah shi yake wucewa da ita idan kuma ya bambamta Hamza ke kaita.
EPISODE5️⃣

Exquisite world collections

Muna sai da jakakkuna da takalma masu kyau wanda idan kuka siya ba lallai ku sake ganinsu wani wuri ba . I assured you. Ku siya ku godemin daga baya domin ingancin kayana. Ina turawa ko ina kike ni kuma Ina Abuja.

Wannan shine instagram handle dina.

I'm on Instagram as shukhria. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=ithkqozo1zuq&utm_content=oeu4f73

08108517010 wannan shine number wayana kuma dashi zaku sameni a whatsapp.

Ahankali cikin muryan bacci wata kalan siririyan murya mai shegen dadi da zaki tace “Gwaggo yunwa” shiruu kakeji banda sound na munshari dake tashi acikin duhun dakin, cikin wani irin raw voice din nan dake nuna bacci mutum yake ko cikin bacci mutum yake maganan tace “Gwaggooooo yunwaaaaaa!” Firgigit munsharin dake tashi daga dakin dakeda duhu nan ya tsaya kaman anyi ruwa an dauke karan hannu kawai ketashi daga dakin dake nuna ana tattaba gadon alamun abu ake nema sai chan aka kunna wani bright torchlight daya wani kalan haska dakin bauuuu kaman wutan lantarki, wata tsohuwar mata ce da akalla zatai 70 kokuma 72 haka kwance kan wani makeken gado mai kyau tana sanye cikin riga bubu da zani na atampa gefenta kuma wata yarinya ce mai jiki sosai kwance ta kankame Yar tsohuwar kaman zata koma cikinta idanunta akulle tana daure da wani pink towel, kallon fuskanta yar tsohuwan tayi tace “Ohh ni Safara’u Allah ubangiji ka nunamin ranan dazanyi bacci tundaga farkon dare har karshe batare da wannan fitinanniyan yarinyar ta tadani tanajin yunwa ba, Ya ubangijin sammai da kassai Ya ubangijin dake busa numfashi rokonka nake Allah ka kawomin ranan nan da gaggawa” cikeda takaici tace “aisai kitashi ga shayinki chan cike a flask, namanki da somasa nacikin kula, buredi ma na wajen idan kuma harda shinkafa zakici to wlh dakanki zakije kitchen kidebo dan kin ganni nan ban barin gadon nan Lulu” still cikin baccin batare data bude idanunta har lokacin ba tace “Gwaggo wlh ki kawomini nan” tai maganan kaman mai shirin kuka dayasa babu shiri Yar tsohuwan takai hannayenta ta kabarda hannunta dake kan jikinta tace “aisaiki sakeni intashi yarinya kaman jikan mayu” tashi daga kan gado tayi tasauka tawuce wajen da flask da wata katuwar kula da cup da duk suke kan faranta ta duka da kyar ta dauka tazo gaban gadon ta ijiye sannan ta kalleta still idanunta arufe suke tace “tashi to kici” kaman jira take ahankali ta tashi zaune idanunta still arufe tana rike da gaban towel dinta dake shirin zamewa sannan ta gyara daurin zanin da kyau tana turo baki tashiga bude idanunta ahankali, wasu hadaddun kitson kalaba ne kan yarinyar dasuka zubo mata har tsakiyan baya an jera beads a bakin kitson kaman wata Yar yarinya, wani kalan kibane da yarinyar bana wasa ba, irin asalin yaran nan ne da ake kira da chubby, idan kaga jikinta zaka dauka she’s about to burst ne dankoni dazu dana ganta kwance kan gadon nadauka Babba ne sai yanzu dana kalli fuskanta Nagane yarinya ce da duka duka bazata wuce 19-20yrs ba, wasu kalan cat sexy eyes gareta dayasa idan ka kalli fuskanta saika kasa janye idanuwanka akanta for some seconds sabida kyawun idanunta, tanada cikan gira kuma baki sidik hakama gashin idanunta da dan siririn hancinta, tanada kumatu rubu rubu dasu that looks super cute on her dawasu kananun succulent pink lips da kana kalllonta yana bada all this kananun jariran yaran nan dakeda kiba din nan sosai, skin dinta is like butter ne ko milk banmasan yanda zan siffanta muku ba but kaganta zaka dauka idan ka latsa jikinta jini zai fito ne, everything about her is chubby harta yatsun hannuwanta dana kafafunta burbur dasu kaganta kaman zata fashe, sauka tayi ahankali daga kan gadon tana kara gyara daurin towel dinta da kyau sannan akan soft carpet din tana bude flask din ahankali duk cikin bacci itakuma Gwaggo tawuce tabude bandaki tashiga. Shayin tazuba cikin wani babban cup dayaji madara da Milo yana tururi sannan tabude babban kulan

samosa ne kusan 20 aciki da naman kaza da akai pepper chicken dasu guda 5 da sauri tashigaci tass ta shanye shayin kofin takara bude flask tadeba tacika tacigaba daci itakuma Gwaggo tafito ta shimfida dadduma kawai tahau tass ta shanye shayin da samosan da duka naman gyatsa tayi sannan ta tashi tahau gado ta gyara kwanciya ta kwanta murya chan kasa cikin bacci tace “Gwaggo kizo mukoma bacci” hararanta Gwaggo tayi tace “nafila zanyi gwarama kiyi baccin ki dan kinsan da asuba zan tadaki yau monday zakuje iskuko oho dai amakaranta” dan gajeren tsaki yaja tanajan bargo ahankali akuma shagwabe tace “ni bazanje ba Mandawari na zaiyi live broadcast karfe shadaya na safe yau” hararanta Gwaggo tayi tace “asheko dake da shegen gantalallen Mandawarin daharyau baimasan ko akwai mai kamanki aduniya ba babanku zai hada yaci ubanku” murguda baki tayi tareda lumshe ido kafi kacema bacci yay awon gaba da ita ganin haka itama Gwaggo ta kishingida da bango danta dan runtsa kadan tasan inhar batahau ba nan bada jimawa ba zata tashi da kanta dan Lulu bata iya bacci bataji ta rike mutum ba tun tana yar kankanuwan ta take haka.

5 na asuba tabude ido ahankali takalli inda Gwaggo take kan dadduma sannan ta tashi zaune ahankali tana jaye zanin gadon tana murmushi tasauka dagakan gadon da sauri tawuce bathroom na cikin dakin da ruwan zafi tai wanka tai brush sannan tai alwala tafito daure dawani towel din bayan ta wurga wanda tacire kan washing machine tazo dakin bataga Gwaggo awajenba hakan yasa tadauki wani dogon hijabi tadaura akan towel na jikinta tahau kan dadduma, tana sallame sallan ta tashi batare datayi azkar ba tawuce tafita daga dakin tashigo falonsu wani chocolate dake kan center table na cabry diary milk tadauka da sauri tana budewa tai wajen kofa daidai nan Gwaggo tafito daga kitchen tace “ina kuma zaki gari bai gama wayewa ba Lulu”? Batare data kalli Gwaggo ba tace “wajen Ya Samira zani” baki Gwaggo tabude zatai magana amman tuni tabude kofan tafice Gwaggo tabita tana kwalamata kira tace “bazakizo kisa kaya ba da asuban nan kina yawo daga ke sai tawul babu dan kwali akanki Lujain” ko juyowa batayi takalli kakartata ba saina kara sauri datakeyi zuwa babban flat din gidan tana tafiya kaman Kazan agric dataci takoshin nan tana tafiya da kyar tana tafiya tana ballan chocolate din hannunta tanaci, gidan dan Babba ne ba laifi kana ganin yanayin tsarin gidan kasan ba laifi gidan masu rufin asiri ne daidai gwargwado, bude kofan flat din tayi tashiga dakin tsaf tsaf sai kamshi yake babu kowa afalon direct tawuce wani daki dake corridor dataji hayaniya budewa tayi tashiga da sauri tana murmushi, yammata uku ne acikin dakin dake dauke dawani babban gado na daidai rufin asiri ga daddumai da hijabai akasa kana ganinsu hancinsu zaisa kagane sudin duka sisters ne saidai su kaf dinsu black beauties ne kuma ko kadan basu da jiki kaman ita su sirara ne yammata sosai, duk kallonta sukayi suka watsar amman ko ajikinta wani kalan murmushi tayi tamaida kofan tarufe takaraso cikin dakin tana kallonsu daya bayan daya, Babban cikinsu wacce akalla zatayi shekaru 23 ne da waya ke kunnenta tace “Baby ina zuwa zan kiraka” sannan ta katse wayan takalli wacce ta shigon tace “Lujain ba jiyan nan da daddare Baba yagama miki magana kan zama da towel dakuma rashin daura dankwali ba” dan yatsine fuska tayi kaman zatai kuka ashagwabe tace “mancewa nayi ban daura dan kwallin bafa Ya Samira” dasauri wacce takira da Ya Samira tace “to towel dinfa” dan turobaki tayi tace “wlh zafi nakeji idan nasa kaya” daya daga cikin sauran biyun matan ne taja tsaki tace “yarinya gabaki

daya Gwaggo tamaidata mara saiti, ba dole kidingajin zafi idan kinsa kaya ba, jibeta kaman buhu" da normally ne da yanzu tai kuka da aka kirata da buhu but yau she's extremely happy hakan yasa tace "wlh banda lokacin ki Ya Abida amman gobe ki tareni ki kirani buhu kiga abinda zai faru" yunkurowa Abida tayi kaman zata daketa hakan yasa da sauri Lujain din takoma baya Abida tace "maimaita abinda kikace"? Dauke kai tayi dayan sister da tundazu batai magana ba tace "Ya Abida inba so kike yau duk mutafi school da bakin ciki ba kada kitaba yarinyan nan yanzu dan wlh bamuba har Baba da Mama ransu yau saiya baci akanta kindaisan fitinan Gwaggo sarai" kaman jira Lujain din take jin ankira Gwaggo  kwafa tayi tace "barta ta tabani ma tagani Ya Habiba" ganin rikici zasuyi yasa Samira tace "ni dan Allah ku kyaleta zonan kifadamin meya kawoki wajena da asussuban nan keda nasan war haka baki tashi ba" murmushi tayi ta harari Abida da Habiba tawuce wajen samira kaman maison gulma tace "ni akunnenki zan gayamiki" kunnen Ya Samira tabata magana tayi mai tsawo sannan ta tashi wani mugun kallo Samira tamata tace "chabdi wlh bazan baki ba hakanan" kaman zatai kuka tace "please Ya Samira kome kikeso zan miki Allah" shiru Samira tayi tana kallonta hakan yasa tace "wlh kuwa" murmushi Samira tayi tunawa da wani abu tace "inhar kin yarda zaki fasa asusun ki kibani duka kudin ciki zan baki wlh dama banda kudin ankon Aisha kinga nasamu" kaman zatai kuka tace "kai Ya Samiraaa duka fa kikace" hararanta Samira tayi tace "ashe baki cika crush din Mandawari ba, ni wlh idan inason wani celebrity babu abinda bazan iyayi akanshi ba, kikasan ma ko a live din dazaiyi yau yaraba ticket na zuwa kallonshi a stadium idan zai buga kwallo basaikije ba, kuma yana ganinki zaice yana sonki kinga yanda kikeda kyau ne" wani kalan mugun murmushi tayi dayasa kumatunta ya lotsa abin kaman wani machine ne awajen ya bala'in haska fuskanta, Abida dakejin firansu ne ta tsoma baki tace "Ya Samira stop deceiving this girl for your personal interest, international player irin Muhammad Mandawari kyakkyawan footballer hadadde ga kudi bazai taba cewa yanason wannan buhun yarinyar ba ko itace last woman on earth wlh" wani abune yatokarema Lujain wuya tajuya tana kallon Abida dake kallonta hararanta Abida tayi tace "yarinya abincin dazataci dukanmu nan bamu iya cinshi, tsakar dare kaman diyar aljanu dansu ke fatin abinci tsakar dare haka itama ketashi taci nata, Gwaggo kawai tabude mata ciki, tayaya ma Mandawari zai dauketa? Wlh tafi karfinshi" daga Abida har Habiba suka kwashe da dariya itakuma Samira tarike nata dariyan dan tana hango samun da zatayi, Habiba dake dariya tace "Mama ma tace babu wanda zai taba cewa yana sonta balle harma Ya aureta bakiga ba duka yan class nasu nada saurayi ita mazan ajin ko kallonta ma basayi bata burgesu everybody gets irritated with cin abincin Lujain da kibanta" juyawa Lujain tayi fuuu zata fice dasauri Samira tariketa tahararesu tace "don't mind them yan bakin cikine Mandawari will acknowledge you one day as his die hard fan sannan zai soki harma ya aureki" sosai hawaye yacika mata idanu ahankali tace "are you sure Ya Samira bazaice nacika kiba ba" murmushi Samira tamata tace "ai kiba halitta ce kuma shi so comes from heart inhar na gaskiya ne ko kinfi kowa kiba aduniyan nan he will love you and cherish you, now smile for me muje mukarasa deal din inhar zaki kawo kudin yanzu zan baki wayan ki kalli live dinshi idan nadawo daga school na karbi wayata kin yarda" dasauri ta gyadakai murmushi Samira tayi tace "to jeki kawo kudin kafin nan nagama waya da Baby" da sauri tajuya tafita su Abida suka bita da harara sukace "wawiya kawai tama dawo ta dauke ledan chocolate din nan data ijiye mana anan dan nan ba dakin kakarta bane data maida bola ba".

EPISODE 6

Exquisite world collections

Muna sai da jakakkuna da takalma masu kyau wanda idan kuka siya ba lallai ku sake ganinsu wani wuri ba . I assured you. Ku siya ku godemin daga baya domin ingancin kayana. Ina turawa ko ina kike ni kuma Ina Abuja.

Wannan shine instagram handle dina.

I'm on Instagram as shukhria. Install the app to follow my photos and videos.
https://www.instagram.com/invites/contact/?i=ithkqozo1zuq&utm_content=oeu4f73

08108517010 wannan shine number wayana kuma dashi zaku sameni a whatsapp.

Tana fita daga dakin daidai wata mata wacce kana ganinta kasan itace mahaifiyar yammatan datafito daga dakinsu sabida yanda sukai kama da mahaifiyar tasu, tsayawa tayi ahankali tace “Mama ina kwana” kallonta Mama tayi daga sama har kasa taja tsaki tawuce hakan yasa itama tawuce daidai tabude kofa zata fita daga falon taji Matar tace “duk randa aljanu zasu shigeki wlh saina bada sadakan dubu ashirin” batace komiba bude kofan dakin tayi tafita daidai lokacin wani magidancin mutum na karasowa gaban dakin sanye da jallabiya shima tareda wani babban yaro wanda bazai wuce 25yrs ba, wani mugun kallo dayama yarinyar yasa kawai jikinta yahau rawa kafinma yayi magana kaman zata fashe da kuka tace “Baba dan Allah dan Allah Baba kayakuri karka doken dan Allah” juyawa tayi zata koma dakin tsabagen rudewa saikuma tasake juyowa da sauri ta kwasa aguje tai side din kakarta mahaifinta yabita da kallo kaman zai doketa da idanu, ahankali yaron dake taredashi yace “kamata hakuri Baba please” dan ijiyan zuciya Baba yasauke saikawai yabude kofa suka shiga falon shida yaron.

Bata kara fitowa daga dakinsu ba sabida tsoron gamuwanta da Baba, saida tasake wanka dan haka take kaman kifi arana zata iya wanka sau ashirin sannan ta shirya cikin kayan makaranta, shima makarantan sabida Baba na nan ne da wlh bazataje ba, wani white long sleeve rigane daya tsaya a cinya sai kuma wani dogon gown ash dazaka daura akan farin rigan sai abun yayi kaman biri da wando dayay mata kyau sosai, zama tayi Gwaggo dakanta tashiga samata safa akafa itakuma tana kirga kudin asusunta data bude Gwaggo tace “wai Mezaki da kudin ki dakike tarawa ma salla iyye”? Turo baki tayi tace “wani abu zanyi” tabe baki Gwaggo tayi tana karasa saka mata black cover shoes nata tace “kyadaiji da rigimanki baran biyemiki da safen nan ba dan na lura neman abinda zaisa bazakije makaranta kike ba” Gwaggo tai maganan tana kawo mata wani fine black bag pack tace “ga jakan ki” karban jakan tayi tabude da sauri chocolate daban daban da aka zubamata ta kalla da biscuit da juices kala uku da goran ruwa saikuma wani dan karamin flasks na snacks sannan tadago kai takalli Gwaggo kirji Gwaggo ta dafa tace “menene kuma ni Safarau dazaki dallamin miyagun idanuwan nan naki” amugun

shagwabe tace “baki samin yoghurt ba Gwaggo” kaman Gwaggo zatai kuka cikeda lallashi tace “wlh bansan yoghurt dinki sun kareba Lulu kiya kuri zansa Baban ku yasayo yau tashi muje chan palour” makema Gwaggo kafada tayi idanunta sun cikada kwalla har kyalli suke amman basu zuboba rudewa Gwaggo tayi tazauna kusada ita cikeda bala’in lallashi takai hannunta tanajan kumatunta tace “haba mana Lulu na yarinyan datafi duka yaran duniya kyau so kike ajimu, kema kinsan kome kikeso sai inda karfina yakare ko wannan ma bansan yakare bane kiyakuri kina dawowa zaki tadda yogurt naki” makema Gwaggo kafada tayi still ita bata yarda ba Gwaggo tace “to yanzu mekikeso? Ni wlh kin fitineni Lujain kin hanani sakat aduniya, zanfa tattara nakoma kauye nabarki” kaman jira take fashewa tayi da kuka sosai kaman ana yankata ta tashi fuuu tafice ko jakan bata daukaba da sauri Gwaggo tadau jakan tabita abaya tana kwalamata kira tace “Lujain zoga dubu daya saiki saya wlh wasa nake babu kauyen dazani nabarki, nima ina zan iya rayuwa babu ke kinmini nisa” kojuyowa Lujain batayiba sai kukan datake daya cika gidan gabaki daya yana eco daidai Baba yafito daga falo chak ta tsaya anan tsakar gidan kukan yamakale awuya Gwaggo takaraso dasauri tana hararan Baba tace “kaikuma meya fito dakai ina ruwanka damu ai magananmu mukeko Lulu” da sauri Lujain ta gyadama Gwaggo kai tana goge fuskanta da bayan hannu, strictly Baba na kallonta yace “collect your bag muwuce school” ahankali tamika ma Gwaggo hannu, Gwaggo tace “yauwa diyar albarka zan sayamiki kafin kidawo kinji ga jakan” karban jakan tayi ta goya Baba yafito zai gaida Gwaggo tace “jeka kaisu kadawo ai ina nan babu inda zani” girgiza kai kawai yayi yawuce Lujain tabishi haka su Samira ma dasuka fito duk sun shirya su sun fara university, suna shiga bayan motan murya kasa kasa Samira tace “ina kudin”? Mikamata kudin Lujain tayi aboye itama taja jakan Lujain tasamata wayanta da earpiece aciki tace “ai kinsan password dina” Gyadamata kai Lujain tayi tana murmushi kaman ba ita tagama kuka ba, a school dinta Baba yafara parking school ne mai kyau ba laifi ga buses awaje an jerasu sabida excursion din daza ayi sauka tayi Baba yakalleta yace “zagayo tanan” zagayowa tayida sauri ta tsaya wajen glass din motar daya sauke yana kallon fuskanta dukta tsure dan tana tsoron Baba sosai, dan jim yayi yana kallonta kaman mai tunanin wani abu saikuma yace “menene bakida shi dakike kuka?” Adan tsorace kaman mai tsoron fadi tace “yooo………ghurt Baba” murya chan kasa still yana kallonta yace “ana saidawa acikin school din naku?” Gyadamai kai tayi ahankali, yace “nawane”? Ahankali tace “500 ne Baba” dubu daya yadauka yabata yace “gashi to kisaya” wani kalan murmushi tayi daya bayyana fararen hakoranta tass irin na yara din nan tace “thank you Baba” murmushi yamata yace “excursion zaku yau ko”? Gyadamai kai tayi tana rikeda 1k din yace “ina”? Hannu tanunamai alamun batasani ba tace “amma ance wajen ceramic ne, zamuje muga yanda ake yin su flower verse, broken plate, bowl, tiles da sauransu” gyadamata kai Baba yayi yace “is a good thing makesure kinyi paying attention and learn everything kinji” gyadamai kai tayi tace “too” juyawa tayi tubur tubur zata wuce Baba yace “Lujain” dasauri tajuyo takalleshi tace “na’am Baba” ahankali yace “be careful okay” gyadamai kai tayi tajuya tawuce saida Baba Yaga shiganta school sannan yasauke ajiyan zuciya yatada motar duk cikin yaranshi yafijin tausayinta bawai sabida ita marainiya bace kadai ba sabida many things, she gets bullied a lot a school, a islamiyya, har agidama, wani zubin yanaso yarabata da Gwaggo but idan yakalla abin deep down badadan Gwaggo ba da yanzu she’s depress Gwaggo nakoya mata komi ba komi bane karta sake tai taking maganan mutane to heart and she should be confident kiba is beauty kuma haka takeyi Koka cemata me kiba da sauransu wani zubin zata iya kuka but give her one

hour ta kakkabe jikinta tayi moving on gashi ko kadan batada riko her heart is as pure as white paper.
EPISODE7️⃣

Jama'a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/

Tana shiga school ana cewa sufito afara shigan bus dan 9:30 zasu bar school yan class nasu yan SS2 akace sufara tafiya bus nasu ita hartama saba batada friend shiga tayi itane sit 1 dan ita tafara biyan kudi tana zama tabude jakanta tadauko ledan biscuit tafaraci yan ajin saikaga wannan yataba wanchan anunata sai akwashe da dariya ko kallonsu batayiba dake bude jakan tayi ta leka wayan Ya Samira tareda dannawa taduba time dan 11 Mandawari zaizo live a IG, murmushi tayi maida jakan tarufe tana cigaba da cin katon biscuit dinta wata Yar class dinsu tamike tsaye a bus din bayan an gama shiryasu an koma wani bus ana shirya wasu yan ajin base on payment tace "Hey Class mate I have a story to tell u tantadaaaaa" duk kallonta akayi wasu yan mata da samari click dinsu sukace "we are listening princess" dariya tayi tace "I want to call some part of the body kugayamin uses dinsu" duk akace okay, tace "the eyes is for whattt?" Yan ajin sukai ihun "seeing" tace "the ears is for what"? Suka kara ihun "hearing" cikeda zolaya from her tone tace "and the mouth is for whatttttttt?" Yan ajin sukai ihu atare "eating" tace "for what" sukace "eatingggggg" Haba sai dariya duk Lujain najinsu hakan bai hanata cigaba da cin abinta ba, komawa princess tayi tazauna tana dariya saiga wata ta tashi da ake cema Lily tace "aga aga" dayake dudda akwai Christian a ajin but duk sunajin hausa universal language sukace "aga" tace "aga chop chop din aji" atare duka suka nuna Lujain sukace "aaaagannntaaaaaa" sai dariya tace "aga mara kawa" suka nunata sukace "aaaaagannnntaaaa" tace "aga mara aboki" sukace "aaaaagannnntaaaa" sanan tai wani ihu irin na final one din nan tace "aga mara boyfriendddddddd" duk aka nuna Lujain akace "aagannnnnnntaaaaa" kwarema Lujain tayi ba kakkautawa dasauri tashiga bude jakanta taduko ruwa da sauri tashiga sha saida tasha sosai sannan click din su princess din sukazo inda take tsabagen son ta kulasu Princess tace "ke miss chubby bakijimu bane Fatty bom bom" wani mugun kallo Lujain tamata batai wata wataba tamike tsaye tareda ajiye jakanta kan sir din dasauri Princess suka koma baya dan sun

zaci dukansu zatayi ko zaunesu cikin kunanrai Lujain tace “Ohhkayyy you want me to say something ko” boldly takalli yan cikin bus din tace “aga aga” Yan makaranta fa akwai son bala’i da fitina, they live for it shine the joy and the fun that comes with being in school da sauri sukace “aga” Lujain tace “aga masu satan amsa during test and exam masuyin chokes olodon aji amman sunfi kowa iya makeup” habawa sai dariya kyakyalya bakaramin kunya princess da Lily sukaji ba, Lujain tanunata da hannu tace “idan kika kara kirana Chubby kowani stupid name saina fasa miki ciki, my name is Lujain but I prefer idan ankirani da LJ, and I am pretty, prettier than this bullies, and I am brilliant cus banayin choke, and I am beautiful I don’t need makeup kuma I have boyfriend a celebrity for that matter” tanunasu habawa sai ihu ajin ana bubbuga kujeru da kasan motan da kafa ana dariya yan class din suka fara matching ana tafi “LJ! LJ!! LJ!!! LJ!!!!” juyawa tayi takoma sit dinta dasauri ta bala’in danne kukan datakeji Gwaggo tasha gayamata kada tasake tayima yan ajinsu kuka idan sun kirata da sunaye dan zasu cigaba saisa bata sake tai kuka and bata taba nunawa wani dan ajinsu she needed them ba tana homework dinta tai karatunta da kanta dan Allah yamata brain.

Teacher dake incharge na class nasu ne tashigo tareda zama akan kujera tace “let’s settle down student remember not to touch without being permitted and not to go anyway da abace muje ba understood” duk suka amsa, juyawa tayi ta kalli Lujain da already ta tara ledojin biscuit uku agabanta tanacin na hudu zatamata magana saikuma kawai tai shiru ta gyara zamanta bus dinsu yafara tafiya.
Bini bini Lujain ke bude jakanta tana duba time awayan Ya Samira ganin har lokacin eleven baiyiba yasa tai murmushi ta juyarda kanta tana kallon hanya, sunyi tafiyan kusan 30min sannan sukakai wani dankareren babban building ita duk zamanta a Abuja bata taba zuwa wajenma bama tasan wajenba to inama take zuwa daga boko sai islamiyya da yamma sai hadda weekend, building na company yayi kyau an rubuta “IMRAN CERAMICS” security gate ne sukai directing nasu to inda zasuyi parking dan musamman aka basu special parking space dan student dole adauki caution saukowa akayi sannan one by one aka fara basu wani sticker dake dauke da rubutun visitor ajiki agaban riguna nan school nasu dake matsayin access card nasu, tanaji wasu yan ajinsu na “wow babban company na wannan, just look at how beautiful visitor’s access card namu” sai alokacin tama kalla dan ana bata mannawa kawai tayi saida teachers dinsu aka kara maimaitamusu yanda zasu behaving da banda tabe tabe sanan akace zasu iya shiga wani ajiyan zuciya tasauke dan surutun yasa bata iya duba wayanta ba kafin teacher sugani a kwace ahankali take tafiya kafin ahankali tasaka kafanta tashiga cikin katon hall don dayake nan reception wani kalan sanyi taji dayasa ta yatsine fuska ahankali tace “AC yay yawa” ihu principal nasu tayi da shigowanta kenan cikin personal car tazo tace “Assemble yourself student” assembly duk sukayi gwanin ban sha’awa murmushi principal din tayi daidai lokacin Hamza yakaraso yana sanye da suit cikeda girmamawa ya gaisa da ita sannan yace “sudan jira kadan CMD na attending ma wasu baki ne” murmushi tamai sannan takalli daliban tace “I am sure all my students here wants to meet the owner, the brain behind this company, this art,  this ceramic work dakenan number one a Nigeria keji dashi, the only ceramic company dake exporting kayayyakin su su plate, verse, mugs, tiles dasauransu zuwa kasan waje,  let’s know little about him and his success story right, what’s the best way to know inda daga

bakinshi ba" student akace yes Ma tace "tom gashinan zuwa" sauke jakanta Lujain tayi tana yatsine fuska kawai anzo an ajiyesu waje daya su haryanzu baa nuna musu komiba ko mene zasuyi damai company oho, danna wayan tayi tacikin jaka ganin 11:05 yasa ahankali tace "Innalillahi na shiga uku" tashi tayi tashiga waige waige ganin teacher su anan baya tsaye yasa tai wajenta dasauri teacher tamata alamu da hannu menene? kaman zatai kuka tace "I want to pee zai zubo" binta da kallo teacher tayi kaman tamaketa tace "Ya za'ayi bazakiji fitsari ba babu kalan abinda bakici ba amota kaman danke kadai akai abubuwan ci aduniya" tai maganan tana cewa follow me binta tayi dasauri zuwa wajen wani security guard tace "excuse me rest room please my student wants to excuse herself" wani waje yanuna musu hakan yasa tace "Oya go" Gyadamata kai tayi ita bama tagane ina ake nunawa ba kawai tawuce abinta da sauri daga malaman har daliban aka bita da kallo wasu na danne dariya ganin yanda hankalin kowa yayi kanta yasa principal tace "attention" duk juyowa sukayi suna kallonta tacigaba da jawabi, ko kadan ita bataga bayin da akacemata ba amman ba wannan ne matsalanta ba waje take nema inda zata labe ta zauna takalli live na Mandawari wani babban corridor data gani yasa tai wajen da saurinta tashiga tafiya harta fita daga corridor taga wani bene da gudu gudu tana haki tashiga hawa benen at the same time tana cire jakanta daga baya duk tana gudu, kaga yanda take tafiya zaka dauka all this kafin agric ne da ake shirin yankawa sunason su gudu, wayan taciro da sauri tana kunna data tana makala earpiece akunne ta sannan tasa hannun tadauko ledan chocolate guda biyu atare tabare ledan ta yarda ledan akasa, jakan batare data rufeba ta sagale a hannunta tana finciko goran fanta da Gwaggo tasamata agefen dan ragaragan aljihun nan na wajen jaka, daidai tana shiga instagram tai logging into her account tana kokarin takai duka chocholate biyu dake hannunta baki ta balla tana kalle kalle ko kadan batasan inda takeba bama tasan tayaya tazo wajenba tadaisan dazu tahau staircase cigaba da sauri tayi ganin duka offices ne awajen kuma duka akulle yasa tacigaba da tafiya zuwa wani corridor data hango daidai tana shiga live din daidai tana yankan kwanan corridor din kawai karo taci da mutum fantan data bude dake hannunta ya kware ajikin mutumin zuwa kasa chocolate din hannunta yawani karye ajikin mutumin yafadi akasa tasan tafadi tasan taci karo da mutum amman still gabaki daya da fuskanta da hankalinta nakan wayan da shi kadaine abinda bai fadi daga hannunta ba sabida yanda tarike gamgam dan shiyafi mata komi mahimmaci ayanzu, ko kallan wanda tabuge batayiba kawai tabi ta gefenshi da bala'in gudu tacigaba da tafiya takara shan wani kwana data gani kawai taga wani kofa abude batai wata wataba tafada ciki ganin bayine ga bayuka kusan biyar kowanne da kofanshi inda take tsaye kuma wajajen wash hand basin ne da mirror yasa da gudunta tayi bayin farkon wajen tana budewa ta sauke marfin masan dakennan karkal ta zauna akai tareda yarda jakanta akasa tawani sauke ijiyan zuciya ta tura kofan dabaigama rufuwa har karshe ba balle tamasaka sakata tana kara tura earpiece din kunnenta da kyau tana kallon wani bakin gaye mai irin askin yan kwalo dinnan da aka kitsa yana sanye da rigan kwallo na magana yana murmushi wani farin hakorin makka na shunning abakinshi wani kalan murmushi tasaki takai wayan ta rungume kirjinta tareda lumshe ido zuciyanta na bugawa tace "I love you Mandawari" na kusan 30sec sannan tacire wayan daga kirjinta tafara replying to live dinshi I love you Mandawari from LJ, My heart beat for you, please check your DM kullum saina maka magana, emojis babu na kalan soyaya dabata dinga turawa ba tana. Cewa please if you see my comments ko sunana ne ka kira a live din nan kana ganin yanda takeyi kasan gabaki dayan brain nata na live din nan.

***
Waiwaye baya kadan….
Daidai taci karo dashi aka bude kofan wani office wani zai fito but ganin Oga tareda wata katuwan yarinya dake sanye da uniform ajikinshi dukansu a tsaye yarinyar na kallon waya kaman abu take nunamai shikuma Oga na kallon fuskanta yasa yakoma cikin office da sauri batare daya gama rufewa ba yana leke, wucewa tayi batare data dauki goran fanta daya fadi da gutsurorin chocolate nataba ta fanfala da uban gudu.

Chak Abee ya tsaya yanabin jikinshi da kallo gabaki dayan suit din dayasa yabaci har zuwa farin rigan ciki dan bai kulle boturin jacket dinba afarin rigan fanta ya zube ga chocolate din some sun manmanne a rigan kaman kashi, sai alokacin ma ya iya juyawa amman hartai kwana sai farin safan kafanta da sandals daya hango azuciyanshi dudda baisan kalan uniform na makarantan dazasu excursion ba but yasan babu any of his employee dazasu dressing like that dan haka that must be a student what on earth student keyi in this floor, kwata kwata nothing yahadasu da this floor dan dazaran yay welcoming nasu factory za'a wuce dasu dake ciki cikin building din suga yanda ake production, jikinshi yakara kallo tayaya zai sauka kasa ahaka yay addressing student, juyawa yayi ahankali cikeda takaici yabude kofan wani office daban ma'aikatan wajen duk suka mike batare daya shigaba yace "call cleaners agoge nan" atare sukace yes sir sannan yawuce yana tafiya anatse zuwa wani special corridor dakenan dawani hadadden office da aka rubuta CMD ajiki murda kofan yayi yaji akulle sai yanzu yama tuna yabar Ibro a office yacemai idan yagama yarufe kofa yakai mishi wasu files mota dan yana gama magana da student fita zaiyi yanada wani meeting dawasu Chinese dasuke son yamusu toiletries, wani mugun tsaki yayi yanzu dole saiyaje General rest room na this floor fitowa yayi yajuya yashiga wani corridor yafara tafiya daidai nan shima wannan employee dayaga lokacin dasukai karo yafito daga office ahankali ganin Oga yay hanyar da yarinyan tayi yasa ahankali yace "Oga yasanta ne"? Saikuma yahau tafiya  da sauri yace "interesting I thought ustazun mutumin nan baison mata so apparently he's deceiving kowa" ahankali Abee yabude kofan bayin yashiga ya tsaya gaban wash hands basin yana kallon kanshi ta madubi dan gajeren tsaki yayi ganin yanda kayanshi suka baci sosai bude tap yayi yatara ruwa a hannunshi ya yarfe hannunshi yakai yana goge chocolate din wani kalan mugun tsaki yayi ganin chocolate din kara spreading ma yake kawai kayan bazasuyi ba dole ya chanza su yasa yaciro wayanshi yakira number Ibro kai tsaye yace "where are you now"? Yadanyi shiru yace "leave the factory ka koma mota ka kawomin office key" yana maganan ya katse waya ji yayi ma he's a bit press hakan yasa yajuya ahankali direct first bayin dake wajen dayaga kofan adan bude yanufa kai tsaye yana tafiyan yana kokarin bude belt din wandonshi daidai lokacin mutumin nan yaturo kofan bayin batare daya shigo ba yakawo wayanshi taciki yana video don baison aji mutum awajen afasa abinda za'ayi saisa yaturo waya yana video ganin Abee na kokarin cire belt yasa yaware idanu yakai hannunshi kan bakinshi aranshi yace "badai yarinyar ke jiranshi anan ba, ai Oga baya using this restroom saina office nashi" kai tsaye Abee yabude bayin tareda shiga ciki atare wani irin ware idanu yayi ganin yarinya zaune akan masan data rufe ga jakanta akasa waya a hannunta tana kallo earpiece akan kunnenta ga chocolate a hannunta tanaci tana murmushi sosai tana kallon waya, alamun kaman da mutum akanta dataji yasa tadago manyan

cat eyes dinta ahankali dan ko kadan bataji shigowanshi ba dan ta taushe kunnenta da earpiece maganganun Mandawari kawai takeji, wani kalan mugun ihu ta kurma tareda zabura ta mike tsaye tana maida kofan tarufe su, takai hannayenta tadaura kan idanunta tace “wayyooo uhmmmmm” tashiga bubbuga kofan da bayanta tana kokarin bude kofan tana kuma kokarin kama bakinta ganin mutum babba kaman aljani akanta.
EPISODE 8️⃣

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Baki gayen dake video yakama daga waje yana kallon yanda kofan ke jijjiga kaman ana wani abu jin muryan yarinyan na nishi, jin mutane na zuwa wajen dasauri yaciro wayanshi daga cikin bayin yawuce abinshi yana maida wayan aljihu yama ma’aikatan dazasu wuce maganan yace “sannun ku” yawuce suka wuce corridor abinsu yalabe wani lungu dan yaga fitowarsu.

Ganin yanda take ihu ta kulle idanunta gam da bakinta gashi takare kofan gabaki dayanta da kibanta balle yama fice abinshi yasa cikeda daka tsawa yace “Ke!” Har cikin kwakwalwanta taji tsawan daya daka mata hakan yasa tarufe bakinta gum sannan tafara bude idanunta kadan kadan ta makale jikin kofan kaman zata manne awajen zuciyanta na bugu ba kakkautawa tasauke idanunta ahankali kan fuskan Abee, ganin yanda tayi kaman tana shirin sakin fitsari yasa yace “open the door kifita” bakinta har rawa yake sosai danta bala’in tsorace tace “ban…….ban…..iy……iyaba” ganin dukta tsorace kawai ta manne kyam akofan yasa anatse yace “step away” gyadamai kai tayi sannan tamatsa ahankali bude kofan yayi fuska adaure batare daya kalli fuskanta ba yace “out” da bala’in sauri tafice daga bayin jakanta da chocholate da wayanta dake kife akasan bayin yakalla hartasa hannu zata bude kofan bayin tafita yasake dakamata tsawa yace “kee!” Juyowa tayi azabure suna hada ido tasauke idanunta kasa jikinta yadauki bari takasa koda daga kafa tai tafiya ball yayi da jakanta daga cikin bayin tareda wayan duka ko ajikinshi dasauri ta tsugunna tadauki jakan tadauki wayan ta jefa cikin jakan ta mike batamasan halin da wayan keciki ba kawai jikinta bari yake fitowa tayi tana waige waige bama tasan ta ina tabiyo tazo wajen ba sai gyara riganta take tafara tafiya tafita daga corridor hanyan

bayin wasu ma'aikata ne su biyu mace da namiji suka ganta sukace “what are you doing here student”? Tsuri tayi bamatasan mezatace ba macen dake kallonta tai dariya tace “hala ta bace ne, come” kaman jira take dasauri tai wajen macen murmushi tamata ganin duk ta tsorace tace “don't be scared kowa da kikagani awajen nan ranan farkon zuwanshi saiya bace acikin company nan, just take that stairs zai kaiki direct kasa though naga Mr Hamza na shirin tafiya daku Factory” Gyadamata kai tayi zata wuce matan tace “what's your name”? Juyowa Lujain tayi takalleta saikuma tanuna kanta ahankali tace “ni”? Gyadamata kai tayi ahankali tace “Lujain” murmushi matan tace “you have a very very beautiful eyes” Gyadamata kai tayi tajuya da sauri sauri tai stairs mutumin yace “kedai Kiyawa kinada son mutane” murmushi tayi tace “she just reminded me of myself danake yarinya haka nataso inada kiba sosai but kasan banbancin mu?” Da sauri ya girgiza mata kai suka cigaba da tafiya tace “she's so beautiful nikuma I was fat and ugly” dariya sukayi yace “common don't say that wlh kinada kyau sosai ke kinganki ne” murmushi tayi tace “yanzu danai girma ne nakuma dakaina nai kyau, amman this girl nada kyau kam sosai Masha Allah kaman ka saceta” murmushi yayi yace “ni duk idanunta sukafi burgeni” dariya dukansu sukayi suka shige office nasu.

Tana kaiwa Anty su tace “ina kikaje? Anje bayi ba'a ganki ba”? Kaman zatai kuka tana haki tace “I got lost dazani bayin sainaje na sama” mugun kallo teacher su tamata ba'a kara cemata komiba suka wuce factory din, sun zagaya factory tass bata taba sanin haka ake kera plate din tangaran dasukecin abinci ba sai yau, aka nuna musu tana daga cikin wayanda ma aka zaba tai practicing tayi plate aka bata kyautanshi daganan suka tafi show room kaman ta kwashe komi takaima Gwaggo takeji sai wajajen 1 sukabar wajen saida taga sun fita sannan hankalinta ya kwanta, abakin layinsu school bus yasauketa.
*****

Tsayawa yayi abayin yabi kasan bayin da kallo yanda chocolate suke akasan wait ma what in the first place takeyi a Gent's restroom?? Dan tsaki yayi daidai Ibro dayasake kira kan yazo bayi direct yakawomai key yashigo ganin Yayanshi dayayi acikin bayi tsaye ga chocolate akasa yana kallo yasa yakarasa gaban bayin da sauri yace “Ipy Yaya Imran” juyowa yayi yakalleshi dasauri Ibro yazaro ido yace “what happen to kayanka Ya Imran”? Hannunshi kawai Abee yasa ya karbe key office nashi dake kan hannun Ibro batare daya amsashi ba yawuce yafita daga bayin yay kofa harya bude batare daya juyoba yace “call Hamza tell him I will not be able to see those school people” yana maganan yawuce office nashi yabude yashiga wani kalan lafiyayyen office ne babban gaske gaban wani daki yaje direct yabude lafiyayyen bedroom ne ciki da gado dakomi bayin dake dakin yashiga wanka yayi da ruwa kai zafi yana fitowa yadauki wani sabon suit ash yasaka sannan yadauki makullin motanshi yawuce yafita.
Stairs yayi daidai mutumin nan yafito daga office girgizakai yayi ganin Abee ya chanza kaya saikuma ahankali yakoma cikin office ya zauna yana jinjina lamarin nan azuciyanshi.

Koda aka sauketa da kafa takarasa gidansu bude gate tayi tashiga Mama ne a tsakar gida da Abida suna gyaran shinkafa duk suka bita da kallo ahankali tace “sannu da aiki Mama” fitowa

Gwaggo tayi daga bangarenta tace “makiran matan nan ina zata amsa gaisuwanki taho diyata tun dazu nake zuwa kofar gida na leka ko kin fara dawowa amman baki dawoba zonan diyar Gwaggo” Gwaggo tabude mata hannu dasauri tana murmushi tawani fada jikin Gwaggo ahankali tace “Gwaggo yunwa” sakinta Gwaggo tayi tace “tuni namiki abinci dakaina dakuma na wanchan Matar ubanki data kawo saida na dandana dan intabbatar ba guba tunda gashi har yanzu ina raye ba guba muje daki” daki suka shiga saikuma tafito ta kalli Abida tace “kin fasa shan furan dakikacemin zakisha ne tijararriya”? Dasauri Abida ta tashi Mama ta tabe baki batace komiba dan yasan dazaran tace wani abu Gwaggo zata hada karya da gaskiya yau yau din nan ta tara yaranta kaf takai karanta.

Tana shiga dakin taga Lujain zaune akasa ko takalmin makaranta bata cireba Gwaggo tacika mata abinci agaba kusan kala takwas, Mama dama fried rice tayi da salad da chicked, Gwaggo takara soyamata wani Kazan daban cikin kula, ta dafamata kwai guda hudu, sai katon flask din tea, ga buredi saikuma taliya ga fanta da coke gakuma fura datake rabawa bama Abida tayi cikin kofi tace “ungo” karba tayi tana kallon cikin kazan dake cikin kula gaban Laujain data faracin abincin ga Kazan Gwaggo badai dadi da zaki ba tanajin kafizabo ahankali tace “Gwaggo nima kaza” dan zaro idanu Gwaggo tayi takalli Lujain data batarai Gwaggo tace “fisabilillahi Abida ni dai bansan kokin maida Lulu kishiyarki bane amman tsakani ga Allah kemafa dazu kin shigo nabaki Kazan nan sannan kinci na wajen uwarki yanzu na jikata ne baraki bari taci ba” turo baki Abida tayi tace “ai nima jikankice” ihu Gwaggo tayi tace “daman nace ke ba jikata bace ni Safara’u amman ai wannan bata da uwa keko ga uwarki chan awaje tana aiki sai shegen bakin zuciya” daure fuska Abida tayi tamike zata fita Lujain tadauki katon cinya tace “uhm” juyowa Abida tayi ganin Lujain nabata tazo ta amsa tajuya bako godiya Gwaggo tace “kobaki gode ba Allah dai yabata lada kinga banbancin rainona da rainon uwarki ko, diyata akwai kirki da farar zuciya kuko zukatanku uwa an shafa bakin fenti irin na gyatumarku” daidai nan Lujain ta tashi tana gaytsa ahankali Gwaggo takalli abincin dudda bata cinye komi ba amman tarage sosai tawuce tashiga bedroom nasu kayan makarantan tacire tashiga bayi wanka tayi tafito daure da towel tasa hijabi tai salla sannan tafito falo ganin bataga Gwaggo ba yasa tadauko jakanta taciro wayan Ya Samira ta kunna wayan batai komiba amman screen din ya tsage faduwa gabanta yayi ahankali ta tashi tana rike da wayan tafito da towel din nan tawuce side dinsu bataga Mama awaje ba hakan yasa yasan tana kitchen dakinsu Ya Samira tashiga tana zuwa ta ijiye mata wayan akan kayanta sannan tafito tadawo daki Gwagho da fitowa ta daga nan daki kenan tace “barakizo kihuta ba kinsan anjima kadan zaku islamiya ko
EPISODE 9️⃣

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/

Bayan one week!
Yau Saturday kasancewa jiya Zainab ta tafi dan mijinta yadawo yasa jama'an gidan suka ragu, kowa na gidan nanan Abdallah ne kawai bayanan danshi both asabar da lahadi duka yanada lectures.
Zaune yake a falo yana sanye da jallabiya fara mai kyau hannunshi rikeda wani cup na shayi mai kyau yana kallon Hajiya da Mustapa dawani abokinshi Haruna shima soja ne yau kuma yashigo Abuja sai hira suke da Hajiya suna dariya shi iyakanshi yay murmushi aka tambayeshi eh ko a'a idan dasabo harsun saba da halin nan nashi, idan baka sansu bama zaka dauka shine bako su Musty sune yaran Hajiya, shayin yakai bakinshi ya kurma daidai wayanshi kiran IPhone 14 pro max dake aljihun gaban farin jallabiyan shi na kara ahankali ya ijiye mug din kan coffee table dake gabanshi yaciro wayan ganin messege ne from an unknown number yasa gently yabude.
“You have 24hrs to pay sum of 100 million in cash dakuma papers na company na Imran ceramic inba hakaba we will release your sex tape ma duniya, in 24hrs time zamuyi contacting naka ta hanyar fadamaka inda zakakai komi ka ijiye”.
Abee kyar ya tsaida idanunshi kan messege din daya karanta kusan sau hudu. “Hey hey Imran!” Firgigit dayago kanshi ganin Mustafa akanshi da Haruna sai Hajiya duk suna kallonshi, ganin idanunshi yasa Mustapa yace “lafiya dai ko me kake dubawa haka”? Mustapa yay maganan yana kokarin karanta abinda ke screen nashi da sauri yay locking wayan yana mikewa tsaye yace “time for asir ko let's go” atare dukansu suka fice suna hira Haruna yakalli wani babban gym dayaga ana fito da tsofaffin kayan workout din ciki ana saka sabo yace “anya kuwa Musty komu sojoji zamu nunama Imran training kuwa”? Dasauri Mustafa yace “inafa bakaga saisa baya tsufa ba look at him please kaman Yayan Abdallah” wani mugun kallo Abee yamai yace “kadaina maidani yaro I don't appreciate that” Musty shima mugun kallo yamai yace “kayi zuciya kai tsufa to” daidai sun kawo masallaci.
Har suka idar da salla sex tape na ranshi to kodai bashi za'a turama sakon ba sukai mistake amman kuma sun kira sunan company shi, gida suka koma daidai an gama lafiyayyen tuwon shinkafa da miyan kubewa da kifi yana zaune akan kujera wayanshi yakara kara ahankali yabude wayan video yaga an turamai babu wani rubutu tareda video, 5 secs video ne hakan yasa yabude tareda maida karan to mute shiya gani a video abayi yana tafiya yana kokarin kwance belt zaije bayin nan just 5secs yakare shiru yayi bayan video yakare he don't really know what to think wannan ranan dahar yay using that general restroom was ranan da yan makarantan nan sukazo to where is the sex yan second dayayi abayin nan ne sex? waye a company shi yamai wannan video? Blocking number yayi sannan yay deleting message din gabadaya dan baiga amfanin abin ba though abin ya tsayamai arai dan shi yasan baiyi wani abu mara kyau ba.

“Are you eating ko mu cinye mubarka”? Musty yay maganan yana kallon Abee, Hajiya tace “ahap wannan aishi da abinci makiya ne baci zaiba kuci abunku ku manta dashi” mikewa yayi dagakan kujera yace “kuci I will eat later ina zuwa” yana maganan yay stairs duk suka bishi da kallo, dakinshi yawuce zama yayi akan gado yay shiru sai chan yay dialing number chief head of security na company shi ringing daya yadauka yace “Sir” anatse yace “Mr James I need you to email me the CCTV footage of on 23rd right away” cikeda girmamawa yace “yes sir” tashi yayi yawuce wajen desktop nashi ya zauna tareda kunna desktop din ya bude email nashi daidai video yashigo budewa yayi sunada yawa danna kowani department daban department da office nashi yake yabude yay fast forwarding zuwa daidai lokacin dayaje bayi saikuma yadawo baya daga lokacin daya fito daga office nashi yana waya har zuwa yazo corridor nan saiga yarinyar tazo da gudu ta bangaje shi alokacin yaga wani ma’aikacin shi da bazai ma iya tuna sunanshi ba but yasan yana cikin Human Resources team nashi, zama yayi yana kallon komi harzuwa sanda mutumin yaje wajen bayi a corridor bayi akwai cctv but babu acikin bayi daidai inda mutumin yafito da wayanshi yasa acikin bayi yay lumshe idanunshi yayi yay shiru meyama yaron nan da yakeso yabatamai suna daidai nan aka turo kofan dakinshi aka shigo dasauri ya kashe desktop din ganin Mustapha da Haruna, Musty dake kallonshi trying to read something from his face yace “are you okay kuwa Imran” key dinshi na mota dake kan desk din yadauka yace “I need to go to office now something came up” ta gefensu yabi yafice yabarsu nan tsaye Haruna yace “what is this saying ma?….Hali zanen dutse ko” tabe baki Musty yayi yace “ai murdadden halin Imran bazai taba chanzawaba tun yana yaro” zama sukayi, Haruna yace “Musty yafijin maganan ka wai har yanzu bazai aureba Kodai yanada matsala ne irin I mean medical one din nan” dan dariya Musty yayi yace “lafiyanshi kalau wlh” Haruna yace “to tayaya yay surviving 13yrs ba mata ni gashi yanzu inada mata biyu na uku ma nake neman yi yanzu dan sunmin kadan, nakasa gane yaya yake surviving” tabe baki Musty yayi yace “ohon mishi idan yazo katambaye shi, ni tashi muje mu buga ball jikina yamin nauyi sabida yan kwana biyun nan damukai ban motsa jiki ba” Haruna yace “yaushe za’a gama aikin gidan naku ne kadau matanka kutafi” murmushi yayi yace “cikin this week yau suke fenti ma dazu nida Imran munje gidan” suna hira suka fice daga gidan bayan sun gayama Hajiya zasu dawo suyi dinner tace to su kawo mata inibi.

Zama yayi acikin office nashi bayan yaciro file din Human Recourse team nashi kowanne ga sunanshi da passport da information nashi awajen akan yaron ya tsaya sunanshi Abdulganiyu Olaniyi Asiwaju Razak bayerabe ne from Osun state aikin nan ne yadawo dashi Abuja this is his second year a company shi, shiru yayi yana kallon hoton yaron, saikuma ahankali yashiga daukan number shi yay dialing yaji akashe ajiyan zuciya yasauke ya maida paper ya ijiye yay shiru kana ganinshi kasan tunani yake yana nan cikin office shi kadai har magrib jin ana kiran salla yasa yatashi yakulle office yafito tareda masu gadinshi sukai salla yajasu jam’i suna idarwa kyautan kudi yamusu har mota suka rakashi suna godiya yawuce yatafi tsayawa yayi wajen masu saida fruits siyan dayawa yayi aka samai a boot harzai wuce saiga mai saida ribbon Muna yatuna batada wani gashi but yanason ribbon most time yakan tsokaneta da aukin siyan ribbon amman babu gashin dazata kama dashi kiran mai ribbon din yayi yace “kawo” dasauri mutumin yazo kafinma mutumin yay magana Abee yace “nawane duka”? Washe baki yayi yace “duka

nan kayan 4,500 ne" 5k yaciro ya kirga yabashi godiya mutumin yashiga yi yaciro komi yahada yabashi karba yayi yaja motanshi yawuce.

Saida yafara tsayawa yay isha'i a masallacin anguwansu sannan yafito yawuce gida bayan ya dauki su Hamza da Abdallah daya gani amadallacin yana parking ribbon din kadai yadauka yaba Hamza key yace "ku kwashe fruits kukai ciki" yawuce babu kowa a falo hakan yasa yawuce sama ahankali yay sallama tareda bude kofan dakin Kausar tana zaune sanye da dogon rigan atampan ta mai kyau rubutu takeyi tadage ganin Abee yasa ta yarda biron ta tashi da sauri tace "Abee dana dawo daga kitso bakanan" tai maganan tana tafiya wajenshi dan yana tsaye gaban dakin, ganin yana kallon kitson da aka mata yasa tawashe baki tace "kitson yay kyau Abee" gyadamata kai yayi yace "sosai" ledan hannunshi yabata dasauri ta karba tace "meka siyamin Abee" ganin ribbons dayawa daban daban wani kalan ihu tayi ta rungumeshi tana tsalle tace "Abee thank you" dan murmushi yayi yace "saken kije kicigaba da assignment dinki, kinci abinci"? Gyadamai kai tayi tana kallon ribbons dinta hankalinta yay nisa awajen, fita yayi daga dakin zuwa nashi.

Wanka yayi shayi kawai Hajiya ta aikamai dan tasan yanda dare tayi bazaici abinci ba, zama yayi yanashan shayin yana tunani na farko babu anything like sex dayayi so wanan ma is off list, nabiyu this so called guy dake blackmailing nashi employee nashi ne and when something happen that has to do with employee naka you need to handle it with lots of precaution, he will try his number again tommorow yaga how things goes.

Washegari yay dialing number still akashe ganin har yamma still babu komi yasa ya tattara komi ya watsar dan in the first place yasan babu wani sex video ballema har ayi leaking nashi a online.

Yau monday as usual bayan breakfast kowa yakama gabanshi Abdallah tareda Kausar suka tafi school dan lecturer su nasafe yace baida lpy bazai zoba, Hamza ya sauke yara yawuce shima Abee yashirya cikin wani Italian suit black dayamai kyau bana wasaba hannunshi daure da rolex,  yana kaiwa company abinda yafarayi was yashiga office na HR amman seat na guy din empty bai zuwa wucewa office nashi yayi dan yanada ayyuka dayawa dazaiyi.

Wuraren 10 aka fita break kowa na ajinsu SS2A yafita banda ita dake zaune tafito da duka abubuwan da Gwaggo tazuba mata a jaka tanaci one by one, tana cikin cin egg and chips princess tashigo class din da ita da Lily dawasu maza guda biyu rike da goran drinks a hannunsu kallo daya tamusu tadauke kai ganin sun dumfarota tacigaba da cin abincinta gabanta na faduwa ganinsu su kusan shidda amman bata nunaba Princess na karasowa

gabanta batai wata wata ba duka kayayyakin abincinta tawani barar dasu dayasa Lujain tamike tsaye dasauri tana kallon Princess da some much anger tace “mehaka princess”? Wani mugun kallo princess tamata tanuna kanta tace “kinganni Miss Chubby, kinga Lily we can proudly say eh munji muna chokes dasauran su but I can assure you this muba yan iska bane, our vaginity is intact unlike you dakin saba har kin iya moan” wani kallan kallo Lujain tamusu tace “me akace miki nayi I don’t understand ni kike kira da yar iska”? Wani murmushi princess tayi Lily ta tofar da miyau agefe tace “you disgust me Lujain you look so innocent babu wanda zai miki kallon karuwa sabida yanda kika kware a pretending” Lujain zatai magana Princess tace “kola play the video for her” dasauri Lujain takalli Kola dake danna wayanshi yana chewing cingum abaki kaman dan daudu saiga muryan Lujain tace “wayyooooo, Hmmm, Hmmm, hmmmm” hmmm hmmm din was repeating babu kakkautawa da karan buga kofa babu wani baligi mai hankali da zaiji da bazaice Iskanci akeba, Kola da abokinshi sukahau dariya Kola yace “Ashedai Fatty bombom tasan dadi kizo muyi dake I promise zan saya miki 5 shawarma da chocolates goma expensive ones ba irin na yan 500 din nan da kike zuwa dashi school ba” dukansu sukahau dariya princess tace “karuwa kawai mai gindin roba” baki Lujain tabude zatai magana kawai taji saukan drinks masu sanyi ana tsiyaya mata akai har zuwa jikinta princess tace “bari mu miki wankan tsarki da drinks” daidai nan Principal tashigo class din dakusan all the school teachers biyeda ita abaya.

EPISODE 🔟

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Zaro idanu Principal tayi ganin yanda suka watsa mata drinks sun mata wanka sun bata mata jiki gabaki daya tace “what in God’s name is this Kola and co?” Da sauri duk suka wurgad da gorunan kasa, Principal tace “to disciplinary office now!” dasauri suka fita sannan takalli Lujain wani irin kallo da Lujain takasa fassarawa koname tace “come with me” ahankali ta tsugunna ta dauki jakanta dake tsiyaya da drink ta kakkabe jikinta tabi bayan principal faran safan kafanta har tusan ruwa yake sabida yanda drinks suka jikashi teachers nasu na kallonta wani kalan kallo tawucesu ahankali suka rufamata baya suna fitowa taga student an taruuuu kawai kallonta akeyi kaman yau aka fara ganinta a school din aka wuce da ita saikuma chan taji student na

murmuring “God forbid, ewwww wasu na cewa na karuwa”  har zuwa office na principal suka shiga principal ta zauna akan wani kujera tanuna mata wani waje teachers kuma suka fita, anatse principal din na kallonta tace “a ina kikasan Alhaji Imran”? Zaro idanu tayi tace “na’am waye Alhaji Imran”? Dan to be honest bamata gane kan maganan ba, ahankali Principal tace “mai company ceramic, at first da aka fara fadamini awaya I thought maybe forcing naki yayi he took advantage of you but after watching the video…….” Principal tai shiru daga gani kasan maganan namata nauyi tace “after watching the video I understood komi yafaru ne with your consent dan is so obvious, ni baran wani iya cewa komiba dan you have your rights as an adult data wuce 18yrs you are 19, keba minor bace, all I will say is have this” tamika mata wani takarda ahankali Lujain tasa hannu takarba ganin letter na susupension yasa dasauri takalli principal din, Principal tace “I believe guardians naki are on their way right now tun dazu muka kirasu wata tsohuwa da farko damuka kira mukaji, hakan yasa muka dauki second number wanda yacemana shine mahaifinki yana hanya” shiru Lujain tayi kawai tana kallon letter ita she don’t even know what’s happening.

Suna parking Gwaggo data gama rudewa tace “Ya ubangijji kasa ba ciwon yarinyar nan bane yatashi ba Wanan damai makarantan takirani gabaki daya” fitowa Baba yayi tareda Mama dasukai gaba daidai lokacin wayan Baba yahau ringing anatse yace “eh muna makarantan yanzu, tom saikun karaso” dasauri Gwaggo tace “waye?” Ahankali yace “Abdulhadi da Yusufa ne” fashewa da kuka Gwaggo tayi tace “kafadamin gaskiya kodai Lujain dina tamutu ne wanan dahar ka kira kannenka suzo nan iyye kafadamin gaskiya” ja idanun Baba sukayi  yakalli Mama yace “kujirani anan bari na shiga” Gwaggo na kuka sosai tace “wlh kafanka kafana kaida matanka damai makarantan kunki fadamin abinda ke faruwa saikuma kuhanani shiga wlh saina shiga” dan jim Baba yayi yana kallonta saikuma yace “muje” dasauri Gwaggo tabishi tana goge hawayenta da bakin zaninta data warware har zuwa principal office suka shiga, ganin Lujain zaune nata kallon takardan da aka bata yasa ta taho dagudu tana shafa fuskanta tana bude mata idanu tabude bakinta tana kallon da duba harshenta danta gane ko rashin lafiya take tace “Alhamdulillah babu abinda yasameki yarnan Iyyee Alhamdulillah wayyo Allah zuciyata kubani ruwa Insha” dasauri principal tabata ruwan gora budewa Gwaggo tayi ta kwankwade tass sannan ta zauna Baba batare daya kalli Lujain ba yace “gamu principal” ahankali tace “ba babanki takardan Lujain” ahankali Lujain tamikama Baba takardan fuskanta yakalla da jikinta daya baci da drinks da jakanta dahar lokacin na diddigan ruwa sannan yasa hannunshi ya amsa ya karanta yakalli principal din harzaiyi magana saikuma yatashi tareda kama hannun Lujain yace “muje” tashi principal din tayi tace “kuyakuri sir bazan iya barin yarinyar ku tacigaba da karatu anan makarantan nan ba she is a bad influence zata batamini sauran dalibai kuya kuri babu abinda zan iya” sai alokacin Baba yakalleta yace “akwai abubuwa da yawa da zaki iya na farko shine kare hakkinta jibi yanda akama y’ata wanka da drinks sabida kunga batada kani ko Yaya amakaranta kobaki koreta bama nixan cireta daga makarantan, inaso kisan abu daya, akwai Allah! Sannan zai wanke mini diyata agaban kowa muna nan zakusan you all have wronged her” yaja hannun Lujain dasauri suka fita tashi Gwaggo tayi tana kallon Mama tace “ke Maman su Samira me akace tayi ne kifadamin” chak Mama ta tsaya kaman jira take tace “yarinyan dakike mana tunkaho da ita kina fifitata kan nawa yaran video dinta dawani kato

dasukaje excursion akafaninshi na yawo a yanar gizo suna fasikanci sun shiga bayi yana dugurguzanta diyarki na ihun dadi" wani kalan zaro idanu Gwaggo tayi tace "mene shairin kine dai ko" wayanta Mama taciro anan office an principal takunnama Gwaggo video tundaga lokaci da Abee ke kokarin kwance belt har zuwa lokacin daya shiga bayi ga muryan Lujain nan dako amarfi tasani tai ihu wayyooo saikuma uhmmm Uhmm uhmmm saikuma chan aka nuno Laujain tafito corridor tana gyara riganta tajuya dasauri ta tafi tunda Gwaggo take bata tabajin tashin hankali hakaba baya tayi zata sume dasauri Mama ta tarota tace "ni kada ki sumemin yace dagangan na nuna miki inason kashemai uwa mutafi" takama hannun Gwaggo tanaja suka fita awaje taga duka yaranta da Yusuf da Abdulhadi dukansu suna sanye da manyan kaya sai Yayanta sunyi jugum suna kallon Lujain da idanunta sunyi ja ganin Gwaggo tafito anriketa yasa tai wajen Gwaggo da sauri saiga hawaye, zaunawa Gwaggo tayi akasa tana zaunar da Lujain bata damu da yan makaranta ba tanuna kanta tace "Lulu tun kina cikin kwalban asibiti nake rainanki nasanki ciki da bai nasan halinki tsaf amman bansan ki da Iskanci ba kifadamin gaskiya meyamiki kike ihu" zaro idanu tayi dukta rude tace "waye? Wani ihu Gwaggo"? Wani kalan fizgota Baba yayi cikin ihu kaman zai mareta yace "ranan dakukaje excursion me mutumin nan yamiki abayi kike ihu"? Jikinta har rawa yake ganin Baba na shirin dukanta tafashe da kuka tace "wlh babu komi Baba" Baba Abdulhadi yace "to ubanme aka miki kike ihu"? Cikin kuka sosai tace "Baffa wlh naje bayi na kalli video wan nan dan kwallon Mandawari ne awaya" kusan dukansu atare sukace "a ina kika sami waya"? Cikin kuka sosai tace "wajen Ya Samira na ara bayan nabiyata da kudin asusu na" Baba yace "saime yafaru"? Cikin kuka sosai tace "ina zaune kan masai nasa earpiece a kunne kawai naga mutum yashigo yana kokarin cire wando" dukansu sukace "Meya miki kike ihu" jikinta har bari yake tana haki tace "wlh babu abinda yamin tsoro naji nadauka aljani ne saisa nadinga ihu na manne jikin kofa shine yamin ihu yace nafita nace ban iya bude kofaba shine yace na matsa yabudemin na fice yay min ball da jaka da wayan Ya Samira harta fashe na kawasa na tafi shikenan" kaman jira Mama take tace "wlh wlh karya kike ke yanzu ki kalli tsabaragen idanun Babanki da Baffan ki kina karya, kifadi gaskiya tun yaushe kika fara iskanci eh? Daman naga gabobin jikinki sai kara habbaka suke waya koyamiki? Wayake matseki? A ina kika sanshi dahar kuka hadu abayi yaushe kika dawo Yar iska mayyan maza Lujain"? Wani kalan fashewa da kuka sosai Lujain tayi tama kasa magana sabida yanda kukan yafi karfinta jin maganganun Mama,  tashi Gwaggo tayi tana kakkabe jikinta takalli Baba tace "ku kaini kampanin yanzun nan" kallonta sukayi duka cikeda bala'i tace "ku kaini kampanin nan Kona tare abin hawa nakai kaina, koya mata wani abu kobai mataba bai isa tasanadin shi a batamin sunan diya ba a yanar gizo duniya tagama ganinta, wlh wlh yau sai anyita an kare" Baffa Abdulhadi yakalli Baba yace "Baba dole dama muje muganshi idan ma za'a kai kara hukuma ne asan nayi kumuje" Ahankali Baba yabude motarshi suna suka bude tasu aka shiga har akakai company nan kuka Lujain takeyi sai yanzu tagane abinda yasa su Princess suka kirata har karuwa dudda bata kallo video ba suna kaiwa company reporters dasuka gani agaban kampanin sunfi hamsin saukowa akayi Gwaggo takama hannunta suka wuce ciki ganin ana musu hoto mayafin jikinta tayaye tayafama Lujain dake kuka tarike hannunta sukai wajen shiga taresu security yayi Gwaggo da idanunta sukai jajir tace "na rantse maka da ubangiji zan tube nai dambe dakai awajen nan kace bazamu shiga ba, dan ubanka Mudi da Uwarka Safara'u idan akai kokarin batama jikanka suna bazakayi abinda yafi haka ba budemin kofa kona fasa" girgiza mata kai yayi yace "Mama Oga yace ba shiga ba fita bakiga

yan jarida sun cika nan ba” cikin ihu Gwaggo tace “yo ina ruwana shi yasan Meyayi ai” jin yanda Gwaggo ke ihu Hamza da idanunshi sukai jajir yazo wajen daga ciki ganin student din makarantan nan da aka lullube da mayafi tana kuka sosai from yanda jikinta ke bari ga wayanda ke tareda ita dazai iya cewa iyayenta ne yasa ahankali yace “kushigo” bude musu kofa akayi Gwaggo taja hannun Lujain suka shiga ciki, waje yanuna musu awajen yace “ku zauna bari naje na sanar” cikin ihu Gwaggo da idanubta sun juya tace “nabaka minti biyu” stairs yayi karo yaci da Ibro da shima idanunshi sunyi jajir yana kallon su Gwaggo da yarinyan dake sanye da uniform da aka lullube da gyale ahankali Hamza yace “I think is the girls family ka kira Uncle Musty” gyadamai kai yayi yace “yama iso he’s trying to come inside” daidai lokacin wayanshi yahau ringing dasauri Hamza yace “Hajiya ko” gyadamai kai yayi ahankali, hawaye ne yakawo idanun Hamza dan he’s a very soft person yace “kana tunanin tasani” gyadamai kai yayi yace “kaima kasan that’s the only answer to yanda taketa kiranmu tun dazu clean those tears if our workers saw that kanason suyi tunanin Ya Imran zai iya aikata abin ne” girgixamai kai tayi daidai lokacin Musty na sanye da kayan sojoji da Haruna dakuma wani babban abokinsu police man su uku suka taho ganinsu yasa Musty yace “calm down you all Ya Imran din”? Ahankali Ibro yace “yana office working as if nothing is happening amman nasan deep down he’s hurting bama wanan ba Uncle Musty I believe the girl’s parent are here gasuchan” yanunasu ahankali Uncle yace “Innalillahi wa innailaihi raji’un! Allahumma ajirni fi musibati” yakalli hannu da police man yace “kuje ku kutaho dasu lemme see him” yana maganan yawuce sama su Hamza suka bishi ahankali yabude kofan office din Abee, kallo daya Abee yamai yacigaba da aikin dayakeyi bazaka iya gane takamaiman reaction dake kan fuskanshi ba karasawa gaban table din Musty yayi ahankali yace “the girl’s parents are here” chack ya tsayar da typing din dayakeyi batare daya kalli Musty ba, anatse  Musty yace “nace su Harun su taho dasu nan we need to speak to them and show them, but maisa baka fadamin komi ba eh Imran” dago idanunshi Abee yayi yama Musty wani kallo yace “me kake so nagaya maka takamaimai nace maka wani anonymous number sent me a text demanding 100M and this company’s document koyay releasing video tarayyana da wata da I know nothing about!”?

Knocking kofan akayi kallon Abee Mustafa yayi yace “gasunan” sanan yajuya yace “bude musu kofa Hamza” juyawa Hamza yayi ahankali yabude kofan Haruna da Police nan mai suna Abdul ne suka shigo sai Gwaggo data rike hannun Lujain gam dake lullube suka shigo tana hura hanci sai Baba dasu Baffa da Yayan Lujain sai Mama wuri harun yanuna musu kan dogon setin kujerun office din zazzamansukayi Gwaggo ta zaunar da Lujain da sheshekan kukanta kawai ketashi acikin office din itakuma Gwaggo tabi kowa na office din da kallo tace “nifa ba zama takawoni ba waye mutum dayaja sunan diyata yabaci aduniya ina mai kampanin?” Ahankali Abee da kanshi ke kasa yadago kanshi gently yazubama Gwaggo idanunshi da hakanan kawai taji magana ya makale abakinta.

💫 SAKON SO 💫

M SHAKUR ✍🏻

Abu daya zan fadamuku gareku masucin hakki na, da masu daukan book dina suna sawa a site dinsu, damasu sawa a YouTube, da dukma wata ko wani mai amfani da book dina yana kudi without consulting me wlh wlh ban yafeba kuma bazaku taba ganin cigaba ba dan hakkin wani kukeci, kome zakuyi da rubutu na contact me first! 07012181461

Jama'a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuna kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da Episode biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

EPISODE1️⃣
~Masjid Ibn Taymiyah~
Aka rubuta ajikin babban masallacin dake cike makil da jama'a kowa yaci manyan kaya manyan shaddoji da kanagani kasan daurin aure ake shirinyi, wani matashin saurayine ke sanye da manyan kaya dakuma babban Riga na shadda datasha aiki yana tsaye daga ta wajen masallacin yana kallon agogon hannunshi da alamu lokaci yake dubawa chan kuma yadago kanshi yana leken kan titin da masallacin ke kai, tabashi akayi daga baya dayasa dasauri ya waigo wani matashin saurayine yatabashi shima yana sanye da manyan kaya yasha hula kube, cikeda damuwa yace "he's 20minutes late Arif kazo mutafi koda na'ibin limamum masallacin nanne ya karba maka Auren, duk an taru mutum daya ake jira haba mana is not cool" girgizamai kai wanda aka kirada Arif yayi yace "I know he will come let's just give him some time, Uncle Hamma is just….." dasauri abokin yace "sociopath" wani mugun kallo Arif yamai zaiyi magana daidai wata Babban jeep na parking abangaren masallacin dayadan sami space na parking, wani kalan walwala ne ya bayyana akan fuskan Arif baisan lokacin dayabar abokin nashi yafice daga cikin premises na masallacin dasauri ba dudda jama'a na kwalamai kira ta ko'ina suna ango ango baibi takansu ba yay wajen motan dayake nan bamaka ganin kowa na ciki sabida tinted glass ne duka kuma arufe, ahankali yasa hannunshi batare daya jiraba yabude gaban motan bangaren mazaunin direba tareda tsugunnawa har kasa cikeda girmamawa batare dayama kalli fuskan mutumin dake cikin motanba yace "barka da zuwa Uncle Imran" wani magidancin mutum ne zaune cikin motan da akalla zaiyi 48/49yrs yana sanye dawani soft milk yadi daya haska bakar fatanshi dake bala'in sheki tsabagen hutu.

Yanada cikan gashin gemu sosai gasunan baki sidik masu tsayi kadan dawasu sirarren saje dakenan a kwance suma lublub, ga cikan gashin gira dakuma suman kai dudda lafiyayyan hulan minister na kanshi hakan bazaisa kagane cewa yanada cikan sumaba, yanada wasu kalan kananun yet manyan idanu idan ya zubamaka su idanba ka natsu ka kalleshi ba zaka dauka idanun nashi a lumshe suke amman abude suke ras kwayan idanun farare fat, hancinshi dogone sosai kuma siriri sai lips dinshi dakenan jazur, kallo daya yama Arif dake tsugunne kanshi akasa babu wani murmushi ko fara'a akan fuskanshi sannan kuma babu wani bacinrai ko wani yanayi akan fuskanshi saima fuskanshi dake nan adake dake lullube dawani kalan warm rahama akai, kaman baiso yay magana yace "Arif" wani kalan murmushi Arif din yasaki cike da mugun girmamawa yace "na'am Uncle Imran" tareda dago kanshi yadan kalleshi saikuma yasake sauke kan nashi kasa dasauri baitaba ganin mutumin dake tattare dawani kalan mugun kwarjini dakuma haiba irin na Uncle Imran ba, duk yanda kakai ga bushewar idanunka baka iya kallon tsabaragen idanun Uncle Imran kamai, Ahankali kaman baiso yay magana cikeda wannan natsuwan yace "get up kayanka will get dirty" tashi Arif yayi babu gardama still kanshi na kasa hakan yasa anatse ya sauko daga cikin motan yafito ya tsaya kusada Arif duk tsayin Arif akafadar Uncle Imran yake dan Uncle Imran giant ne sosai, dudda babba ne shi ya manyanta amman jikinshi da gabobinshi gabaki daya atsaye suke tsaf kana ganinshi kaga wanda yake gyara jikinshi ta hanyar cin lafiyayen abinci dakuma excercise, yana sanye da babban riga dake kyalli da wandonshi daya tsayamai a daidai idanun sahu, kafanshi na sanye da ankle sock dake cikin wani givency covershoe dake sheki sosai, juyawa yayi yadauko wani bakin glasses dan idanunshi basason haske sosai yasaka sannan yakalli Arif dakanshi ke kasa yace "muje ko"? Gyadamaikai Arif yayi yace "to bismillan mu Uncle" yay maganan suna jerawa tunda yake baitabajin mutum dake kamshin turare kwatankwacin irin turaren Uncle Imran ba, turaren Uncle Imran nada bala'in dadi gasu da sanyaya rai, tun kafin su karasa cikin masallacin mawaka da maroka kemai wake wanda ko kadan bayaso hakan yasa baice musu komiba koyabasu kudi ba yawuce suka shiga masallacin nan da nan abokin Arif yace "waliyin Arif ya iso" karasawa sukayi cikin aka zazzauna nan da nan aka daura aure tsakanin Arif da Salma akan sadaki 500k wanda Uncle Imran yabiya mishi akai addu'a ana gamawa ko sec daya tal bai karaba yamike yajuya Arif yatashi dasauri yabishi abaya, abokin Arif yataba wani abokinsu da duk sukabi Arif da Uncle Imran din dasuka fice daga masallacin da kallo yace "dan Allah jibi Arif saikace yaga God" dayan abokin mai suna Muhammad yace "to ai kusan hakane wannan Uncle din nashi shiyamai komi aduniya tundaga primary school konine abinda yafi hakama zanmai wlh Aliyu tunda mahaifinshi ya gudu yabarsu bai kuladasu ba" tabe baki wanda aka kirada Aliyun yayi yace "bakasan waye mutumin nan ba idan kasan irin kalan bakin girmankan dayake dashi saikai mamaki bakaga yanda babu wanda yagaida a masallacin nan ba sai uban dingile wando shi adole ustazu da ijiye gemu" wani kallo Muhammad kema Aliyu yace "waikai Ali me mutumin nan yamaka ne danni wlh banga aibunshi ko daya ba"? Mugun kallo Arif yama Muhammad yace "bazaka gane bane waini mutumin nan zai hana aiki sabida wai inashan taba yay rejecting application dina a company shi, shi wayasan kalan abubuwan dayayi lokacin dayake matashi yana soja kafin yay retire"? Kalan kallon da Muhammad kemai yasa yace "me to ai gaskiya nafadi ni to even tell you the truth gwara dabai

daukeni ba dan ance mahaukaci ne tuburan tuburan saidai in alluran sojojinshi basu tashi ba wlh bakaga saisa har yanzu babu wacce ta yarda ta aureshi ba sai tsufa yake agidan tsohuwarshi" wani mugun harara Muhammad yamai yace "kainedai kaga tsufan dan ni bangani ba wlh ko mahaifin Arif daya girma yafishi tsufa, haushin shi kawai kakeji sabida yahanaka aiki dayayi, kuma aure dabaiyiba shine baiyi niyya ba tunda akazo har gida aka kashemai mata da yara biyu" dasauri kaman jira Aliyu yake yace "kasan shekara nawa yanzu da mutuwansu? This is the 13th year amman har yanzu bai kara aure ba, wlh basabida mutuwan matanshi bane ba, matsalan haukanshi yasa babu wacce ta yarda ta aureshi" zai cigaba da magana ganin Arif na tahowa wajensu yasa yay shiru yamike tsaye yana kakkabe rigan jikinshi.
EPISODE 1️⃣1️⃣

Jama'a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Hannunta Baba yakama cikeda damuwan dazaka iya gani kwance kan fuskanshi yace "Gwaggo dan Allah ki zauna kiyi shiru maza suyi magana, haba mana Gwaggo" Abdulhadi shima cikeda damuwan yace "dan Allah Gwaggo, dan Allah" cikeda bacinrai Gwaggo tace "aini banmasan kamilin mutun bane haka ba babba kuma,  nadauka irin yaran nanne dake tashen balaga masu kudi da rawan kai amman wannan kalleshi nutsaste kamili dashi" hannunta da Baba keja alamun ta zauna yasa ta zauna kan kujeran tace "nayi shiru yanzu amman wlh idan baku karbanma jikata hakkinta ba wlh zan bude bakina ehe" ta zauna tana goge kwalla, dan murmushi Musty yayi yataho wajensu anatse yace "dudda nasan kowa hankalinsa atashi yake gaisuwan musulinci wajibi ne dan haka Assalamu Alaykum" atare dukansu su Baba suka amsa, Musty yace "nasan meke tafe daku amman dan Allah alfarma nake nema inaso kafin ku yanke hukunci kokuyi wani abu zan muku bayanin komi dakuma asalin nuna muku video CCTV camera dake nan akowani lungu da saku na company mu" gyadamishi kai su Baba sukayi alamun tom, yace "ni sunana Mustapha nine babban abokin Imran gashichan aboki nane tun muna yara yan kanana" yanuna Abee daya maida kanshi kasa dukansu suka kalli Abee, Musty

yace “ga kannenshi chan Hamza da Ibrahim wayan nan kuma abokanenshi ne, Imrana nada yara hudu, biyu sun rasu tareda matarshi da akazo har gida aka kashe” ahankali su Baffa sukace “Allah musu rahama”  Musty yace “sai biyu yanzu keraye, namijin nada shekaru 22, macen 21, nasan kuna mamaki maisa nake fadamuku haka inaso kusan waye Imran ne, bawai sabida Abokina bane, tunda nake bantaba ganin mutum mai kiyaye dokokin Allah kaman Imran ba tun yana kankanin shi mutum ne kamili nutsastse mai amana, abinda kuma yafaru tsakaninshi da yarku was nothing daya wuce kaddara kokuma nace samin akasi akayi wannan shine kawai abinda zance bari na kunna muku CCTV camera footage na ranan dasukazo makarantan kugani Ibrahim zokasa”  zuwa Ibraheem yayi gaban babban tV dake office din yamakala flash dinshi saiga video yafara daga inda sukazo makarantan tundaga waje har zuwa ciki da lokacin datace zatai fitsari anajin maganan dudda bada kyau yake fitaba aka nuna inda ta tsaya tana juye juye dan bata gane bayin ba saitabi corridor tahau gudu tana ciro su waya da chocholate har zuwa inda ta bangaje Abee Musty yace “inaso kusaka idanunku akan wan nan mutumin” bayan ta wuce tai kwana aka nuno Abee yayi hanyar office nashi ya murda akulle sai kuma yay hanyar bayi saiga mutumin yafito, saikuma aka shiga lokacin da Lujain tashiga bayin da gudu daganan babu komi kuma sabida babu camera a bayi, saiga Abee shima yazo yashiga, Gwaggo ta gyara zama idanunta kaman zasu fito su sauka kasa, saiga mutumin yazo ya soka waya yana video jin muryan mutane yatafi yabar wajen kusan 2min da shiganshi saiga Lujain tabude kofa ta tsaya sai gashi anyo ball da jakanta da wayan ta tsugunna ta dauka ta goya ta gyara riganta tana waige waige tawuce dahar yanda mutanen nan suka mata kwatace saiga Ibrooo yazo har bayin yashiga rikeda key sannan aka nuna musu duka video Lujain a factory da yanda tai Plate har lokacin databar company su sannan ya katse.

Anatse Musty yace “abu na farko danakeso kugane kuduba lokutan da abin yafaru idan fasikanci ko wani abu sukayi dan wanan lokacin yayi yagama? Sanan akanme yana mai kampanin nan gabaki daya bawai shida wani ba bazai kaita office nashi ba inda akwai daki, bayi dakomi aciki sai nan bayin kowa bayin ma’aikatanshi Iyye? Koma bayin kowa ne zai iya sa security idan wani abu zaiyi yace kar wanda yazo banda haka kuma bayin maza ne ita meya kaita bayin maza dudda nasan yaran makaranta babu abinda waya baya sasu suyi tunda harta bugeshi batama tsaya ta kalleshi ba balle bada hakuri, abu na karshe video dakuke gani idan kunada wayanda sukasan computer zasu iya gayamuku cewa anyi editing dinshi da yanda kofan ke jijjiga da muryan karan datakeyi duka kari ne, saikuma shi wanan mutum dakukaga yay video yaturama abokina messege kan yanaso abashi miliyan dari da kampanin nan koyayi releasing video shi yana tarayya da wata shi yasan baiyi abu hakaba yay blocking kaman yanda kukaji abin nan kwatsam haka muma muka jishi kwatsam, dan Allah dudda dai babu abinda kaddarace bayasawa amman babu amfanin cewa wannan keda laifi ko wanchan keda laifi, munsan sunan diyarku yabaci haka shima nashi yabaci amman dan Allah kuyakuri, dan Allah abu baiyi dadi ba ko kadan” binsu Baba Gwaggo tayi da idanu daya bayan daya kowa jikinshi yay sanyi dan babu karya amaganan su bawai wanan ba dukansu sun kalli Abee baiyi kama da wanda zai aikata hakaba dan zai iya haifan Lujain dinma kuma itama tafadi abinda yakaita bayin tun kafinma suji bakin na mutanen nan, tsaf abinda tafadi shi suka gani a video, babu

atom of lie aciki, kumama idan akace za’ayi blame yarsu ce taje bayin maza ita takai kafanta, this is just a common mistake da kowa can make ganin yanda sukai shiru babu wanda ya furta abu yasa cikin kumfan baki Gwaggo tace “ohhh barakuce komi ba”? Dasauri Baba yace “Gwaggo dan Allah kiyi shiru kitashi mutafi gida kawai”.     ”mtswwwwww” Gwaggo taja wani mugun tsaki ta mike tsaye batai wata wata ba ta jaye gyalenta data lullube Lujain dashi idanunta sunyi jajir fuskanta yay jaaaa sabida kuka jikinta dabare da jirwajen drinks fuskanta har kyallin dankon drinks yake tana kuka sosai tana wani kalan ajiyan zuciya tarike jikin kayanta gam da hannayen ta data dunkule kowa yabita da kallo adakin banda Abee da kanshi ke kasa, duk wani mai imani da zuciya yakalli Lujain saiyaji jikinshi yay sanyi, Gwaggo na rike da gyalen ta taka zuwa gaban table din da Abee ke zaune cikin ihu tace “kawani sauke kai kasa kaman sabon ango kalli jikana nace, dago kanta ta kalleta” ahankali Abee yadaga kanshi yadan kalli Gwaggo sannan gently yakalli direction din datake nunamai gabanshi na faduwa sauke idanunshi dasukai jaa yayi kan Lujain dake kuka sosai idanunta akasa yay shiru danji yayi zuciyanshi tai wani iri, komawa Gwaggo tayi wajen Baba ganin yana kallon Lujain din datace ta fizge paper da aka bama Lujain amakaranta tadawo ta ijiye gaban Abee tace “kaga yanda akama jikata wanka da lemu tundaga ka har kafa banda haka makarantan suka bamu takarda waisun koreta sabida fasika ce mugun iri zata bata musu sauran dalibai” fashewa Gwaggo tayi da kuka sosai daidai nan ta durkushe awajen ahankali Abee yasauke kanshi ganin yanda tsohuwar da akalla zata girmi Hajiyanshi da yan shekaru na kuka sosai agabanshi, Baba da Abdulhadi ne sukazo wajen da saurinsu zasu dagata tace “wlh kuka tabani zan daga muku nono awajen nan ku kayaleni kawai” tai maganan tana tashi takalli Abee da kanshi ke kasa sannan takalli Musty tace “kaga yarinyar nan dakake gani haka marainiya ce uwarta na nakuda kanta haifeta ta mutu agurguje akai operation aka cirota sabida wai tasha ruwan cikin wanda yamutu yarinyan nan dakuke gani saida tai kusan shekaru biyu acikin kwalban asibiti ni ke biyan komi ubanta wannan din nan dakuka gani” tanuna Baba dashima yasauke kanshi kasa tace “shi baida kudin biyan kudin kwalba duba sha biyar duk ranan duniya acirota daga kwalban wai mutafi gida, likita kuma yace ana cirota baifi tai awa ashirin da hudu ba zata mutu, mijina babansu mai kudin kauye ne daya mutu inada gado kap na saida gidaje na manya manya a binni guda hudu da shanaye na kauye haka na biya dubu sha biyar biyar na shekara biyu cur kafin acirota, nine komi na diyar nan tundaga zama a asibiti, abincinta, kayan sawanta da rainonta da komi ma, koda aka bani ita haka muka dawo gida yau lafiya gobe ciwo ko shigowa bayayi yadubata dan yanada wasu yaran lafiyayyu marasa ciwo, nikuma na nunamai zan iyama jikata mai ciwo gata tamafisu jin dadin duniya, saida yarinyar nan takai shekaru bakwai aduniya tafara makaranta” Gwaggo tashare idanu dan hawayen sinki tsayawa tace “bakuga yanzu tana shatara a SS2 ba bayan su Samira suna shekaru sha shidda sun  zana jarabawan kare sakadire, amman ita har yanzu bata gamaba sabida ciwo, ni nasan wahalan danayi akan jikata nasan gumi rashin bacci rashin sukuni danasha akanta, har yau har gobe tunda tazo duniya bantaba baccin dare bantashi ba saita tadani, yau awayi gari sunanta yabaci kuce nai shiru koda akace zata mutu ban hakura akanta ba yanzu ne da lafiyanta kalau zan hakura nai shiru akanta wlh wlh Billahillazi La’ilaha Illahuwa bazata yuba ko laifinta ne ko laifinshi ne nidai nasan bakuyi fasikanci ba dan bangani alamu a jikinta ranan ina tareda ita data dawo daga makarantan ai kaima bakai kama da Babba mai lalata yaraba dan haka idan kunason zaman lpy abu dayan zan gayamaka shine ka auri jikata! Ka auri dan baran iya da raina da lafiya na

inaji ina gani sunan jikata yabaci ba, tun yanzu a makarantan su kadai an mata wanka haka da koro uwa wacce aka kamata dumu dumu tana zina, ahanamini yarinya fita titi gudun kar adinga nunata wlh baran yarda ba, hanya dayace shine ka auri jikata!"

Jama'a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI
Jama'a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

EPISODE1️⃣2️⃣

Kowa na dakin hatta Lujain din dake kuka sosai dashi kanshi Abee saida yadago kanshi yakalli Gwaggo jin abinda tafadi, cikin tsantsan nuna seriousness Gwaggo tace "eh haka nafadi, nace saika auri jikata! Duk abinda babba ya hango karami bazai hango ba, wannan video dakuka nunamin kokun watsashi aduniya mutane ba yarda zasuyi ba bazai wankemin jikata ba, hanya daya zai wanke jikata tastas shine ace kaidin mijinta ne da aure tsakaninku, daga masu gulma dashi usulin algugumi dan wutan jahannama daya yada video dana tabbata baku ganshi ba haryau saisuji kunya kaga ko banza yay aikin banza, shi bazai sami miliyan darin ba shibai

samu kampanin ba" hannunta Baba yakama zaiyi magana Gwaggo ta fizge hannunta idanunta sunyi jajir tace "wlh wlh duk wanda yace saija dani cikinku saina tsine mishi albarka ubanme zaka gayamin lokacin dazata mutu ma baka tsaya mata ba yaune da aka kirata da fasika zaka tsaya mata? Nine komin Lujain, nine uwarta, nine ubanta, nine kakanta, kamin shiru kawai, wlh wlh saiya aureta akan wani dalili zaija sunan diyata ya baci kuma bazaiyi komi ya wanketa ba, wlh saiya aureta inba hakaba wlh wlh sai hukuma tarabamu, marainiyan yarinya na eh ku jibeta fa abin tausayi ubanta bai damu da ita ba sabida yaga batada mahaifiya, inda yau mahaifiyarta na raye Kunsan kalan tashin hankalin dazata shiga kuwa? Bayan kunsan rayuwa yakoma yanzu iskanci ado ne wajen namiji mace ce rayuwanta zai baci har abada, yanzu awannan video banda bayanshi anga fuskanshi eh? Yar yarinyar nan dai akaga fuskanta har akaga tana gyara riga, idanba aurenta yayi ba koya wanketa wazai auri Lujain iyye? Kufadamin wani namiji ne zai aureta? Wasu iyayene zasu bar dansu ya auri yarinyan da video fasikancinta ke yawo a yanar gizo? Shi yanzu bashi kwana biyu anmanta dashi itako fa? Namiji mutane barasu iya taranka ma itako Yar yarinya mace halama saidai tadaina fita danta fita tareta za'ayi amata duka a titi, yakukeso tayi? Matar ubanta kuma dama ba sonta takeba kaga gwara ka aureta naga kanada hankali kanada yara dasunma girmeta zaka rikemin ita amana koyau na mutu banda nadama dama kullum tunanina wazan aura mata da hankalina zai natsu dashi ashe kai Allah zai kawo mata amman ta wannan kaddaran" Gwaggo tafashe da kuka muryanta kawai akeji a duka office din ganin yanda take kuka kuma su Baba sun kasa mata magana gudun karta tsine musu yasa ahankali Mustafa yaje inda take tsugunnawa yayi yakamota kaman yakamo mahaifiyarshi hannu yasamata a fuska yana goge hawayen datake yace "dan Allah Gwaggo kiyakuri kidena kukan nan dan Allah sabida ni" ahankali tahadiye kukan tana kallonshi cikeda lallashi yace "Gwaggo kinga nan office neko wannan matsalan kuma matsala ce daya kamata atattauna agida kibamu address din gidanku anjima da daddare namiki alkawari dukanmu shima harda iyayenshi zamuzo sai ayi magana da kyau Gwaggo kinji Gwaggo amman yanzu kutafi, itama ku kaita gida tacire kayan nan kar wani abun yasameta maganganun nan da ake agabanta bai dace ba, kuma babu kyau yanda kike kuka agabanta, kece karfinta, kobaki hakura kitafi dan kowaba kiyi dan ita naga yanda kike sonta" juyawa Gwaggo tayi takalli Lujain dake kuka sosai har lokacin taji barata iya musuba tace "gidan mu na nan kwanan tipa a Gwarimpa idan kun shigo gida na biyar mai gate mai ruwan goro" anatse Musty yace "zamuzo anjima da daddare" tashi tayi tadauki gyalenta dake kasa taje wajen Lujain ta lullubeta dashi ta kama hannunta tadagata tace "muje Allah natare dake, nima ina tareda ke" su Baffa duk suka tashi, Musty yace "kaisu ta back door bata gaba ba sabida reporters" binsu su Ibro da Hamza sukayi dan kaisu sannan ahankali Musty yazauna tareda sauke wani ajiyan zuciya yana kallon Abee, Harun yace "wlh wlh idan aka kamo yaron nan I will make sure yay rotting at the worse Nigeria prison" Abdul yace "the guy is evil" daidai nan wayan Musty yashiga ringing ganin Hajiya ne yasa yakalli Abee da kanshi ke kasa yace "tashi muje gida Hajiya is calling" batare daya kalleshi ba yana kokarin fara typing yace "ban tashi daga aiki ba sai 4, and this is just 12:54" shiru Musty yayi yana kallonshi Allah kadai yasan yanda yake hurting right now amman bazai taba nunawa ba, ganin bakinciki Abee zai cusamai yasa yajuya yakalli su Harun yace "kumuje" saikuma yajuya afusace yadauki wayan Abee dake kan table yace "shima ka kwace idan ka isa" yawuce yafita fuuu daidai Hajiya na kara kira dauka yayi kafinma tayi magana yace "Hajiya gani nan zuwa komi yazo dasauki kada kidamu kanki hawan jininki yatashi" katse wayan yayi suna fita

suka shiga mota sai gidansu Abdallah da Kausar sun dawo daga makaranta dudda sunada lectures ganin videos dake trending na babansu, Zainab data tafi daga ita har mijinta sun dawo, kofar gidansu yacika kaman anyi mutuwa dayan anguwa babu wanda baya sonshi a anguwan dukansu sun karyata guards na estate dinsu sun hana ko reporter daya ya shiga saida su Musty suka fara gaisawa da mutanen waje sukace shairi akamai sannan suka shiga ciki bayan babban Liman na anguwan wanda yake matsayin ubansu yabisu zuwa cikin gida duk suka zazzauna a falo idanun kausar yay jajir taci kuka harta gaji na Abdallah ma haka amman shi baiyi kuka ba.

Hajiya kafin suyi magana tace “ina yake”? Musty yace “ai kinsan Imran da taurin kai yace aiki yake sai 4 yake tashi daga aiki munbarshi achan danko jawoshi zamuyi da karfi bazai tahoba amman Ibro da Hamza na chan tareda shi karki damu” tagumi Hajiya tayi Anty Binta ta bubbuga mata baya yace “dan Allah Hajiya kada kidamu kanki” anatse Hajiya tace “Meya faru Musty”? Ahankali yabasu labarin daga farko har karshe tsaf da yanda iyayen yarinyar sukazo da abinda sukayi kowa yay tsit adakin na kusan minti biyar sannan Hajiya tai breaking shiru takalli Liman tace “Liman kaine kake matsayin mahaifin yaron nan yakake ganin za’ayi”? Ahankali Liman yace “shi aure rufin asiri ne kuma sutura ne ga mumini, gabaki dayan mu nan munsan Imran bazai taba iya aikata wannan abuba abinda nakeso kuduba anan shine ayar dake tattare da abin nan inhar Allah ya shiryamai wannan kaddaran to da dalili, saikuma abu nabiyu shine inhar akabar zancen nan haka shikenan yabata ma ita yarinyar dashi Imran suna nan da gobe zakuji wasu sabbin labarai da kazafi da sauransu natashi indai mutane ne, saikuma sana’arshi da kampaninshi zai jijjiga that is idan hukuma bata shigo bama ta rufe company gabadaya ba, amman yanzu duk idan kuka ijiye sauran hujjojin nan kuka dauki hujjan farko dana kawo kaddaran suce Allah yaga dama yakuma tsara musu ita ahakan dan haka ayarda da auren amusu auren amusu auren asanara duniya su daman ma’aurata ne dan killace mutuncinsu hakan kadaine za’ayi ya wankesu shikuma yaron kubashi dududu satin nan dakanshi zai kawo kafanshi yanemi gafara zan nunamai ayar Allah ba wasa bane sannan Allah sarki ne tsarkakke Al Azza Wajal! Dan haka mu amince da abinda sukace mu kalli maraicin yarinyar”, dan hawaye Hajja ta share tace “nasan bazai taba yarda yay aure nan ba, babu abinda Abee ya tsana kaman aure, amman yau zan nunamai nine mahaifiyarshi, zan iya komi dan kare mutuncinshi aduniyan nan” sallama Liman yamusu yatafi sukuma kowa yay zugum falo saida aka kira la’asar ne ma su Musty suka tuna ko azahar basuyibasuka wuce.

Biyar daidai on the dot Hamza da Ibro suka shigo office din yana zaune akan kujeran su kallo daya yamusu yadauke kai anatse Ibro yace “Yaya Imran is 5 mutafi gida” dago idanunshi yayi yakalleshi ahankali Ibro yasauke kanshi kasa dan gabaki dayansu babu mai iya jure idanun Ya Imran akansu kwarjininshi is way to much, kaman daga sama yace “yaushe nida ku muka fara barin office tare?” Da sauri dukansu suka dagakai suka kalleshi karamin Mac book dinshi da yan kananun abubuwanshi yashiga hadawa batare daya kallesu ba babu alamun wasa akan voice nashi yace “ku kama gabanku” daidai yatashi daga kan chair din tareda daukan Car key

nashi laptop dinshi a hannunshi yafito wuce su yayi duk suna tsaye suna kallonshi yabude kofa yafice dasauri suka fito Ibro ya tsaya yana kulle office din ganin yayi hanyar dazai kaishi main entrance suda sukeso yabi ta kofan baya dan reporters har yanzu na main entrance yasa aguje suka bishi yana jinsu amman ko juyowa baiyiba yakallesu anatse yake tafiya one after another kaman mai sarauta har zuwa gate din suma security nashi daga gaban entrance din ganin Oga yasa sukaji kaman sucemai yajuya yakoma ta dayan exit din amman shakka da tsoro yahanasu, budemai kofa sukayi yafice reporters na ganinshi suka taso aguje ana binshi kowa da kalan tambayan dayake watsamai koransu security nashi suka dingayi suka rike hannu suka taresu shikuma yay wajen motanshi yabude laptop dinshi ya ijiye a dayan sit na gaban sannan yashiga yarufe kofa yatada motan yafice, su Hamza ma suka shiga motocin su suka mar mishi baya.

Agaban estate nasu wasu reporter yagani but anhanasu shiga dayake motarshi tinted ne basusan shibane aka budemai gate yashige abinshi yan jama’a yagani akofar gidansu ciki harda Arif dolenshi ya tsaya akofar gidansu yasauke glass batare daya sakko daga motan ba, chaaa jama’an anguwa sukamai akai suna Allah kyauta Alhaji duk mai nufinka da shairi Allah ya maida musu Liman yamana bayanin komi Allah natare dakai kuma zamu nunama mutumin ayar Allah ba abin wasa bane wlh saiyazo harnan anguwan dakanshi yabada hakuri dan murmushi yamusu yace “nagode” hakan yasa suka watse saura Arif kadai da idanunshi sukai jaa yataho wajen motan ahankali zubamai idanu Abee yayi kaman babu wani abu yace “what are you doing here kabar Amarya”? Kasa magana Arif yayi but kana ganin hankalinshi kasan atashe yake, dan murmushi Abee yamai kadan yace “wuce ka koma gidanka” gyadamai kai Arif yayi ahankali babu musu yakoma yashiga motarshi shikuma Abee yatada motanshi aka budemai gate yashiga cikin gidansu.

You can read EPISODE 13 a IG💃💃EPISODE 1️⃣3️⃣

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Parking yayi awajen parking nacikin gidan, yakai kusan 5min zaune acikin motan ya jinginar da kanshi tareda lumshe idanu sannan yatashi yabude kofan motan yafito ahankali da Maigadin

gayamiki babu kyau tagumi ba” kaman jira take wani kalan rushewa da kuka tayi  sosai tanuna kanta tace “Gwaggo su princess sunce wai ni Yar iskace, ni karuwa Gwaggo ai kintuna lokacin dana fara period kince min ko hannun namiji yarike zanyi ciki ko” Gwaggo ta gyadamata kai itama kaman zatai kuka ganin yanda Lujain ke kuka bitterly, cikin mugun kuka tace “wlh Gwaggo, wlh wlh ko yatsana bai tababa, baimazo kusadani ba, Gwaggo bantaba ganinshi ba sai ranan, Gwaggo nida banda saurayi babu wanda kesona sabida ni katuwa ce inada kiba, dawane zanyi iskanci? Gwaggo ni yanzu konaga mutumin ma bansanshi ba baranma ganeshi ba, Gwaggo nayi ihu daga ganshi bisa ka na abayi sabida nasaka earpiece banmaji karan tafiyan da ba, ganinshi akaina yasa nai ihun nan ba wannan ihun wanda wanda….. wanda naji aaaa……..” tawani kalan fashe da kuka sabida yanda abin kemata ciwo, hannunta Gwaggo takai zata share mata hawayen cikin kuka kaman wanda ta tuna wani abue tace “shine suke kirana fasika, karuwa da Yar iska, Gwaggo ni, ni ni Lujain ce karuwa” tanuna kanta tana wani kalan kuka mai tsuma rai dayasa Gwaggo tafara matse hawaye tana kallonta takasa lallashinta tace “Kola harda cewa wai zaiyi Iskanci dani ya siyamini shawarma guda biyar da Fanta goma sabida nine mayyan abinci dazan iya iskanci idan zaa bani abinda zanci, wlh banyi komiba Gwaggo ni danasani da banmaje excursion dinba dan dama banso zuwaba” yanda take kuka yasa Gwaggo tahau matsar kwalla tace “Allah kaimu gobe wlh wlh har ajinku zanje sainayi dambe da gantalallun yaran nan masu tallan bushahhsen gero, shegun yara wayanda ba’a haifesu ranan juma’a ba, ai gasunan sune zasusha kunya tunda Imrana ai yanzu mijinki ne” duk wani kuka da Lujain keyi tsayawa yayi ta kalli Gwaggo da rinannun idanunta tana zarosu tama kasa tambayan komi wani kalan washe baki Gwaggo tayi ganin tana kallonta tace “ai wlh kinyi goshi Lujain dakika sami miji irinshi ga kudi, ga kyau gakuma hankali jibi girman kampaninshi barima kiga” Gwaggo ta tashi da sauri tayi falo ta kwaso mata kwalin giro dana sweet din tace “kinga goro da sweet na daurin aure, jiya da daddare kina bacci aka daura gaban kawunanki da duka dangin su Imranan anan falon babanki bakiga idanun Maman su Samira ba kaman zasu fado kasa sabida bakin ciki taga Allah yabaki mai kudi daga sama ita dake cewa barama kisami mai aurenki ba balle mai kudi yanzu ai gashinan ke kinyi miji nata zankadaddun yaran dabata basu abinci suci su koshi sabida karsuyi kiba na nan agabanta” Gwaggo takara washe baki tace “dazaran kin tare da yan kwana biyu nima zan tattaro yinawa inawane nadawo gidan naku ina zan iya zama gidan talaucin nan ubanki na fama da saida atampopi akasuwa too wlh badani ba” wani kalan mugun kuka Lujain tasaki tace “Gwaggo ninace muku ina sonshi ne dazan aureshi dazu nadauka tsoratasu kawai kikayi akanme zaki auramin mutumin dabanma san kamannin shiba?  Mandawari na fa”? Wani mugun harara Gwaggo tamata tana tabe baki tace “kina ganin yanzu da wannan video naku ya zagaye yanar gizo mandawari zai yarda ya aureki idan ma ya kulankin kenan? Yau shekara nawa kina bibiyan yaron dabaimasan da zaman ki adoron kasan nan ba” cikin kuka tace “eh nidai shinake so, ai dama celebrity basa amsa messages da wuri, kinsan followers nashi nawa ne almost 400million global followers, baruwanki da ni da Mandawari, wlh wlh banason Auren nan nibaran aureshi ba” dan dariya Gwaggo tayi tace “aure kuma tuni ya dauru yarinya naki wasane, bakida hankali yanzu lamarin nan na manya ne kimana shiru kawai ki kalli ikon Allah” wani kalan kukan datake yasa taji cikinta na hantsinewa ta tashi da gudu tana kukan sai bayi Gwaggo tabita duka shayin datasha amayo dashi tayi tadasa uban kuka tun Gwaggo na lallashi ta tana bata baki harta shareta ta kwanta akan gado abinta tai bacci itama daga baya anan kasa baccin yay awon gaba da ita.

Koda Gwaggo ta idar da sallan asuba da jan charbinta tashi tayi tafito falo tareda bude kofa ta taho bangaren su Mama bude kofa tayi uwa an biyota tazauna akan kujera daidai Mama tafito daga dakinta ganin Gwaggo taso tafirgita saikuma tace "lafiya Gwaggo da asuban nan" kallon banza tamata tace "lafiyan ce takawo haka" tabe baki Mama tayi tawuce tashiga kitchen abinta bata wani jima afalon ba saiga Babatareda Yayansu kafinma ya gaisheta hannu tamikamai tace "bani kudin sadakinta" dan kallonta yayi da mamaki yace "Gwaggo dama zan cika kudi ne namata kayan daki" cikeda daga murya tace "bakaji ance yanzu anan gidansu zasu zauna ba baa gama gidanshi ba lokacin daya gama gidanshi anemo wani kudin amata kayan daki" zama kawai Baba yayi yana kallon mahaifiyar tashi ganin haka yasa tace "ko baraka bani bane"? Ahankali yace "zan baki mana Gwaggo amman mezakiyi dahar dubu dari biyu gabadaya" cikeda ihu tace "yoo gyaran Amarya mana dudda ma babu wani lokaci mai tsawo yau kwana hudu yarage atafi da ita gidan mijinta amman dai abinda zanyi kenan" Mama dake tsaye cikin kitchen tanajinsu ahankali tace "fitinanniyan tsohuwa inama tamutu ahuta" kallon Yayan su Samira Baba yayi yace "jeka kawo kudaden nan adakina Auwal" tashi Auwal yayi yawuce dakin Baba baijimaba yafito da bandir na yan 1k guda biyu yakawoma Gwaggo yage takardan guda tayi sannan takalli Auwal din tace "kaine Babban jikana kaito ga dubu biyu sadaka kasama Auren kanwarka albarka" gudun fitina yasa yasa hannu yakarba yace "Allah basu zaman lpy" kwalama su Samira kira tayi tace "nasan kuna jina to kuzo nan" kaman munafukai suka fito suka gaida Baba da Gwaggo dake kallonsu tace "nasan kunsan kaddaran daya fada kan kanwarku Lujain, koma baku sani nasan farfesan uwar ku tariga ta fesa muku labarin daga tushe zuwa iri to yanzu dai Alhamdulillah Allah yabata miji nagari son kowa kin wanda yarasa da ake cewa bazata taba samin wanda zai sotaba da wannan kiban babu kalan gorin da baku mata ba to yanzu dai ga sa'an datayi dan haka nan sadakin tane zan muku sadakan dubu dai dai duk ku sanya mata albarka" dubu dai dai tazaro tabasu amsa sukayi kowannensu yace "Allah sanya alheri" tace Ameen, sannan takalli Baba tace "kake kallona kokaima nabaka ne" girgixamata kai yayi tace "bari naje namata abincin kari zan fita anjima, da daddare tarinka amai inhar naji jikinta da zafi zaka kaita asibiti" Gwaggo na maganan tana daga zaninta tana tura kudaden a cikin lalita tawuce tafita tana kaiwa dakin akan dadduma taga Lujain din tai salla takifa kanta akafa tana kuka hararanta Gwaggo tayi tace "aisaikiyi" kitchen tashiga tahau dumamata shinkafan jin kukan kuma taji takasa daurewa fitowa yayi tashiga uwardakan zama tayi agabanta tabuga tagumi tana kallonta tace "wai Lujain saikin kasheni tatas kinga bana numfashi zakiji dadi iyye? Yanzu mikikeso fadamin"? Ahankali batare data da go kanta daga kafanta ba tace "ni banason Auren nan ban isa aure ba kumani Mandawari nikeso" shiru Gwaggo tayi tana kallonta saikuma tace "kikace baki isa aure ba inace nannan Aisha har ajinku ta Islamiyya dake shekaru sha shidda tai aure har anko saida kika tasani agaba namata, su Zainab ma dake sha bakwai ba suna zana jarabawan gama sakandire aka musu aure ba kema inda rashin lafiya yabarki kinfara makaranta da wuri da yanzu kin tsufa da gama sakandire, kawayenki kadai yan layin nan dasukai aure sunkai hudu yanzu da akazo kanki ne zakice baki isa aureba, shikuma Mandawarin yasan ki? Yasan dake? Yamasan sunanki? Ke yarnan ki kiyayi kanki da auran calamburuti ina gayamiki barinma Mandawarin nan mai kamada shaidanu har kitso yakema gashin kanshi" sosai take kuka still bata dago kanta ba tace "wlh shiba shaidani

bane Gwaggo yanada kirki, yana bada taimako har gidan marayu yake zuwa, yarabama guraguma keke" Haba Gwaggo takama tace "to akace miki shi kadaine mai kirkin duniya" tai maganan tanajan hanci jin kauri natashi tace "nashigesu wannan yarinya tasa na babbaka abinci" tai maganan tana fita daga kitchen da sauri kashe rishon tayi dan arisho take girki tadawo zama tayi kusada Lujain din ahankali tadagota tace "haba Yar jikata Yar lukutata Yar bulbul Yar kyakkyawa yimin murmushi ingani" ashagwabe hawaye na gangarowa daga idanubta tamakema Gwaggo kafada irin baratayiba, washe baki Gwaggo tayi tace "naji to zan miki abinda kikeso" dasauri tace "zaki raba Auren ki nema mini Mandawari"? Gyadamata kai Gwaggo tayi wani kalan murmushi tayi dayasa dimples dinta suka lotsa tai bala'in kyau tawani rungume Gwaggo Gwaggo na dariya tace "to jekiyi wanka nima fita zanyi amman bari nafara hada abincin ki" tashi tayi tawuce bayi tsaf Gwaggo tahada mata abincin kari da shayi wani green towel ta daura tazo ta zauna tafaraci Gwaggo tadauki mayafi tace "tonatafi kiyi zamanki adaki kada kije konan da chan kinji" gyadama Gwaggo kai tayi.
Tun safen nan sai wuraren 4 na yamma Gwaggo ta dawo da buhu buhu na itace da saiwowi saikuma zabi kaji da tantabaru da aka hadesu aka kullemusu kafafu, wasu yara takira tasa suka yanka mata aka gyara tafito dasu karfi da yaji sukazo suna aiki Gwaggo tun tana yarinya tayi gadon iya hada magunguna lafiyayyun tsumi tayi anan tsakar gida akan ittace daya hada da zuma da mazankwaila babu suga ko digi, sai farfesun su zabin datayi na magungunan hada su Samira tayi da Lujain din duk sukaci sannan tashiga hada farfesun jijjibi wasu magunguna kuma ta shanyasu, sai wajajen shadaya suka gama komi su Samira suka koma dakinsu itada Lujain suka koma dakinsu tsumi tazuba cikin kofi tabama Lujain tasha sannan tahada mata wani ruwan zafin wasu itace data dafa, Lujain dake zaune tana kallon cartoon a falo tanashan tsumin kadan kadan tace "Gwaggo wai magungunan menene" batare da Gwaggo takalleta ba tana saka farfesun daban daban datayi dasuka jera a robobi a dankareren freezer ta tace "shawara tamiki yawa baki gankiba Saura kadan kizama zabiya tsabagen haskenki" yatsine fuska tayi tana gyara daurin towel dake jikinta tun Gwaggo namata mitan tawul harta barta dan bata taba ganin mutumin daya tsani kayaba irin Lujain.
Gwaggo bata kara mata maganan auren ba sai uban magungunan datake loda mata na safe daban na rana daban na dare daban, ita dakeson yogurt saida Gwaggo tasa tasani yogurt sabida yanda take zubamata garin magana a yogurt din daban daban.
****

Yau Friday tun ranan Monday bayan an daura auren nan dasuna shigowa gidan Abee yawuce dakinshi dagudu rabon kowa dayaganshi ko masallaci baya fita, Ya kulle dakinshi baya karban abinci yanda za'a kawo abinci a ijiye gaban dakin haka zaa dawo adauka, shigowa gidan Musty yayi afalo ya zauna yana kallon yanda Hajiya dakowa yay jugum ahankali yace "har yanzu bai fitoba Hajiya"? Wani kalan ijiyan zuciya Hajiya ta sauke tace "ai inhar ciwon nan yatashi saikuma yanda tayu, har yanzu likitan nashi"? Ahankali Musty yace "gashinan zuwa Ibraheem yadaukoshi daga airport" shiru dakin yasakeyi babu wanda keda walwala Kausar da Abdallah yakalla sun bashi tausayi yauma basuje makaranta ba, jin karan gate yasa Musty yaleka yace "Alhamdulillah gasunan" Dr na shigowa falon baima tsaya gaidasu ba yace "give me his room key" ciro key Hajiya tayi daga Yar purse na hannunta yawuce sama kowa na zaune akasa, kusan 30min yayi aciki sannan yasauko kowa tashi tsaye yayi yana jiran abinda zaice dan

murmushi Dr yayi yace “ku kwantar da hankalinku he is fine” ajiyan zuciya kowa yayi, Mustafa dake kallonshi yace “Dr maisa yake kulle kanshi yaki fitowa duk yanda Imran yakaiga son bautan Allah jam’i baya wuceshi zakaga hatta masallacin baya fita yaje, yaranshi dayakeso baya yarda yagansu baya ganin kowa, why is it like that”? Ahankali Dr yace “kasan patient nawa aka rasa to PTSD post traumatic stress disorder? I applaud Imran bakaramin jarumi bane mai kwazoba he’s fighting it with all of his strength, PTSD nakama mutum ne Idan mutum yay experiencing a shocking event, mutuwan matarshi, yanda akai hanging nata sun harbeta a goshi, aka kashe yaranshi in cold blood shine abinda yasa PTSD yakamashi, symptoms nashi shine magrine, da mutum ya tsani kanshi yayita bama kanshi laifi akan abinda yafaru, mutum yay isolating kanshi daga mutane kaman yanda yake yanzu dasauransu irinsu rashin yawanyin magana, gashinan gashinan ne, for 13yrs I’ve been managing him da little medication su Anti depression dakuma psychotherapy, yana zuwa har office dina he talks to me I talk him out of all the guilt the experience dakomi dayake feeling, for a long time now kusan shekara daya kenan baitasomai ba sai ranan Monday din nan shima sabida wannan dan he’s traumatized sabida kazafin da akamai aka kuma yada  aduniya yanar gizo, saikuma this sudden Marraige, Auren nan dan gani yake he’s betraying his late wife, yanzu dai I assure you komi yazo karahe, Hajiya inason kije kiyi magana dashi but before then dukku zazzauna inason magana daku gabaki daya” zama dukansu sukayi shima Doctor yazauna yace “all abinda patient na PTSD ke bukata is love and support from close family nasu and friend, ku nunamai kuna sonshi he means a lot to you, sannan kununamai ku bama kusan yana ciwo ba koyanada wani ciwoba duk randa yabude kofan nan dakanshi yafito kuyi mu’amala dashi kaman bakumasan yashiga daki ya kulle kanshi na kusan kwana biyarba baci basha kungane”? Dasauri kowa yace “eh” Dr yace “sannan karkumai kuka, don’t show him pity rather show them love, idan yaga kuna nunamai pity kunamai kuka zaiyi worsen condition nashine dan he will feel yana causing muku pain, karku nunamai kowani abu instaed ma zai iya idan yafito kuce mai babu kaza kaza kaza agida, Abee inada assignment kaza kaza kungane engage him in something life moves on” yakalli Hajiya yace “idan kinje dakin nan ba danki mai lafiya ke magana ba, ba Imran dinki zakigani ba, this one is Imran mara lafiya, PTSD mess with brain Hajiya, so no matter mezaiyi don’t show weakness kokuma kiyi kuka agabanshi, as his mother handle him kaman jariri tell me kinasonshi he’s your everything, sannan idan kin shiga dakin daidai da hasken screen na wayanki kada kisake ki kunna bayason haske bayason hayaniya bayason kuka at this time cus all of that nakara tunamai da traumatic experience na lokacin memory nadawo mishi fresh, idan tadade adakin ku aikamata da abinci kar wanda yashiga dakin abakin kofa zaku ajiye kutafi, babu abinci acikinshi sannan he’s dehydrated, ga weakness kungane” atare duk sukace to, Hajiya share hawayen fuskanta tayi tass sannan tawuce sama, Dr yabi kowa na dakin dasukai jugum da kallo yace “he is fine nan da 24hrs that’s idan yamakai kenan ya warware” yay maganan yana bama Ibraheem prescription sheet yace “he needs this drugs now kuje kusayo” tashi Musty yayi yakarbi takardan a hannun Ibro yace “bari naje nasayo kai Ibro drop Dr at home tunda ba mota a hannunshi” suka fita tare.

EPISODE 1️⃣5️⃣

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp

da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Ahankali Hajiya tabude kofan dakin tashiga ciki tareda maida kofan dakin tarufe dakin duhu kaman tsakiyan dare bata ganin komi amman haka ta lallaba takarasa da tattaba bango harzuwa wajen gadon tazauna abakin gadon ahakali, dan ijiyan zuciya tasauke tana gyara numfashinta ahankali tana saita kanta, murya chan tace “Imrana Hajiya ce, your Mom” dan murmushi tayi, tace “natuna ranan da aka faracewa ina dauke dakai acikin cikina I was so so soo happy, tun aciki ka kasance yaro mai hakuri wanda baida damuwa ko kadan, cikin duka yaran dana haifa aduniya dudda kaine dan fari kai kadaine banma mugun laulayi ba sannan nakudan kama haka kasan me mahaifinka ke yawan kiranka dashi”? Tadanyi murmushi tace “dan baiwa” dan dariya tace “kuma bantaba karyata sunan ba sabida hakika kai dan baiwa ne, you are a God gift, muna tsananin talauci amman muna haihuwanka Allah yafara budama Babanka kofofin samu, tun kana dan yaro kankani 10yrs ka sauke Al Qur’ani mai girma, kana zana JSSCE kaci, WAEC da Jamb duka sau daya kayi kaci, kana applying zama soja sau daya kasamu, bayan kai quitting kanasa hannunka a sana’a Allah yadafa maka kalli company daka gina ayau in just how many years, kampanin ka shine number one a Nigeria dana Africa gabaki daya, kuma kampanin yay suna aduka duniya gabaki daya, imagine kampanin ka nacikin top ceramic company da Forbes sukai publishing, idan kai ba dan baiwa bane kai menene Imran? You are my son Imrana, abin alfaharina, sanyin idaniyata, yarona mai kyakkyawan zuciya, yarona mai taimako, yarona mai jama’a, yaron na yaron Hajiya Sadiy…….” Ahankali taji saukan kanshi akan kafafunta yakama duka hannayenta biyu hannunshi narawa sosai yakaisu zuwa fuskanshi ya kankame muryachanchan kasakasa dan itama Hajiya dabadan ta natsu ba da barataji ba yace “Hajiya” ahankali itama kaman yanda yay magana tace “Imrana” bakinshi da lips dinshi da duka jikinshi bari suke duka cikin wani kalan murya yace “Hajiya I am scared hold me” wani kalan kankameshi tayi yakifa fuskanshi akan cikinta kaman dan yaro jikinshi nawani kalan bari, ahankali tace “shi shiiii I am here now don’t be scared yarona, Mamanka na nan” wani kalan jiniya taji yafara daya tahoda kuka sosai tunda Hajiya take tana ganin tun bayan da Inrana yay girma yaune nabiyu datake ganin kukanshi da rasuwan Muna shima hawaye ne kawai sai yau yaukuma kukane jitayi zuciyanta na breaking babban mutum ke kuka haka Innalillahi wa innailaihi raji’un, cikin kuka yace “Hajiya they killed her sannan suka dauketa sukai hanging nata da igiya a fanka kirjinta na fitarda jini from harbin bindiga, kalli hannuwa Hajiya gabaki daya duk jini Muna da nasu Abdul ne kingani” cikin kukan yadaga hannayenshi yana nuna mata acikin duhun dakin, gyadamai kai tayi ahankali tace “nagani Imrana Allah zai saka

maka kaji, daina kuka kada su rainamin kai, kanuna musu kai jarumine jarumina kaji" wani kalan ajiyan zuciya yake saukewa yana shesheka, ilimi education ma yayi ne arayuwa dan idan wasu sukaga irin abin nan da Abee yake cewa zasuyi kodai Ya haukace kokuma aljanu ne nanko is a medical condition call PTSD, zaro hannunta Hajiya tayi tasaka cikin suman kanshi tana shafa kanshi ahankali tace "ya isa hakan nan duk wanda ke neman ganin bayanka Allah bazai barsu ba kuma kasan mene duk wanda aka kashe dan aljanna ne so be happy, I love you so much Imran, nasan cewa bansha gayamaka hakaba sabida bakada magana sosai bakada hira dani, kuma I use to feel ka girma kai babba ne ga manyan yara what's the point of telling you ina sonka, but I love you deeply Imrana, ina bala'in kaunar ka dako sauro banson yatabamini kai, kome zai sameka gwara yasameni burina kullum inganka lafiyanka kalau, I want you to fight Imran, fight this thing for me ni mahaifiyar ka, for kannenka, for yaranka Abdallah da Kausar, fight for your family, fight for your friends and love ones, tell yourself I am fine! I am okay lafiyata kalau, you are a fighter! Yarona jarumi ne that can fight anything, inasonka sosai Imran" Mama tai maganan duka ahankali takai bakinta saman sumanshi ta sumbaci kanshi jin kukan dayakeyi na raguwa ahankali, murya chan kasa tace "zakasha ruwa"? Girgixamata kai yayi alamun a'a, murya chan kasa tace "shayi fa Kausar ta dafamaka shi zakasha"? Shiru yayi kaman bazaice komiba saikuma ya gyadamata kai ahankali wani kalan hamdala tayi azuciyanta tace "kwanta anan in daukomaka" baiyi ko motsi ba daga jikinta hakan yasa gently ta kwantar dashi akan gado da saurinta tai wajen kofa tana budewa taga tray shayin da kof an ijiye musu da magani balli daya rak akai hakan yasa tadauko tashigo dagashi tazo tadinga bashi shayin tass ya shanye yasha maganin sannan yakara maida kanshi kan cinyanta ahankali take shafa bayanshi ahaka bacci yayi awon gaba da shi.
Kusan 2hrs Hajiya tayi adakin saida ta tabbatar da bacci yashigeshi sosai dan ayanda yake baccin zaka gane yadade baiyi bacci ba yasa ta tashi tareda jan bargo tarufamai, tsugunnawa tayi ta tofamai addu'o'i sannan tabude kofa ahankali tafita daga dakin tasauka kasa, duka yaran tagani afalo Musty shima yana nan Kausar da Abdallah takalla dake kallonta ba kakkautawa tace "In sha Allah komi yazo karshe now kowa yaje yacigaba da aikin dayake" tana maganan kowa yamike yana hamdala Maman Aneesa da Kausar dasu Sajida da Zainab suna kitchen Hajiya tawuce daki tama Musty da Anty Binta alamun su biyota daki, zama duk sukayi Anty Binta tace "Hajiya menene"? Ahankali Hajiya tace "anya auren nan dana yarda akama Imrana namai adalci kuwa? Nasan wannan matsalan na Imrana tun bayan rasuwan Maimuna amman bantaba ganin yanda yake ciwon da idanuna ba sai yau kunsan har yayi yagama babu wanda zai sashi a ido sai likitanshi yauda naganshi jikina yay sanyi" shiru duk sukayi saikuma chan Musty yace "Hajiya aure rahama ne kuma mata garkuwan mijinta ne, saiki iyaganin sanadin auren nan sanadin warakanshi kenan" shiru Hajiya tayi tana kara tuna condition dinshi tace "anya kuwa Musty zancen auren ne yatada ciwon nan fa, nidai barance komiba dan lamarin nan is complicated, abu daya dana nasani shine idan yaji bai iya zama da yarinyar nan zai sauwaka mata bazan hanashi ba idan kuma ya zauna da ita still duk daya all abinda nake cewa shine I will support Imrana dan Imrana is suffering fiyeda tunaninku, My son is suffering" cikeda kulewa dakuma damuwa Anty Binta tace "koma wanene wannan mutumin dayama Ya Imran abin nan wlh wlh bazamu yafemai ba zaisan yataba bawan Allah, tayaya ma Ya zai zauna da wacce ko Kausar dinshi ta girmeta ni kawai sabida tashin hankalin nan yasa nai shiru amman idansu Ya Abdul police suka kamo yaron dazaran yayi confessing agaban duniya ya wankesu Ya Imran

kawai ya saketa tunda baison Auren abarshi meyake nema? Yanada yara yanada sanaa yanada family Hajiya, Muna kadai yakeso and he will love her har karshen rayuwanshi, mubar Ya Imran yay kome yakeso Auren nan is nothing but a trash…….” wani kallon da Musty yamata yasa tai shiru da maganan yakalli Hajiya yace “Hajiya kuyi taking komi easy nasan kun damu da Imran, yanzu an gama saka furnitures adakin da yarinyar zata zauna?” Kallon Anty Binta Hajiya tayi tace “angama aikin?” Tabe baki tayi tace “oho ni banduba ba kaima Husby saikace auren soyayay ne dakawani bada kwangilan saka sabbin furnitures adakin kaman wanda suke dakin basuyiba” hararanta yayi yatashi yace “bari naduba dakaina” sama yawuce wani daki wanda dagashi sai kwanan lungun dakin Abee yaje bude dakin yayi dakin yay kyau anmishi wani babypink fenti sannan ansaka wani farin gado mai bala’in kyau, ga carpet akasa ga komi da komi, kusanshine yay komi da kudinshi dan Imran deserve more kome yamai bai biyashi ba aduniyan nan maida kofan yayi yarufe sannan yakalli lungun dakin Abee saikawai yajuya, fita yayi waje yadauki wayanshi yakira Anty Binta sannan yashiga bayan mota yazauna fitowa tayi sanye da mayafi tazo wajen motan bude baya tayi tashiga tana kallon fuskanshi ganin bacinrai karara akai, kai tsaye yace “are you trying kisa Hajiya ta tsani yarinyar da she’s not to be blame for anything daya faru ko itama kinzaci tanason auren ne? Kinsan hakkokinta nawa aka tauye Fatima? Explain your behavior to me?” Shiru tayi tana kallonshi saikuma ahankali hawaye yazubo daga idanunta da sauri ta sharesu tace “kayakuri Husby nasan ban kyauta ba, wlh ko nasan yarinyar is not to be blame for anything kawai I can’t help it ne some part of me nacemin duk ita taja inda at the first place bataje bayin maza ba itada Ya Imran bazasuyi wannan clash dinba, sannan inda badan aurenta ba PTSD Ya Imran bazai tashi yau 4days kenan ko 5 nema dukanmu bamu sashi a ido ba baci basha ba fita,duk ciwon dazai hana Ya Imran fita masallaci ai kasan babba ne, jibi yaranshi yanda sukai zuru zuru Abdallah yayi missing test a school yaron dake medicine sabida all this things, look at Hajiya, look at us kanninshi kowa ya susuce kaman bamuba kowa lost his happiness, I can’t help it but to blame her for everything dudda nasan non of it is her fault I am sorry Husby” bakaramin tausayi tabashi ba ganin yanda take kuka jawota jikinshi yayi ta kankameshi yana bubbuga mata abaya murya chan kasa yace “I know non of this makes sense nasani, but I want you kizama kaman ni duk wani hard situation dakika sami kanki arayuwa think of the positive things that could come out of it, yanzu idan aka wayi gari Auren nan resulted to something meaningful fa mezamuce? Imran yazo yana sonta morethan the way yaso Muna ma” dagokanta Anty Binta tayi daga jikinshi takalleshi kallon irin anya, murmushi yamata yace “yes baby is very very possible, I am a man loneliness is not good for anyman, kinzaci yanda Muna ta mutu feelings din Ya Imran sunbita sun mutu sun tafi ne? No wife basu tafiba, Ya Imran is suffering nasan bai kamata ina gayamiki this ba danke kanwarshi ce but I think you need to know dan kece elder idan su Sajida sukaga bakison yarinyar kina kyaranta suma haka zasu dingayi, abinda yakamata muyi nidake is muzama team and help Imran batare da yasani ba let’s make them come closer, let’s unite them batare dasu kansu sunsan they’re getting closer ba, bakisan kirki da Imani dakuma kyautatawan Yayanki bane yasa Allah yamishi kyautan fresh yarinya rana tsaka ba, is it easy mutum mai shekarunshi yasami danyan yarinya jagab haka shekara 19 bakisan irinsu ne sukafi shiga zuciyan babba tashi dayaba? Yanzu idan ya auri bazawara ko wata mai shekaru haka is not like I am saying bazai sotaba no zai sota but time phase dazai dauka to fall in love with yarinya karama will be faster than time phase dazai dauka to fall in love with Babba mai shekaru, budurwa of 19 are

sweet charming an shiga rai” turobaki tayi tace “wannan daka dage kanamin wannan bayanin hope ba shiri kake kamin kishiya da yarinya Yar 19yrs ba” wani dariya maganan ta yabashi baisan lokacin da yay Yar dariya ba yace “mata da kishi Allah dai ya yayemuku yanzu dai kingane what I am saying, I want us to be team both not team your brother kadai” murmushi tamai ta rungumeshi tace “thank you Husby for enlightening me, na amince and I am ready to support you and make things work daga yanzu nadawo team both” murmushi yamata yace “da this weekend zamu koma gidanmu an gama fentin but for this our mission nakara miki one week” dariya tayi sosai tana murna yace “muje kiga gidan daganan ma nadanyi kin gane ai” Ya kashe mata ido daya” dariya tayi tafito suka koma gaba suka bar gidan.

Asabar!
Karfe 4:30 yabude kofanshi yafito yana sanye dawata white jallabiya dayasha karin guga yasaka hula fara sai wani kalan kamshi yake mai kwantarda hankali, bakaramin kyau yayi ba saida kana kallon kwayar idanunshi zakaga yadan fada sosai yarame, direct dakin Hamza yashiga bubbuga bakin gadonshi yayi Hamza yabude idanu ahankali ganin Ya Imran har sake goge idanu yayi zaiyi ihu yatuna maganan Dr, “bazaka tashi bane” Abee yay maganan ahankali murmushi yayi ranshi fess yatashi da sauri yace “natashi Yaya Imran” ficewa Abee yayi daga dakin yashiga dakin Abdallah dake bacci Abdallah daya bude ido yaga mahaifinshi saura kadan yafada jikinshi yadaure baiyiba yatashi yawuce bayi yana murmushi kaman anmai kyautan dream car nashi c300, dakin Kausar yawuce ya kunna wuta yana kallon yanda ta kudundune abargo dakinta kaman fridge AC yafara kashewa sannan yabubbuga gadon yana karbe bargon hakan yasa tabude idanunta ganin Abee dawani kalan sauri ta mike tsaye daga gadon kawai tafada jikinshi dan lumshe ido Abee yayi yabubbuga bayanta, sakinshi tayi tana murmushi tace “Abee sorry na rungumeka banyi wanka ba mafarki nayi na rungumeka saisa ina ganinka nayi” hancinta yaja yace “talkative” washe mai baki tayi yajuya yafice daga dakin kap yatada sister nashi duk wanda yaganshi saikaga smile of happiness akanshi sauka kasa yayi zuwa dakin Hajiya dayaga wutan a kunne ganinshi batasan lokacin data shafe addu’an datake ba tace “zaku wuce masallacin”? Gyadamata kai yayi yace “eh Hajiya” murmushi tayi tace “incedai wannan mayen baccin Hamza yatashi” dan murmushi yayi yace “yatashi” daidai nan daga waje Hanza yace “to natashi Hajiya kuma naji abinda kikace” murmushi yayi yafito daga dakin Hajiyan suka fice Hajiya tadaga hannu tareda godema Allah daya fito yau dakanshi.

Hi GGM, did you know just because you act different baya nufin kai mahaukaci ne, sometimes is just PTSD! Now check on your family members and share ❤️
EPISODE 1️⃣6️⃣

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;

https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Wuraren 8 yashigo gidan na safe sabida yanda Baba Liman ya tsaidashi sunyi maganganu masu tsawo, da sallama yabude kofan falo yashigo ganin Musty, Harun da Abdul police a tsakar falon kan lallausan carpet suna breakfast da waina yaji man shanu da farfesu, ganinshi yasa da hannu Musty yace “zo wlh saura kadan su Abdul su cinye maka wainar ka” dan murmushi yayi ga mamakinsu tahowa yayi yazauna kusada Musty cikinsu yadauki spoon yafaracin wainar dasu babu wanda hakan baimai dadi ba, sosai yaci abincin kodan baici abinci yau kwana nawa bane oho saida yaji yakoshi sannan yatashi daga wajen dauke da mug na coffee Hajiya sai farinciki take sabida yanda taga yaci sosai, laptop Abdul yaciro daga jaka yakunna yaduba wani abu saikuma yarufe yatashi zuwa gaban TV yace “BBC sun fara sanarwan kuyi shiru muji” BBC suna sanarwa cewa wani ma’aikaccen company shi yahadamai wannan shairin sabida bai bashi miliyan dari ba dakuma takardun company tareda saka hotonshi a tashin kan cewa duk wanda yaganshi hukuma na neman yaron, saikuma nabiyu Alhaji Imran mijin yarinya da ake cewa yay fasikanci da itane ga shaidanan daga iyayensu nan aka fara nuno su Baba dasu Hajiya suna cewa ma’aurata ne, sannan video edit ne su kansu tashar BBC sun tabbatar da hakan sabida ma’aikatansu dasuka tabbatar dahakan, saikuma na karshe suna kirada Al unmma sudaina yada karya idan kunne yaji gangan jiki ya tsira shikuma wannan gayen duk inda yashiga hukuma zasu bishi har wajen akamoshi” adaidai nan news din yakare, yan dakin kowa yashiga cewa Alhamdulillah Alhamdulillah, kurban shayin Abee yayi ahankali su Musty suka shiga janshi da hira sai wajajen 11 yatashi dan yaje ya kwanta, sama yawuce ganin Anty Binta nafitowa daga wani dakin da dagashi sai corridor shiga dakinshi rikeda kaskon turaren wuta bamata lurada shi ba saida tajuyo ganinshi yasa tace “Yaya ina kwana” Gyadamata kai yayi batare daya amsa ba hakan yasa tawuce ahankali yakarasa gaban dakin harzai wuce saikuma yadawo kaman baiso yamika hannunshi yabude kofar dakin, gidansu nada bala’in kyau bana wasaba but dudda haka dakin nan standout agidan gabaki daya yakai kusan 2min tsaye gaban dakin yana kallon cikin dakin batare daya shiga ciki ba saikuma yajawo kofan yamaida yarufe yawuce dakinshi.
*****

Yanda Lujain kejin jikinta ita kanta har mamaki take maganin shawaran kesata jin haka, gashi Gwaggo kullum saita mata dilka ta gurgurza mata jiki hakan yasa fatarta yawani kalan kara kyau dudda tanada fata mai kyau, jikinta yakara wani kalan lumu lumu dawani extra taushi daman yawanci masu kiba nada taushin fata barin ita da fatarta is ultra soft yanzu saiyazama wani extremely soft.
Yauma kaman kullum daga ita sai wani pink towel data daura akirji an tsife nata kalaban dake kanta da alamu ma an wanke gashin sabida yanda bakin keta uban shinning gashinta is so silky

and coily ga tsayi an mata parking nashi dawani blue ribbon mai kyau anyi donut da bakin gadhin, tana zaune a tsakar gida kan tabarma kusada Gwaggo dake tankade wani gari hannunta manya manyan chocholate ne guda biyu tanaci tana kallon yanda Gwaggo ke tankaden, dan juyowa Gwaggo tayi takalleta tace “mekike kallona nan nan dazan fita babu yanda banyi dakeba muje tare kinki fita akanme zaki dinga tsoron fita, rabon dakimaje jikin gate kibude ki leka waje harna manta, nace babu abinda mutane zasu miki dazun baki tashiba BBC sun saka sanarwan an wanke ku tass to mezai faru, koma ba’a wanke kiba akwai wanda ya isa yamiki kallon banza ne ina taredake eh”? Dan turobaki tayi tace “Ya Samira fa tanunamini Gwaggo wlh muryana ne sarai ni bansan ya akayi yay tsawon nan ba” hawaye ne yacika idanunta, murya chan kasa tace “kowa yanzu har yan islamiyyan mu kallon Yar iska sukemini koni banmantaba tayaya wayanda suka kalla zasu manta wlh kaman in mut…..” buge mata baki Gwaggo tayi tace “wlh kika karasa fadin kalman nan saina dokeki wawiyar yarinya kawai asalin yan iskan duniya masu fasikancin na rayuwansu suke abinsu ba saike dabaki komiba duk kinbi kin dami kanki duk jibi yanda kika fada kalli wuyanki har yau idanunki basu koma daidai ba sabida kuka” tashi dagakan tabarman Lujain tayi da gudu tashige dakinsu tana kuka Gwaggo tabita da harara tace “aisaiki tayi bakida damuwa ne yarinya tunda inasa kudina ina sayamiki kayan kwalama ubanki nasaya miki ne” Gwaggo tai tsaki tacigaba da tankaden datakeyi Gwaggo tacigaba da masifa tace “yarinya sabida ita yau kwana nawa kenan ban samu nahuta ba amman ta isheni Alhamdulillah yau zanyi bacci nai munshari wahalar ki kuma saidai takoma kan mijinki Imrana nahuta” Gwaggo takarashe maganan ahankali sabida tunda ta tasa rigiman batason auren Gwaggo ta zuzxuba mata karya bata sake mata maganan ba ko anjima akazo kaita da ubanta zata barta ai bata isa tama Babanta wannan haukan da shirmen ba tuni zai karairayata yabama karnuka kashin itane dai data raina takema yan abubuwa, jin kukan yay yawa yasa Gwaggo takasa daurewa dan jin kukan Lujain take har cikin jinin zuciyarta kakkabe hannunta tayi tawuce dakin.

Anayin mangariba Gwaggo takirawo su Samira dukansu kuskus sukayi nadan tsawon lokaci kafin su shiga falon Gwaggon inda Lujain take a zaune tana shan tea, ganin Samira rikeda dawani babban jaka yasa Lujain ta tashi da sauri tace “Ya Samira baby yakawo miki wani abu ne”? Daure fuska Samira tayi tace “banace kidaina kiramin saurayi da sunan danake kiranki ba” dan murmushi tayi mai bala’in kyau tace “to yakuri menene amman ajakan” jakan tabata tace “Baba yace mukawo miki ki shirya bayan isha’i yana nemanki” zaro idanu tayi takalli towel din jikinta tace “Kodai yaganni da towel ne saida ya aikomin da kaya na shiga uku” tai maganan tana fizge jakan dasauri tai uwardaka zata fara farke ledan Samira tashigo tace “Malama jeki wanka” daga falo Gwaggo tai ihu tace “da ruwan maganin nan zaki wanka” wucewa bayi tayi itakuma Samira ta zauna abakin gado tana bude jakan wani simple lafaya lace ne mai kyau red and gold, sai Yar cikinta, sai set na dankunne da sarka na zirconia mai kyau shima sai flat shoe na Zara kayan dai gabaki daya akalla Baba yakashe 35k fitowa tayi tana zaro idanu tana kallon kayan tace “laaaa harda sarka da takalmi anya ni Baba yace akawo mawa kuwa saikace zanje biki” tabe baki Samira tayi tace “idan kinje ki tambayeshi nidai Malama kidauko pant da bra kisaka kizo kisa kayan” tsayawa tayi jimm kaman mai tunani Samira tace “kuma kima kanki fada kidaina daura towel akirji kina zama koda yaushe nonon ki duk zasu zube ne” dan yatsine fuska

Lujain tayi tace “Ya Samira ni damuna suke wlh na tsani saka bra da pant, pant na cimini cinya” tsakani ga Allah tai maganan, Ya Samira tace “kiba yasa suke cimiki jiki, ciye ciye yamiki yawa babu namijin dazai soki idan kina haka cus yawan kiba  is disgusting” tsayawa tayi tana kallon Ya Samira saikuma tajuya mata baya tasauke towel din ta daura a waist zata fara saka bra, saida tasaka bra din tajuyo tace “saisa su Ya Abida basa sona sabida inada kiba I am disgusting” tsayawa kallonta Ya Samira tayi this is the first time take ganin jikin Lujain haka dudda she’s putting on bra tanada very nice fat boobs gasu a tsaye, inda ace batada kiban nan bakaraman Cinderella za’ayi ba anan gwarama da aka mata Auren nan dan nan gaba kar samarinsu suzo suna ganinta sudinga cewa Lujain takeso, ganin yanda Ya Samira ke kallonta yasa dawani kalan sauri takai hannunta takare kirjinta tace “mehaka Ya Samira”? Tsaki Samira taja tace “Malama kizo kisa kayan nan angayamiki ke nake kallo ni I am lost in my thought ne mezan gani anan da banda shi” karasa saka pant Lujain tayi tazo Ya Samira tashiga shiryata bata mata kwalliya ko dayaba kawai lafayan tasaka da dankunne da sarkan ta tayafamata lafayan akai sai Lujain tayi kaman ba itaba ita kanta Samira saida tace “dayake duk wanda yasanki da towel yasanki inbadai kayan makaranta kika saka ba yau sai kikayi kaman ba kanwata Lujain ba,   bakiyi kaman Lulu Gwaggo ba daikika fito tsaf Lujainnnn, kidinga saka kaya kinga yanda kikai kyau ne” kallon kanta Lujain tayi amadubi wani kalan murmushi tayi tace “wlh nai kyau amman kinga harsun soma damuna kayan kaman na kwabe su cizona suke” Ya Samira tace “ki kwabesu Baba ya kwabe ki” kyalkyacewa da dariya Lujain tayi sosai hakan yasa Gwaggo ta daga labulen uwar dakan taleko tace “chakulkuli kike mata ne datake dariya hak……” kasa karasa maganan Gwaggo tayi ganin yanda Lujain tayi kyau, Gwaggo batasan lokacin data yafito su Abida ba tace “kuzo kuga kanwarku” dasauri suma duk sukazo kallonta suka shigayi Lujain sai dariya take tace “nai kyau ko Gwaggo na”? Washe baki Gwaggo tayi tace “kaman hurun ini Lulu ta” tabe baki Abida tayi takoma tazauna Habiba tace “kidinga sa kaya haka jibeki saikika fito kaman mai hankali” hararanta Lujain tayi zatai magana Gwaggo tace “barta da halinta yi maza kiyi isha’i gashichan an sallame a masallaci yanzun nan Babanki zai kiraki” gyadama Gwaggo kai tayi tahau kan dadduma Gwaggo tasaki labulen taja su Abida kitchen tabasu manya manyan jakunkunan da Allah kadai yasan meta hadama Lujain aciki tace “su wuce sukai motan Baba” kaiwa sukayi suka dawo Abida tace “Baba yace kije waje” gyadamusu kai Lujain data tashi daga kan dadduma tayi zata saka slippers Gwaggo tace “saka takalmin da Baban naki Ya Aiko miki mana” sakawa tayi dan kuttubin kafanta yay kyau tayi da cute white feet nata da long long nails dinnan kaman kasa abakinka kaitasha, tana murmushi tawuce tafita lullubin lafayan na zamewa baya kyakkywan gashinta Ya bayyana gate tabude tafita, Baba tagani da Baffan ta guda biyu awajen tsaye jikin mota dukansu tsayawa kallonta sukayi ahankali tace “ina yininku” amsa mata sukayi Baba yazo gabanta ahankali yadaga hannunshi yajawo Dan kwalin lafayanta gaba sannan yakama hannunta zuwa bayan motan yasata aciki Baffa Abdullhadi yashiga maxaunin direba yusuf Ya zauna agaba Baba Ya zauna abaya kusada ita sannan aka tada motar.

Murmushi tayi takalli hanya tace “Baba ina zamu”? Anatse Baba yace “gidan mijinki zamu kaiki!”.

EPISODE1️⃣7️⃣

Jama'a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Don't miss this book for anything dan yanzu aka fara💃💃

Wani kalan faduwa da gabanta yayi  saida taji kanta yasara dum, hannunta Baba yakama yace "namiki laifi da dama Lujain tun kina Yar kankanuwan ki, lokacin banda courage na kallonki ne sabida banda abinda zan kuladake, wannan auren ma bawai dan Gwaggo tadage akai yasa na yarda ba is because that's the only right thing I can do for u, dakina karama I couldn't do anything but yanzu I can do anything to protect you, your image, I can do anything dan inga society ya girmamaki, yakuma darajaki, nasan bakisan mutumin nan ba shima baisanki ba but abu daya dana sani shine bazai cutarmini dake ba dan shima yanada kamarki kokuma nace wacce tafiki agida, he's a father so he can handle you, munyi bincike akanshi shaida daya bamu samu akanshi na cewa mutumin banza bane dan haka inaso ki zama mai tsoron Allah ki manta da komi kicigaba da rayuwanki amatsayin matarshi kinji" wani kalan kukane taji yana tasomata amman kotari takasa tana tsoron Baba dako gardama batayi agabanshi Baba nada dukan yara yasha dukanta dasu Samira ita kuma babu abinda take tsoro kaman duka yanzu wayau Gwaggo dama tamata dasu Ya Samira, sai alokacin hawaye yazubo mata dasauri takai hannunta ta share, amman ina bini bini saisu zubo ta share sunyi tafiya mai nisa sosan gaske sannan sukakai wani mahaukacin estate dinsu bude musu gate akayi dan ansan da zuwansu har gidansu Abee gateman yabude musu gate suka shiga yamaida gate yarufe yatafi ciki da gudu duk suna zaune cikin motan Musty yafito shida Harun duk suna sanye da manyan kaya sai Anty Binta da Matar Harun mai suna Amina sunci atampopi masu kyau sunsha aiki kana ganinsu kama hadaddun mata masu kudi, bude mota su Baba sukayi sannan Baba yasa hannu yafito da Lujain daga cikin mota, gently tasauke kafarta akan interlock na compund din wani kalan sanyi taji yashigeta kaman zata sandare dan har hanjinta taji sanyin, ahankali Baba yaja hannunta tsayawa tayi kikam dayasa Baba yajuyo yakalleta wani kalan fashewa tayi da kuka tana girgizama Baba kai dan sai yanzu ta yarda wani wuri fa yakawota tace "dan Allah Baba karka kaini wlh bansan su ba, Baba baran kara rashinji ba, ban kara zama ba dan kwali, ban

kara zama da towel, ban kara aran wayan Ya Samira wlh Baba zanmabar wajen Gwaggo nadawo kwana adaki dasu Ya Samira amman dan Allah kada ka kaini ko'ina mukoma gidanmu" Shi kanshi Baba sanyi jikinshi yayi baitaba kawowa cewa Lujain ce zata fara aure acikin duka yaranshi ba, amman yadaure yay ta maza wani mugun kallo yamata yace "let's go my friend banson shirme" kafafuwanta har girgidi suke kaman maijin fitsari tabishi kanta akasa tana kuka sosai duksu Anty Binta dasuke dan nesa dasu na kallonsu afuskansu kadai zaka gane suma jikinsu yay sanyi jin maganganun Lujain, karasawa gabansu su Baba sukayi da fara'a aka gaisa sannan sukace bismillan ku, Baba na rikeda ita suka shiga falon sake tirjewa tayi ajikin kofa ganin mutane afalon cike kowa kuma su ake kallo, Hajiya da duka yaranta, sai Abdallah Kausar da matan Ibro sai Abee dake zaune kan 3 sitter da Hajiya ke zaune kai dan anan ta umurce shi da zama yana sanye da shadda anmai dinkin jumper da hula akanshi yay wani kalan kyau kaman kasace shi  kanshi na kasa dan shi kadaine adakin wanda ba kofan yake kallo ba, ganin mutane na kallonsu gashi ta turjemai yasa Baba yajata da karfi but karfin dat is not obvious shigowa Anty Binta da Amina sukayi suna ayiririririiiii kujerun dakenan empty su Baba suka zauna da Lujain na kusadashi kanta akasa tana kuka sosai, cikeda dattaku Hajiya tai murmushi tace "barkan ku da zuwa ah'ah amaryan tamu mai kuka ce kodai Alhaji kun tsunguleta a hanyan zuwa ne" dan murmushi Baba yayi yace "munsameku lafiya Hajiya" murmushi tayi tace "lafiya lau" cikeda dabara ta taba kafan Abee hakan yasa anatse yadago kanshi yakalli Baba ahankali yace "ina yini" murmushi Baba yayi shima yace "Alhamdulillah Imrana" kayan ciye ciye aka shiga cika gabansu dashi murmushi Baba yayi yace "Alhamdulillah sassannunku da aiki an gode Allah amfana" mikewa tsaye yayi ahankali sannan yakama hannun Lujain da kanta ke kasa tana kuka har lokacin yadagata yaja hannunta tana biyeda shi Dan murmushi Hajiya tayi tamike tsaye ahankali tareda komawa gefe, gently Baba yazaunar da Lujain kusada Abee kuka take ita bama gani takeba balle tasan meke faruwa hannunta da Baba kerike dashi yadauka yakama na Abee da kanshi ke kasa yasa aciki dudda kukan da Lujain take but she was able to understand hannunta baya cikin na Baba kuma, wani kalan warm serene cold taji akan hannun Abee dake shiga cikin fatar hannunta, matse hannun Abee Baba yayi kan nata hakan yasa Abee yarike hannunta gam addu'a Baba yatofa a hannayen nasu biyu da duka Ya rirrike yahada sannan yakalli fuskan Imran dake kasa ahankali yace "Imrana" gently Abee yadago idanunshi yadaura akan na Baba, ajiyan zuciya Baba yasauke dan Abee nada wani kalan kwarjini da charisma da idan yakalleka dole kagani yace "ga diyata nan Lujain nabaka ita amana, bansanka ba amman na yarda dakai zuciyata ta aminta dakai sama da yanda kake tunani, karikemini ita amana daga yanzu rayuwanta komi nata na hannunta ne banda iko akanta saikai karike amana kaji Imran" Abee jiyayi kanshi yamai nauyi ganin yanda Abee ke kallonshi amsa yake jira yasa ya gyadamai kai batare dayay magana ba dan baijin zai iya magana ba, sakesu Baba yayi yatashi yajuya yakalli Hajiya hannunshi yahade yace "Hajiya ke mahaifiyar muce nan gabaki daya ga diyata nan nakawo muku marainiya ce tun kafin a haifeta mahaifiyarta tarasu, a hannun mahaifiyata ta girma takuma tashi, Lujain goyon kakace, nasan zakuga abubuwa da dama na shirme da rashin wayau dakuma  rawan kai ina rokonki da idan batai daidai ba ki tsawata mata dan kin isa ne, sannan ku dorata akan hanya mai kyau, Alhamdulillah nazo na ganku duka naji dadi hankalina ya kwanta dan Lujain tabar family tane tazo tasami even a bigger family dan haka kurikemini amana nan ta, tunda take aduniya yaune rana na farko da barata kwana tareda kakarta ba kokuma agidansu ba ko tafiya bata tabayiba, dan Allah kuyi hakuri da ita sannan ku

dorata kan hanya madaidaiciya” wani kalan kuka Lujain take tafara kokarin cire hannunta daga nacikin Abee kallon hannun nata dake cikin nashi Abee yayi saikuma yadauke kai batare daya saketa ba dayaji takeson yayiba, ahankali Hajiya tace “na dauki amana in sha Allah bazamu cutar da Lujain ba namaka wannan alkawarin” murmushi Baba yayi yace “to mungode mungode bari mukoma gida saida safen ku” cikeda girmamawa Hajiya tace “Muma mungode saida safe agaida kowa da kowa” tashi su Baffa sukayi Baba yajuya shima zai tafi jin da gaske Baba tafiya zaiyi yabarta agidan nan wani kalan fizge hannunta Lujain tayi daga cikin na Abee ta tashi da gudu ta kankame Baba tabaya tana kuka sosai har gyalenta na zamewa kasa lafiyayen gashinta da aka kama da ribbon mai kyau ya bayyana cikin kuka sosai tace “Baba dan Allah dan Allah kada katafi ka barni wlh ban sansu ba, wlh kuwa” bata damu da da karfi take maganan ba tarike Baba gam cikin kuka tace “Baba wlh baran kara maka barna ba, Baba nace baran kara aran wayan Ya Samira ba saika siyamini tawa Baba dan Allah kada kabarni anan” tahowa su Baffa sukayi ganin yanda ta rirrike Baba tabaya yakasa motsi kaman zata karyashi Baffa Hadi yace “ke cikashi” cikin kuka ta makemai kafada tace “dani zaku tafi Baffa” Musty daduk suke kallon drama yay murmushi yakalli Anty Binta da Amina hakan yasa suka taho wajen Anty Amina tace “yakuri Lujain ki barsu sutafi” wani kalan ihu tabuga da saida yasa for the first time Abee yadago kanshi yadaura akanta, dudda he’s not seeing her face directly but yaga yanda goshinta har zufa yake ketowa kuka harda majina ga gashinta da aka gyara tsabagen yanda take jujjuyar da fuska abayan Baba harya hargitse babu lallashin duniya da Anty Binta da Amina basuyiba har Hajiya tasa baki ina taki sakin Baba da Baba ta kular dashi wani kalan tsawa yadaka mata Lujain! Yanda taji saukan tsawan saida ta sakeshi tai tangal tangal tama fadi akasan tiles na wajen jikinta narawa sosai tana girgizama Baba kai, kowa na falon su yake kallo jin yanda Baba yadaka mata tsawa, kaman Baba zai daketa yace “stand up go back to your sit ki zauna” juyawa tayi da sauri tana rarrafe ta tashi yanda ta tashi takoma tazauna zaka dauka mala’ikan mutuwa tagani, tahowa Baba yayi azuciye batasan lokacin datai pulling hannun Abee ta kama hannun Abee gamgam ba ta boye fuskanta akafadanshi kaman zata shide tace “Baba dan Allah kayakuri karka dokeni” yanda jikinta ke bari da yanda take numfashi kaman zata shide Abee could hear it, yanda tarike hannun Abee gam tana boye fuskanta abayanshi Musty yakalla daidai itama Anty Binta takalleshi kashe mata idanu yayi tayi murmushi Baba zaiyi magana Hajiya tace “aaaa ina ake haka Alhaji? Har gidana zakazo ka firgitamin diya sabida tayi kuka kan katafi da ita bata sanmu ba yo ai batai karyaba babu wanda tasani anan, kataba ganin inda aka rabu da amarya lafiya dama ai sai sunyi yan koke koken nan, karma kafadi abinda kakeson fadi dan nasan fada zaka mata” dan murmushi Baba yayi akunyace yace “shikenan to Hajiya saida safen ku” anatse kowa yace “Allah bamu alkhairi” fita sukayi hakan yasa ahankali tasaki hannun Abee sannan takoma gefe takifa kanta akafa tana kuka sosai tashi Abee yayi yawuce sama Hajiya tabishi da kallo tashi Kausar itama tayi tawuce fuuuu sama ahankali Hajiya tazauna kan kujeran daidai nan mai gadi yashigo dawasu jakunkuna manya guda biyu yace “Hajiya ina za’a saka wayan nan” Hamza ta kalla tace “jeka kaimata dakinta” gyadama Mamanshi kai kawai yayi yawuce sama ahankali Hajiya takai hannunta tadaura saman bayan Lujain cikeda lallashi yace “kiyakuri kowace mace saitaji irin abin nan dakikeji idan aka kawota gidan mijinta, amman zakigani nan da sati kin warware kin daina tunanin gida ko” ta tambayi su Anty Binta dake tsaye akansu sukace “hakane” murmushi Hajiya tayi tace “ku kaita dakinta Binta” Gyadamata kai Binta tayi dagata itada Amina sukayi

suka wuce da ita sama Mama takalli su Sajida da Zainab tace “ku kai abinci dakinta dan ba lallai taci abinci ba” dan tabe baki sukayi saikuma suka tashi itadai Maman Aneesa na zaune tana magana da yaran tace “Aneesarh takarasa maganin ta” gyadama Hajiya kai tayi takalli Abdallah dayay shiru tace “kaikuma fa dakai shiru haka”? Dan murmushi yayi yace “bakomi ni zuwa zanyi ma na kwanta inada lectures gobe” Maman Aneesarh tace “dole abama Abdallah award din shine mai fara zuwa ya kwanta agidan nan kafin kowa” murmushi yayi yawuce abinshi.
EPISODE 1️⃣8️⃣

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Zaunarda ita Anty Binta tayi akan gado itada Amina sosai take kuka tana kwabe baki kaman yanda yara ke kuka Anty Binta dake kallonta da yanda takeyi kawai fadomata maganan mijinta yadingayi a zuciya she looks so cute, cute sosai yanda takeyi gashi yanda takeda kiba da yaran kumatunta keyi yayi soo adorable kaman kasaceta kagudu she looks kaman Yar baby Yar yarinya hakanan kawai taji Allah yasanya mata son yarinyar azuciya and idan Abee zaizo yasota she will be so soo happy wlh, zama Anty Binta tayi kusada ita tace “dan Allah ya isa hakanan Lujain kiyakuri” makema Anty Binta kafada tayi tana tabe baki cikin kuka tace “ni gidanmu zani wajen Gwaggo na” murmushi dukansu biyun sukayi Amina tace “to yanzu kidaina kuka kinga tunda babanki yayi fushi yanzu baraki iya komawa ba kibari gobe saimu maidaki gida” rage kukan tasomayi tana kallon Amina dake magana ahankali tace “da gaske zaku kaini wajen Gwaggo na gobe”? Gyadamata kai daga Amina har Anty Binta sukayi atare daidai su Sajida da Zainab na shigowa da kulolin abinci da tray na drinks suka bita da kallo kaman yanda itama ke kallonsu still hawaye nafita daga idanunta amman ba kuka takeba gashin idanunta sun jike sharkab, suna ijiyewa suka fita Anty Binta tace “zakici abinci? Ga abincin ki nan ankawo miki” murya chan kasa tanabin abincin da kallo tace “tea zansha da bread” tashi Anty Binta tayi tace “bari naje nakawo miki” daidai lokacin Sajida tashigo da flask da gwangwanin madara da Milo da chokali da karamin mug da bread Anty Binta tace “yauwa ga kayan tea nan bari nahada miki” karba tayi Sajida tawuce tafita Anty Binta nan da nan tahada mata tea akaramin cup tadaura akaramin tray takawo mata saman gado tabata karba tayi ahankali tana kallon fuskan Anty Binta saikuma takalli tea yanda yake tururi Anty Binta tace “oohh zafi bakishan tea

tafashashe haka”? Gyadamata kai tayi ahankali hakan yasa Anty Binta tashiga juya tea ahankali take sauke ijiyan zuciyan kuka saida Anty Binta ta dandana tea jin zata iyasha yasa tamika mata karba tayi takai bakinta ta dandana jitayi yafi na Gwaggo dadi kaman bada milon da aka sabayi aka mata anan ba bread din Anty Binta ta dauka tana kokarin budewa taciro mata slice Lujain tamika mata cup din ahankali tace “Anty akaramin” daga Anty Binta har Amina kallonta sukayi ayanda kadai yarinyar take orobo Masha Allah sunsan bakaramin abinci takeci ba da murmushi Anty Binta tamata shima tasha tareda bread cup uku tasha na tea sannan tace takoshi yunkurin sauka tafara daga kan gadon har lokacin bata daina ijiyan zuciya na kuka ba Anty Binta tace “ina zaki”? Kaman zatai kuka tace “wanka zanyi kayan nan na cizona” wanan karan Amina saida dariya ya kufce mata Anty Binta kuma ta murmusa tace “to ga bathroom naki nan kije kiyi” gyadamusu kai tayi tawuce ciki duk suka bita da kallo suna kallon uban tulin gashinta kodan family su basuda gashine oho jitayi kaman ta deba ta sammata, tashi sukayi Amina ta tayata daukan flask din itakuma Anty Binta tadau cup da tray suka fitada shi suka rufo mata kofa, kowa har yashige dakinshi though bawai anyi bacci bane but babu wanda ke falo ijiye komi sukai a kitchen suka fito Hajiya suka gani tsaye gaban dakinta dake nan kasa tace “taci abincin kuwa”? Anty Binta tace “shayi kawai tasha Hajiya” kallon Amina Hajiya tayi tace “ke ina mijin naki” dariya tayi tace “wlh Hajiya ni baraki kadani natafi yauba kwana zanyi sai gobe zan koma” hararanta Hajiya tayi tace “ai shikenan, saida safenku” “saida safe Hajiya” har Hajiya tashiga daki saikuma tajuyo daidai sun zauna a falo zasu kunna kallo Hajiya tace “Binta” dasauri Binta tadaga kanta tace “naam Hajiya” cikeda damuwa tace “dan Allah kiduba mini Yar mutane kafin ku kwanta dan nasan Imrana ba dubata zaiyi ba” murmushi Anty Binta tayi tace “tom yanzu ma wanka tashiga Hajiya saisa muka dan zauna anan mubata wuri” gyadamusu kai tayi tawuce ciki dan ita bata jure hawa benen nan sabida kafafu saitafi wata bata haura sama ba.

Tadade tana kallon bayin komi daban da bayinsu dansu normal shower ne, kasa amfani da shower tayi, da kyar ta iya bude pampon shikuma ruwan sanyi ne aciki duk yanda zatai tayi takasa hakan yasa tabude wani sabon towel fari kal data gani abayin tadaura tafito tana tafiya ahankali tana kalle kalle dakin, bakin gadon taje tazauna ahankali dudda sunce zasu kaita gida gobe but hakanan taji wani sabon kuka yazomata data tuna auren da aka mata yasa take awan nan gidan dabatasan kowa ba, babu wani abu dake mata dadi aduniya, bata taba tunanin zatai aure yanzu ba ita dake ganin zabga zabgan yayunta agida basuyi aure ba, wai itane matan aure matan wani tayi kukan jin kanta na sarawa yasa ta tsagaita da kukan hakanan tareda jingina kanta da bangon gado wani kalan gyangyadi ne yafara dibanta har baccin yay nasaran kwasheta ahaka wuyanta ya bankare.

Ganin Shadaya har darabi yasa Anty Binta takashe kallon tace “zomuje mu duba Amarya saimu je mu kwanta” kashe wutan falon sukayi sukai sama, sallama sukayi jin shiru yasa Anty Binta tabude kofan ahankali zaune suka ganta daga ita sai towel babu dan kwali akanta wuyanta Ya karkace tana bacci awahale Amina tace “laaaaaa” gaban gadon Anty Amina tayi takira sunanta.

“Lujain, Lujain” amman shiru dan ita tanada nauyin bacci idanba itane ta tashi ba saikai da gaske zaka iya tadata, Anty Binta tace “ko kayan bacci bata sakaba baccin ya kwasheta” Amina tace “gajiya ne da uban kukan datashi gyaramata kwanciyan kawai” gyaramata kwanciya Anty Binta tayi hakan yasa tasake sauke ijiyan zuciyan kuka Anty Binta tadan kalleta sanan taja bargo tarufa mata tareda rage gudun AC dakin sannan takashe wutan dakin sukaja mata kofa sannan suka wuce dakinka.

“Don’t forget cinta, shanta, lafiyanta, suturanta her well-being is now on you, not any of your family members ko Hajiya, I know you saisa nake fadin hakan, it doesn’t matter ko kanason auren ko bakaso anriga an daura, make sure ka kiyaye hakkokin that girl Imran, she’s in that house because of you, so kaji tsoron Allah and remember Allah na yafe kowani laifi banda hakkin wani bazanzo kafara this phase at the wrong foot her” dan gajeren tsaki yayi gama karanta messege din da Musty yatura mai ijiye wayan yayi yana kallon magungunan shi dake gabanshi kwashesu yayi yaja drawer yazuba su all this while baya sha yanzu ma bazai faraba duk maganin sa bacci hakan zai taimakamai da migraine but no kusan 12 yakai yana aiki a desktop nashi komi anatse yakeyi sannan ya kashe komi yamike yawuce gado kwanciya yayi tareda addu’a yaja bargo dudda bayajin bacci but he’s trying to fall asleep.

Wuraren 3:00 cikin bacci tace “Yunwaa” ahankali tasake cewa “yunwaaaa” jin shiru yasa dakarfi tace “Gwaggo yunwaaaaaa” jin yanda dakinta ya amsa maganan sabida yanda tai dakarfi yasa tabude idanunta rasss ganin duhu still adakin babu hasken torchlight na Gwaggo yasa ta tuna bata gidansu yau, gadon datake kai tashiga tattabawa hartakai karshen gadon bataji alamun mutum akaiba wani kalan mugun tsorone yasauka akan zuciyanta tunda ta taso tai wayau yaune rana na farko datake ganinta adaki ita kadai bata kwana da kowaba she’s always with Gwaggo ga ko’ina tsit babu ko minshari irin na Gwaggo dake fadi wani kalan tsinkewa zuciyanta yashigayi ko za’a kasheta batasan ina switch yakeba dazata danna taga haske ba balle kuma waya, tashi tayi lips dinta har rawa suke ta jingina da bangon gado tana kwalalo idanu tana bin ko’ina da kallo gani tayi kaman akwai wasu abubuwa da yawa kan carpet na dakin hakan yasa ta kara Gwalalo idanu ganin abubuwan na motsi suna kusada ita yasa tawani kwala uban ihu tsakar daren nan. “Wayyooo Gwaggooo, Gwaggo kizo akwai aljanu agidan nan wlh gasunan Gwaggo suna tahowa kusadani, wayyooo Allah na nashiga uku na bani, Aljanuuuu” tai maganan takai hannunta tadaura akan idanunta ganin kaman kwara daya yahayo kan gadon nan daidai nan aka bude kofar dakinta tareda kunna wutan dakin hakan yasa haske ya gauraye dakin, Abee ne tsaye gaban dakin sanye dawata faran jallabiya batare daya rufe boturan wuyanba da alamu da sauri yafito dan mana iya hango kwantaccen gashin kirjinshi, ganin yanda take ihu tana kiramusu Gwaggo kaman zata tadamusu da gida sama sabida ihu yasa yace “Ke!”
EPISODE1️⃣9️⃣

Jama'a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI
Har tsakiyan kanta taji tsawan da aka daka mata dayasa lips dinta nawani irin bari tashiga bude idanunta kadan kadan tana kallon direction din da Abee yake tsaye kafin takarasa bude idanun rass sai alokacin wani kamshin turare mai bala'in dadi yadaki hancinta, dawani kalan sauri hartana neman faduwa akasa tai tsalle ta duro daga gadon tai wajen Abee daya dauke kai daga kallonta dasauri ganin abinda ke jikinta, dan nesa dashi ta tsaya tasaki kuka ahankali takai hannuwanta duka biyun kan idanunta tace "dan Allah ka kaini gida wajen Gwaggo na nan gidan akwai Aljanu gasuchan a tsakar dakin yan gajejjeru" tai maganan tana mai pointing da hannu tsakar dakin sannan tajuya jakunkunan ta guda biyu da Gwaggo ta bada akawomata tagani da kuloli guda uku na abincin da aka kawomata jiya dan zaro idanu tayi sannan gently tajuyo da kanta kaman mara gaskiya tadan kalli Abee daidai shima yazubamata nashi idanun wani kalan cika mata idanu yayi ahankali tasauke kanta kasa dasauri takai hannunta tana goge hawayen dasuka zubomata babu alamun wasa akan voice nashi yace "those things looks like Aljanu to you"? Girgizamai kai tayi ahankali tanajin muryanshi har cikin heart dinta, dan tsaki Abee yayi yajuya zai fita wani kalan fashewa da kuka tayi kaman jira take tabiyoshi da gudunta da sauri yajuyo jin tabiyoshi da gudu hakan yasa chak ta tsaya chak tasauke kanta akasa tana kuka, kallo yamata daga sama har kasa kaga idanunshi kaman zai daketa dasu yace "where do you think you are going"? Kasa magana tayi sai kukan datakeyi strictly yace "wuce ki koma cikin dakinki" ahankali kaman wacce idan tai magana da kyau zai make tace "I can't sleep alone" watsa mata harara yayi yace "amman kin iya zuwa bayin maza alone" dago jajayen rinanun idanunta tayi takalleshi hada idanu sukayi dasauri daga ita har shi kowa ya kauda kanshi shi kanshi baisan yama akayi yayi maganan ba he's just angry so many things acikin zuciyanshi, cikin dan murya azafafe yace "go back inside" shiga cikin dakin tayi dabaya dabaya takoma ciki tana kallonshi batare data kulle kofan ba, dan gajeren tsaki yakarayi yakai hannunshi yakama handle na kofan yajawo zai rufe karaf yaji tarike taleko da kanta ta ragowan space din dayarage ta kwawkwabe baki takalleshi idanunta sun cika da hawaye tam kaman ana ciremata rai tace "dan Allah dan Allah karka rufeni wlh tsoro nakeji, idan ka rufe ni zan mutu kaji I can't sleep alone pleaseeeee" dan kallon idanubta yayi kadan cikin wani kalan fushi Abee yabude kofan yashiga dakin da sauri takoma baya ganin yanda yashigo kaman zai daketa, azafafe yace "inda kinsan you can't sleep alone dabaki abinda kikayi ba, dabakije bayin maza kin rufe kanki kina kallon only God knows what ba with phone, ke bakison kwana ke kadai ni do you think I love this kaddararren auren nan da akamin dake? Do you think I want someone like you as my wife?

Do you think I will ever consider you my wife? Listen and listen well? Dagayau you will sleep alone and learn how to live and survive anan you did that to yourself not me understood? Kome kika sami kanki aciki ayau ke kikama kanki, I never wanted you, I didn't initiate this marraige, your family did, su suka miki so deal with it understood?" Gyadamai kai tayi dasauri tana hawa gado dukta daburce ta manne jikin gadon sosai ko'ina najikinta rawa yake sai gyadamai kai take kaman lizard alamun taji arayuwan nan bayan Baba sai wannan mutumin ne suka taba mata ihu da tsawa kuma sutafi tsoro yanzuma saitaji kaman tafi tsoron wannan kan Baba dan Baba kome zaiyi Gwaggo is always there to save her wannan ko babu wanda zaizo, shi kanshi Abee yanda yaga tanayi kawai saiyaji zuciyanshi ya tsinke tabashi tausayi baimasan mesa he vent his anger on her is just a mistake dako Kausar dinshi can make so why is he this bitter towards her? Did she even understand him? Why will he even waste anger nashi akan Yar yarinyar nan saikace yana fada da babba sa'anshi. Juyawa yayi yafice daga dakin dasauri tareda bangin kofan dakin kaman jira take sauka tayi daga gadon dasauri ahankali ta zauna akasa kusada kofan jitayi yunwan ma yabace dataga bala'i, sosai take kuka tanabin dakin da kallo kaman wani abu zai bayyana tagani haka takeji, maganganun dayamata sai yawo yake mata akai, for the first time bayan yay maganan sai itama taji mema yakaita tashiga bayin maza? Look abinda tama kanta yanzu? Wannan wani kalan rayuwa ne tashigo rana daya, idanunta kur har aka kira sallan farko na asuba tana matsar hawaye tananan awajen ta zauna ta kudundune kanta dan tiles ne wajen ba carpet ba ga sanyin kasa ga sanyin AC gashi daga ita sai towel wani kalan wahalallen bacci yay awon gaba da ita.

As usual 4:30 dot Abee yafito, wani ash color jallabiyane yanzu ajikinshi fuskanshi har wani haske yake na musamman sabida yawan sallan dare yana kamshi mai dadi dakin Hamza yashiga yatada shi, yashiga na Abdallah, sannan yafito yashiga yatada Kausar kafin yatada kannenshi su Anty Binta harzaiyi stairs Lujain tafadomai arai yanzu dai da gaske responsibility yakaru akanshi he can't believe it abin namai kaman he's dreaming, juyawa yayi kaman baiso yataka yawuce zuwa bakin kofanta hannunshi yadaga kaman baiso yayi yakai hannun kan kofa yay knocking kofar ahankali batare dayay magana ba jin shiru yasa yabude kofan kadan da fuskanta yafaracin karo dake lilo sabida yanda tai baccin awahale anan kusada kofa bayanta jingine da bango, idanunshi ne suka sauka kan hannunwanta data kankame jikinta dasu duk cikin bacci, tsigan jikinta sun tashi yirrr dazai nuna mugun sanyi takeji, almost 30sec yayi yana kallonta sannan yadaukekai shibaimasan ta yanda zai tasheta ba. "Ke" yafadi ahankali amman ko gezau batayiba kana ganin baccin kasan bata dade dayinshi ba. "Kee!" Yafadi da karfi dudda tanada nauyin bacci amman har cikin zuciyanta taji yanda yakirata agigice tafarka tamike tsaye towel dinta na neman kwancewa dawani kalan mugun sauri Abee yadauke kai tareda juyawa yace "go and pray" yaja kofan yawuce da sauri dudda uban baccin datakeji but she's so use to salla da asuba bayi tashiga tanaso tai wanka still tarasa yanda zatayi jikinta har danko yake mata gatanan kaman kifi sabida son wanka, brush tayi kawai tayo alwala tafito tana tafiya ahankali gaban babban wardrobe na bango dake dakin taje tabude ahankali kaya tagani acike sababbi babu atampa ko daya saidai abayoyi da kayan bacci da kananun kaya sai hijabai wani milk hijab taciro tasaka tana tunanin to inane gabas aka turo kofan Kausar ce sanye da kayan

bacci na riga da wando batare data shigo ba ta tsaya nan gaban kofan, gaban mirror tanuna mata tace “nan ne gabas Abee yace nazo na nuna miki” tajuya zata wuce dasauri Lujain tace “ya ake kunna shower ruwan zafi yazo”? Batare da Kausar tajuyo ta kalleta ba tace “ki murza wajen zuwa kasa” tana maganan taja kofa tawuce dan hararan kofan Lujain tayi tace “angaya miki nima inason gidan naku ne dan nama tambayeki shine zaki amsani kaman na rokeki kudi? Mai halin Ya Abida kawai” tasake hararan kofan Dadduman ta shimfida tahau kai tai salla saikuma tai shiru bazama ta iya kwatanta abinda takeji ba kaman taita ihu tana kuka takeji sabida kunci daura kanta tayi akan gadon tana tunani ga yunwa datakeji bana wasa ba yanzu shikenan barata dinga  ganin Gwaggo ba da Gwaggo na nan da yanzu taci abinci, da yanzu tana mata hira, she’s missing Gwaggo kaman takira sunanta taganta anan wani sabon kuka yazo mata kawai tahau kuka anan saida tayi takoshi sannan bacci yay awon gaba da ita.

7 daidai Abee ya shigo gidan saida ya gaida Hajiya sannan yataho sama dakinshi yawuce batare daya kalli daidai da kofar dakinta ba sake wanka yayi yashirya cikin wani black suit na italian yasa black takalmi sai kamshi yake yafito rikeda wayanshi a hannu harya wuce kofan dakinta kaman wanda yatuna wani abu yadawo wannan karan bai knocking ba yabude dakin zaune yaganta kan dadduma sanye da milk hijab tadaura kanta akan gado tana bacci, daganan kofa yakirata. “Kee!” Firgigit tabude idanunta kaman taji muryan mala’ika mikewa tayi zumbur hakan yasa towel dinta yay kasa hijabin yawani kama jikinta dayasa zaka iya ganin komi dauke kai Abee yayi saikawai yajuya yafita batare dayace mata komiba.
Kokarin hawa gado tayi ta kwanta but jin fatar jikinta kaman ma danko danko yake mata yasa tacire hijabin tawuce bayi, da ruwan sanyin hakanan tai wanka dawani sabon soso da shower gel datagani abayin mai kamshin dadi sai ihu take tana sauke ajiyan zuciya sabida sanyin ruwan, daura towel tayi tafito har rawan sanyi takeyi sosai tawuce takashe AC sannan taje gaban madubi wani cream datagani awajen na QEI tadauka tabude dan shima sabone tashiga shafawa sabida sanyin ya barta gama shafa man tayi ganin taki daina jin sanyi yasa takoma bayin tacire towel din ta wurga washing machine datagani abayin tadauko wani towel din tadaura tafito, zama tayi jin sosai takejin sanyi yasa tasake mikewa tai wajen gadon tashiga gyarawa sabida tadainajin sanyin daidai tana gama gyaran ana sallama tareda bude kofan dakin hakan yasa da sauri takalli kofan da kodaddun idanunta dasunsha kuka Anty Samira ne tace “gyaran gado kikeyi Lujain”? Gyadamata kai Lujain tayi ahankali tace “ina kwana”? Murmushi sosai Anty Binta tayi tace “muntashi lafiya ya Kwanan sabon waje”? Shiru Lujain tamata batare dabata amsaba karban bargon hannunta Anty Binta tayi tace “kawo natayaki ninkewa naga yamiki nauyi kaman ma kin wanka ko”? Gyadamata kai Lujain tayi ahankali, Anty Binta tace “to je saka kaya duk suna cikin wardobe atampopinki ma yau tela zatazo ta aunaki, yi maza sa kayan musauka kasa”? Gyadamata kai tayi hankalinta na kara kwantawa wannan datace su sauka kasa that means zata kaita gida kenan, wardrobe din tabude dogon rigan da hannunta yafara tabawa tadauka wani nakine amman yanada gold stone dake sparkling, dan juyawa tayi tadan kalli Anty Sam ganin hankalinta gabaki daya nakan bargon datake gyarawa akan gado yasa ta dauki cotton pant data gani awajen Babba aka sayo da kananu babban tadauka tasaka yamata cip tasaka underskirt, sannan tazare towel din ta ijiye tajuyama Anty Samira baya tadau wani white singlet tasaka daya kamata bam dan ko kadan batason tasaka

bra tadauki rigan tasaka dayawani haskata da kaman dan ita akayi, dan kwalin abayan tadauka zata yafa dasauri Anty Sam data gama tana kallonta tace “noo kifara gyara gashinki” dan zaro idanu tayi ahankali tace “ban iyayi ba Gwaggo ke mini” yanda tai maganan saida Anty Binta tai murmushi ganin yarinyar nada shagwaba komi nata ashagwabe takeyi dan yamabi jikinta tace “zauna kiga” zama tayi akujeran gaban dressing Anty Binta tacire ribbon din tana kallon tsayin gashinta sannan tadauki man kitso tashafa mata tareda tsage gaban kan sannan ta tajemata ahankali tai parking gashin dayawani kwanta tai parking tsaf tana kallon fuskanta tagaban madubi tace “idanunki sun kode da yawa sa kwalli saimu sauka muyi breakfsat ana jiranmu” kwallin tadauka tasaka ahankali sai idanun sukai kaman na aljanna gyalen Anty Binta ta karba tayafa mata aka sannan tace “tashi mujeto” tashi tayi Anty Binta tai gaba tana biyeda ita abaya suka fice daga dakin sukai stairs kanta akasa, kowa na nan, Hajiya na zaune tasanya wata atampa blue mai kyau, sai Abee dake zaune kan one sitter dake facing stairs din, sai Kausar na zaune akasa wajen kafanshi rikeda littafi da byro a hannunta tana rubutu, sai Abdallah yana zaune kusada Hamza da Ibro duk suna kallon stairs din sai Sajida da Zainab da Maman Aneesarh duk suna zaune suma tareda matan Ibro ga yara akasa suna zazzaune, kallo daya tama falon da mutanen ciki tasauke kanta kasa hakanan kawai gabanta nafadi dum dum dum, ko Anty Binta ta lurada hakan ne kamo hannunta tayi suka karasa sauka kasa har zuwa gaban Hajiya tace “ga Maman mu nan gabadaya dudda jiya dakika ganta kinata kuka but itane Maman Mu Hajiya Babba dakanta” dakuwa Hajiya tama Binta tace “kinci gidanku Binta” sannan takalli Lujain da kanta ke kasa tace “Mun tashi lpy Lujain” Gyadamata kai Lujain tayi ahankali murya chan kasa tareda dan dukawa kaman yanda take gaida Baba tace “ina kwana Hajiya” murmushi Hajiya tayi tace “lafiya lau, to har yanzu boyemana fuskan akeyi ne” kara noke fuskanta tayi kasa, kusada ita Hajiya ta nuna mata tace “zoki zauna to” kasa zama tayi kusada Hajiya ahankali ta zauna akasa kaman zata fashe da kuka daidai nan Aneesarh dake wasa akasa tawani rarrafo dagudu zuwa jikinta tana kokarin magana na yara tana kallon fuskan Lujain din kaman yanda yara keyi irin taga bakuwan fuskan nan sai kowa na dakin ya tsaya yana kallonsu, ware idanu Lujain tayi for the first time dawani kalan sauri tasa hannunta tadauki Aneesarh ahankali tace “Fine babyyy” washe baki Aneesarh tayi tana dariya tanajan gyalenta ahankali gyalen abayan ya zame kasa gashinta da Anty Binta ta gyara mata yawani bayyana for the first time Lujain tawani saki murmushin dayasa dimples nata duka biyun suka lotsa ganin yanda Aneesarh keja mata gyale daidai lokacin Abee yadan kallesu.

EPISODE 20

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Breakfast aka fara kawowa cikin falon dan Hajiya tace ita barata dinning ba, Maman Aneesarh tace “Aneesarh taho kisha cerelac dinki kibar Anty Lujain tayi breakfast” sauka daga jikin Lujain Aneesarh tayi ahankali mikewa tayi kaman zataje wajen Mamanta saikuma da gudu tai wajen Abee zatahau jikinshi takasa, daukanta yayi ahankali yana kallon fuskanta ahankali yace “you don’t want to eat”? Gyadamai kai tayi da sauri tana kallon Coffee dayake sha, dan murmushi yayi yakai bakinta kurba tayi kadan jin daci yasa ta tabe baki tasauka daga jikinshi tawuce wajen Mamanta.

Lujain na zaune inda take akasa atisha yazo mata hannunta takai kan fuskanta tayi tanajan hancinta saiga nabiyu yazomata shima tayi tace “Alhamdulillah” na uku na zuwa, Hajiya tace “sannu Lujain” na hudu ne yazomata shima tayi dayasa kowa ya kalleta banda Abee dake kokarin kurban coffee shi, Hajiya tace “kin kwana da AC ne Lujain”? Gyadamata kai Lujain tayi ahankali, hakan yasa Hajiya tace “bata farfesu da shayi tasha Binta, sannu mura keson kamata” shayi Anty Binta tahada mata mai kayan kamshi, bala’in yunwa takeji jikinta har rawa yasoma ganin shayi, Anty Binta nagamawa dasauri tadauki cup nashayin takai bakinta ta kurba wani kalan zafi dataji yasa batasan lokacin datasaki cup dinba shayin sai cinyanta wani kalan ihu ta kurma dayasa har Abee saida ya kalleta. “Wayyoooo Allah na zafi, Gwaggo” tai maganan tana kokarin kwaye doguwan rigan sama tana yarfe hannu tana kuka, Hajiya tace “daga gani bata sabashan shayi mai zafin nan ba Subhanallahi sannu ya isa daina kuka” Anty Binta ganin shirin dage rigan take yasa takai hannunta ta taba inda shayin yazuban mata tace “sannu sannu, jeki cire kayan zan biyoki da breakfsat din sama” Gyadamata kai tayi tana share hawayen daya zubomata tawuce sama da sauri tana tafiya ahankali su Sajida suka bita da harara, Anty Binta tashiga hada mata breakfsat nata a tray tace “Kausar zo dauka ki kaimata” dan turobaki tayi sannan ta tashi ahankali tazo tadauka tawuce sama daidai Abee ya mike yakalli Hajiya yace “natafi Hajiya” ahankali tace “tom Allah bada sa’a Imran” wucewa yayi yafita daga dakin suma su Hamza da Abdallah suka fice daga falon Sajida da kaman jira take su fice tace “tsakani ga Allah wlh da auren wannan yarinyar kaman buhu gwara rashin aurenta, wanan shirmen za’a bama Ya Imran a matsayin mata ai wlh ancuceshi haba mana” Zainab tace “mugun an cuceshi ma bakiga ko kallo bata isheshi ba, yarinya banda haske babu abinda ya ceceta sai shegen kiba, taga shayi jikinta har rawa yake sabida son abinci” Matar Ibro ne dake wajen tace “wlh irin kibar yarintan nan ne, nima akwai kanwata Ummie haka tun tana karama takeda irin wannan kiban kaman ana hurata tashi daya kuma ta zazzage kiban tass kaman ba itaba itama zata rame ne, kwanan nan ma tunda duk damuwa yamata yawa” cikeda kulewa Sajida tace “ba wannan ake magana ba kekuma Matar Ibro mu bama sonta amatsayin Matar Ya Imran ne, mezaiyi da yarinyar da Kausar ta girma wannan ba cuta bane” daidai nan Kausar tasauko tace “ni wlh na tsaneta Allah ya kyauta Abee dina yay rayuwa da wacce na girma amatsayin mat…..” wani mugun kallo da Hajiya tama Kausar yasa takarasa maganan tace ”zoki saka Hijabinki kibar gidan nan kitafi makaranta nasan Hamza na mota yana jiranki” ba musu ta taho hijabi ta dauka da jakanta tafice Hajiya takalli su Sajida tace “kuzo kubarmini gida babu ruwanku da yarinyar

nan, babu abinda ya shafeku da ita dan haka ku kiyayeta, bansonjin wani yakara maganan ta agidan nan, ban yarda kuci zalinta ko zarafinta ba, babu ruwanku tsakaninta da mijinta Imrana shine mai ita shine mai iko da ita, koni ba zamana takeba zaman mijinta take agidan nan, koba komi I expect dukanku ku girmamata amatsayinta na Matar yayanku dan haka ku kiyaye" duk shiru sukayi Hajiya tamike tawuce dakinta.
EPISODE2️⃣1️⃣

Jama'a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Abee na zaune a office nashi wuraren 2:30 aka tura kofan office dinshi batare da anyi knocking ba aka shigo dago kanshi yayi kallo daya yama Musty dake sanye da manyan kaya yana kalllonshi yana wani makirin murmushi yadauke kai yacigaba da abinda yakeyi, maida kofan Musty yayi yarufe yakaraso gaban table yace "Ango Ango kai kaga wani glowing dakakeyi ne irin na amarcin nan" dan dariya yayi ganin ko kallonshi Abee baiyiba Musty yace "no bama wannan ba tell me everything about the first night" wani mugun kallo da Abee yamai yasa yawani kalan kyalkyace da dariya yace "inda kallo na kisa da yanzu idanunka sun kasheni yafi sau dari" dauke kanshi Abee yayi yacigaba da duba papers din dake hannunshi yace "idan abinda yakawoka wajena kayi kenan kabarmin office please" hadiye dariyan Musty yayi yakalli Abee yace "to ka ijiye takardun ka kallen mana muyi magana" dan ijiyan zuciya Abee ya sauke ya ijiye takardun ahankali yakalleshi tareda folding hannunshi a kirji cikeda tsokana Musty yace "yaushe zaka komarda Amarya gidanka? Kasan gidan Hajiya bazai barka kai amarci da kyau bako"? Akufule Abee yatashi pappers din yashiga tattarewa yabar wajen yakoma kan lumtsetsen couch na office din yazauna ahankali yacigaba da abinda yakeyi anatse shikuma Musty yana zaune inda yake yana kallonshi yakai kusan 10min sannan yatashi shima yazo yazauna kusadashi batare da Abee yakalleshi ba yace "zan barmaka office din gabaki daya fa Mustafa" murmushi Abee yayi yace "nasan zaka iya, all jokes apart magana nazo muyi Imran look at me" yanda yay sounding serious yasa Abee yadago idanuwanshi ahankali yakalleshi alamun ina jinka. Ahankali Musty yace "Nasanka to be someone da kana taimako kana tsayama wayanda bama kasansu ba kabi musu hakkinsu ka kwace yancinsu, yaran dakai sponsoring

education nasu bansan iya adadinsu ba saisa yauma is still on that matter nakeso nida kai muyi maganan fahimta best friend" shiru Abee yayi still yana kallonshi anatse Musty yace "I know bakason auren nan and you don't consider this girl your wife" daukekai Abee yayi hakan yasa dasauri Musty yace "hear me out mana Imran bawai inaso nace you should consider her matarka bane wlh ko daya I accept that take as long as u want kafin kai accepting nata kokarkayi accepting nata ni duk dayane awurina but as your friend reminder na musulunci nazo namaka" shiru Musty yakarayi sannan yakalli Abee yace "I know you better than anyone nasan yanda kake idan bakason abu yanda kake wulakanta abin, banso kama dat small innocent girl that kind of treatment Imran, bance kai accepting nataba as your wife but inaso ya zamto ka kiyaye hakkokinta na musulunci, lafiya, ci, sha, sutura and respect, duk kabata kaga idan ka wulakanta yarinyar nan and neglect her mutanen gidanku kap haka zasu mata suma, remember bata tareda dan uwanta ko daya, remember kaman yanda su Kausar basuda mama itama batadashi su Kausar sunma fita gata in the sense sunsan mahaifiyarsu banda haka kaga ga all your sisters and family sun taso cikinsu itako has only her grandma! Just grandma, inaso kajata ajiki be nice to her please Imran, saikuma second abu dazan fadamaka is school idan all this issue yakara sanyi saika nemi wani good school kasata since school datake sun koreta saita fara wani sabo mai kyau kaji Imran that's the only abu da dama zan maka magana akai kaji"? Dan dauke kai Abee yayi kaman bazaiyi magana ba saikuma chan yace "naji" murmushi Musty yayi yace "to hurry ka karasa abin nan gashichan ana kiran salla muje muyi saimu wuce gida".
**

Koda takoma daki kayan tacire tashiga bayi tana wanke kafanta wajen dan ja yayi dan bawani konewan kirki bane towel ta daura tafito tana kallon kulan abinci da tray shayi dataga an kawo mata dabatasan waya kawoba, zama tayi tahada shayin dakanta ta shanye tass sanan tacinye duka chips da egg dake kulan ta shanye farfesun shima tass rabonta da abinci tun jiya hawa gado tayi ahankali sai bacci koda Anty Binta tashigo ganinta kwance kan gado da towel yasa ta murmushi ta kwashe kayan abincin tafita, wajajen azahar ta tashi tashiga bayi da ruwan sanyin still takara wanka tafito tana atishawa hijabi tasa tai salla sannan tazauna kawai tai shiruu tana kallon dakin, duniyan kawai yamata ba dadi, komi ya tsayamata chak, gidan yamata wani kala kawai sai hawaye sosai tayi kuka jin ana taba kofanta ana magana yasa tashare hawayenta da gudu, Anty Binta ne tashigo tareda wata mata kallo daya Anty Binta tamata tagane tai kuka amman tai kaman bata saniba tace "anzo aunaki tashi to" tashi tayi ba musu matan ta aunata tsaf sannan suka fice itada Anty Binta chan saiga abinci wata Yar aiki takawo mata dauke kai tayi wasu hawayen sun sake zubomata that means bara'akaita gidansu ba kenan, tsanan abincin taji tayi jin ana kiran la'asar yasa tawuce bayi tadauro alwala tazo tai salla, jin dakin yamata wani kala sotake tama danga hasken rana babu yasa ahankali ta tashi tai wajen window ta yaye labulen tareda bude window wani kalan iska ne yabuge fuskanta ahankali tasauke ijiyan zuciya tadade tsaye wajen sannan tajuyo akwatin da aka kawo mata tai wajensu tabude duka, robobin daddakkun magungunan ne daban daban da sauri ta maida tarufe dan barata shaba magungunan nan da badadi dayan tabude ganin su chocholate minti biscuits da yogurt daya cika akwatin yasa batasan lokacin datai murmushi ba tawani fashe da kukaba takifa kanta kan kafa ahankali tace "Gwagooooooo" sosai take kuka da sunan Gwaggo, chocholate guda uku ta

dauka sannan tarufe akwatin tasaka wani white slippers pink dake dakin masu kyau daidai kafanta tabude kofa ahankali tafito tana mamaki dataji gidan tsit babu ko muryan yara bin ko'ina take da kallo hartakai stairs tafara sauka tana bude chocholate dinta wata Yar mata tagani afalo tana shara matan jin tafiya yasa tadago kanta dan murmushi tayi ganin Lujain tace "ina yini amarya"? Dan turobaki Lujain tayi jin ankirata da amarya takarasa saukowa ahankali tace "ina masu gidan"? Murmushi matan tayi tace "duk sun fice nan makota yau ana sunan matan Kamal" shiru Lujain tayi sokawai take tafita waje juyawa tayi tafara tafiya zuwa kofa itadai Yar aikin tacigaba da sharanta tana mamaki ina Amaryan gidan nan zata daga ita sai towel akirji babu ko hula, bude kofa ahankali Lujain tayi tana kallon babban tsakar gidansu dayaji flowers ahankali tashiga sauka dagakan dakalin tana kallon gate dababu kowa awajen wani zuciyan nacemata tawuce tabude tafice abinda ta tafi gida wani zuciyan kuma nacemata karta fita kotaje gida daga Gwaggo har Baba zasu kara dawo da itane, tafita ma mutane su ganta ayita kallonta ana kiranta Yar iska tunda yanzu duniya gabaki daya sun santa, hawaye taji sunzo mata tunawa datayi abinda yasa tamazo gidan nan in first place, karasawa tayi wani wani plastic chair dake wajen flowers na compound din ta zauna takai chocholate nata baki ta balla tana taunawa still tana kallon gate din, kaganta kaman wata aljana fatarta fari kal kaman jini zai fito idan katabata ga pink towel da slippers ajikinta she looks so adorable and very cute.

Tana nan tanacin chocholate din tana kallon gate aka bude karamin gate dasauri aka shigo mai gadi ne baima lurada itaba key gate yacire da saurinshi sannan yashiga bude gate din sai zare idanu take innocently tana kallo tanakai chocholate bakinta tana balla.
Ana bude gate din daga Abee har Musty dukansu hangota sukayi zaune kan plastic chair daga ita sai towel babu dan kwali akanta hannunta rike da 3 different chocolate data bare tana ballansu all at the same time, da sauri Musty yadauke kanshi yaciro wayanshi yana dannawa kaman baiga komiba shikuma Abee kuri yayi yana kallonta yanda tadage tana kallon wajen gate din har mikarda wuya take kaman wata jimina tanacin chocolate kaman akwai abinda ta ijiye waje, jan motan yayi ciki tabi motan da kallo batare data gane waye aciki ba dan bata iya gani mai gadi yashiga kulle gate din.
Ta glass Abee ke kallonta batare daya fito ba kozata tashi tashige ciki amman ko gezau sai kallon gate din dama tacigaba da yi tanacin chocholate dinta, dan kallo Musty yayi ganin yana danna wayanshi yasa batare daya kashe motanba yace "I need to get something for Hajiya bari na karbo prescription din mutafi" "okay" Musty ya amsashi atakaice hakan yasa Abee yabude kofa yafito tanacikin kallon gate taji karan bude kofan mota hakan yasa takalli wajen da sauri hada idanu sukayi itada Abee dake mata wani kalan kallo wani kalan faduwa gabanta yayi takasa cigaba da tauna chocholate din datakeyi takasa tashi takasa zaune takasa komi, sai kirjinta dake bugawa dum! Dum! Dum! Daidai Abee yakai gabanta batare daya kalleta ba babu alamun wasa a voice nashi yace "follow me" yay gaba tashi tayi hakanan kawai taji jikinta yafara rawa falon itama tashiga amman taga haryay stairs hakan yasa tabishi abaya agaban dakinta taga ya tsaya yay folding hannunshi akirji yajuyo yana kallonta, jitayi legs nata are shaking amman haka tadaure kanta akasa takaraso ahankali gaban dakin ta tsaya tana watsa da yatsunta cikin sanyin murya da yet zaka jishi a zafafe yace "bakida kayan sawa ne"? Girgizamai

kai tayi batare data dago kanta sama ta kalleshi ba, cikeda dan zafi Abee yace “then why are you sitting outside da towel”? Dan tabe baki tayi irin na masu shirin yin kuka jin yanda yake mata magana kaman zai daketa ahankali tace “ai kaya tsungulina sukeyi, haka nake zama awajen Gwaggo naa” wani mugun kallo yamata yace “look up” ahankali gabanta na racing tadago idanunta dahar sun cika da kwalla sosai takallai, babu wasa kan kwayar idanunshi yace “this house yamiki kama da gidanku?” Girgixamai kai tayi daidai hawayen na zubowa sharrr yace “then this should be the last time dazaki daura this thing kifito waje understood”? Gyadamai kai tayi ahankali saikuma tajuya da sauri tabude kofan dakinta tashige tareda fashewa da kuka sosai tafada kan gado, yakai kusan 1min tsaye wajen yanajin karan kukanta yadanja tsaki yawuce dakinshi yarasa mesa yakemata magana with anger he’s so pissed of ne wlh.
Wanka yayi ya shirya tsaf cikin jeans da Riga yadauki wasu jersey yahada awani karamin workout bag dan yanaso yabuga kwallo bayan magrib yafito batare daya kalli kofan ba yawuce yasauka kasa.
EPISODE 22

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Wajen motanshi yayi yabude yashiga ciki yana jefa jakan daya dauko baya yatada motan Musty na kallonshi baicemai komiba saidan murmushi dayayi tareda gyara zamanshi, ganin ba hanyar pharmacy sukayi ba sai barrack dasukayi zuwa filin kwallo yasa Musty kawai murmushi yace “maganin Hajiya fa” changing room Abee yawuce batare daya amsashiba Musty yabishi abaya suka shiga shidayake Musty nada kayan chanzawa a locker shi na changing room shiryawa sukayi suka fito suka shiga field sosai suke buga kwallo team na Abee daban nasu Musty daban Abee saicin kwallon yake kana gani kasan ya iya kwallo sosai ya kware, saida aka fara kiran sallan magrib sannan suka tashi wanka sukayi suka maida kayansu sannan suka wuce mosque.

Saida akayi isha’i sannan yadawo gidan kashe mota yayi yafito yana magana da waya akan kunnenshi, yashiga falo anan ma yake gani suma basu dade da shigowa ba, samin waje yayi yazauna yakarashe wayan dayakeyi sannan ya amsa gaisuwan kannenshi daidai nan Hajiya tafito daga dakinta da charbi a hannunta tace “waini tunda nashigo banga Lujain ba, ke Kausar tashi kije ki kiramini ita nasata a idanu” tashi Kausar tayi ahankali tawuce sama, Hajiya takalli Abee tace “dazu fa kaman nace itama ta shirya tabimu sunan saikuma dai na bari dan bangaya maka ba” shiru Abee yayi baice komiba dan baimaso anamai magananta daidai nan Kausar na saukowa tace “tana wanka Hajiya” amman nafada mata daidainan Anty Binta takawoma Abee shayi zubamai tayi a mug tabashi karba yayi ahankali tace “Yaya nakawo maka dinner”? Girgixa mata kai yayi yace “no” saida ya shanye shayin tass sannan yatashi yace “Hajiya bari naje daki” “to Imrana Allah bamu alkhairi” wucewa yayi yahau stairs yayi sama yana gab da karasawa gaban dakin Lujain Lujain tabude kofan tadakinta tafito tana sanye dawani doguwan riga black tana rawa rawan sanyi dan bala’in sanyi takeji gashin kanta ya dan hargitse ga lema leman ruwa tagaban gashin, juyowa tayi bayan ta maida kofan tarufe karaf suka hada idanu da Abee dake tahowa yana tafiya one one kaman wani sarkin kasa, wani kalan mugun faduwa gabanta yayi dawani kalan sauri har hannunta na rawa tabude kofan dakin takoma cikin dakin dasauri tareda maida kofan tarufe daidai wani atishawa na zuwan mata tayishi, bin kofar dakin nata Abee yayi da kallo yawuce yashiga corridor yabude dakinshi yashiga.

Ahankali tazauna kan gado tai shiru tadade zaune ahaka saikuma ta tashi tacire rigan tadauko towel tadaura tasake dawowa ta zauna bakin gado tasakeyin shiru tanajin wani kalan yunwa, wani kalan kwanciya tayi kaman marainiya tana kallon kofa bude kofan nata akayi aka shigo saida tadan firgita ganin Anty Binta ne yasa dasauri ta tashi Anty Binta tace “kince ma Baba baki kara zama da towel amman kinata zaman ko” sauke kanta tayi ahankali kasa tana wasa da yatsanta batare datace komi ba, Anty Binta takaraso gaban gadon tace “Hajiya na kiranki mesa bakizo”? Dago kanta tayi ahankali takalli Anty Binta saikuma takalli kofan dakin takasa cewa komi, kallon kofan Anty Binta tayi itama ganin kofan take kallo saikuma ta kalleta tace “Ya Imran yahanaki fitowa”? Gyadamata kai tayi ahankali hawaye na gangarowa daga idanunta wani kalan mugun tausayi Anty Binta taji tabata hakan yasa gently tazauna bakin gadon bama tasan mezata ce ba tace “ki yakuri kinji Lujain” kaman jira Lujain take fadawa jikin Anty Binta tayi ta kankameta sai kuka, dan lunshe idanu Anty Binta tayi tabudesu zatama Hajiya magana tagayama Ya Imran yanemi makaranta yasata tun wuri kan wani abu yasami yarinyar mutane gashi babu mai kulata daga ita sai Hajiya ke kulata yanzu idan ta tafi next week yazatayi, tadade tana kuka sannan Anty Binta tace “Ya isa to” Anty Binta takai hannunta kan fuskanta tana sharemata hawayen tana mamakin taushin fuskanta da kumatunta kaman fuskan Yar jaririya, ahankali Anty Binta tace “kinajin yunwa ko”? Gyadamata kai tayi cikin kuka, murmushi Anty Binta tayi tace “to bari naje nakawo miki abinci da shayi, stop crying now konai fushi” hadiye kukan tayi tana kallon Anty Binta, murmushi Anty Binta tayi tajuya tafita daga dakin bata wani jimawa suka dawo itada Kausar daketa kumbure kumbure tadauki tray na kayan shayi itakuma Anty Binta tadauki flask guda biyu Kausar na ijiyewa ko kallonta batayiba tajuya tafita itakuma Anty Binta ta ijiye tace “to sauko kici” ahankali tasauko tana dake goge hawaye.

Zaune yake gaban desktop nashi yana wani aiki dagashi sai singlet dawani dan gajeren wando wayanshi ne yay kara hakan yasa yadauka ganin Hajiya ne yasa yakai wayan kunnenshi yana mamakin meyafaru take kiranshi.
“Ka sameni adakina Imrana” ta katse wayan, ijiye wayan yayi yatashi tareda daukan jallabiya yasaka sannan yasa slippers yafito batare daya kalli kofan dakin Lujain dayake iyajin maganan Anty Binta aciki ba tana mata fira wucewa yayi yasauka kasa Hamza da Abdallah yagani a falo suna buga video game suna ganinshi duk suka natsu dakin Hajiya yawuce da sallama yabude kofan yashiga Hajiya na zaune bakin gadonta tana kallonshi hakan yasa yakarasa ciki yazauna kan lallausan carpet na tsakar dakin ahankali yace “gani Hajiya” karasa jan charbi datakeyi tayi ta ijiye sannan takalleshi tace “Imrana” dan dago kanshi yayi yakalleta yace “na’am Hajiya” ahankali tace “I promise not to meddle with affairs naka dana matarka but I think akwai somethings that I can overlook a matsayina na babba” Hajiya tadanyi shiru saikuma tace “banson damuwa yama Yar karaman yarinyar nan yawa Imran, kaiba kulata kake ba kannenka ma haka, Binta ne kawai ke kula da yarinyan nan agidan nan nikuma baran iyaba dan kafafuna ba barina zasuyi ina hawa saman nan ina saukowa kullum ba” Hajiya takarayin shiru sannan tace “inaso gobe kafin katafi aiki ka dauki yarinyar nan ka kaita makaranta mai kyau kasata, islamiyya kuma zaka sata wanda su Kausar ke zuwa asabar da lahadi, amman dai gobe yarinyar nan tafara makaranta kaga karatu nata wuce ta, tunda bawai wani abu take agidan ba banda zaman kadaici da kuka dan haka ka kaita kasata a makaranta mai kyau kaji ko Imrana” gyadama Hajiya kai yayi yace “to” Hajiya tabishi da kallo tace “tashi katafi to Allah bamu alkhairi” ahankali yace “Ameen” yatashi yafita daga dakin tareda maida mata da kofan yarufe, sama yakoma daidai lokacin Anty Binta tafito tareda Lujain din da hijab ke jikinta black dayawani kalan haskata, ganinshi yasa tasauke kanta akasa tashige bayan Anty Binta ahankali tana wasa da yatsunta, Anty Binta ma sauke kanta kasa tayi ganin yanda yake kallonsu da wannan idanun nashi dabaka jurewa, kallonsu yayi ba yabo ba fallasa yace “where to”? Ahankali Binta tace “dakina zamu ta kwana awajen Ya Imran wai bata iya kwana ita kada…….” wani mugun kallo yama Anty Binta yace “bacemin daga nan” dawani kalan sauri Anty Binta tawuce tayi hanyar dakinta, wani kalan kuka Lujain taji yazomata batare data kalleshi ba tajuya ahankali takoma cikin dakinta ko tsayawa kulle kofan ma batayiba da gudu tafada gado sai kuka, yadade awajen tsaye sannan yakarasa gaban dakin nata batare daya kallo ciki ba yasa hannu yajawo kofan yarufe yawuce dakinshi.
EPISODE2️⃣3️⃣

Wanka yashiga yafito ya shirya cikin wasu milk pajamas masu bala’in kyau yazauna kan gado, drawer jikin gadon yajawo yadauko wani babban english novel na UK mai suna the soulless love, wani akwati yabude na glasses yabude yaciro wani white glass yasaka sannan ya jingina da gadon tareda kashe wutan dakin yakunna wutan side lamp kadai ya jingina da gado tareda jan bargo ya lullube kafanshi yabude book din yafara karantawa yanajin kukanta sama sama dan daga nan dakinshi yakanji abinda ke faruwa acikin dakinta, almost 2hrs yayi yana karanta

book din sannan ya maida yarufe ya ijiye saman drawer ya kwanta ahankali yanaso yay bacci amman baya iyawa kuma bayaso yanashan magungunan shi, dan lumshe idanu yayi yabudesu jin ko'ina tsit that means tayi bacci kenan, wayanshi yadauka ahankali yabude wani locked folder hotunane aciki na wata black beauty mata maidan jiki kaman yanayin girman Anty Binta, kaganta kamanninta da Kausar daya sak kaman tayi kakin Kausar ta tofar, lumshe idanunshi yayi ahankali yabudesu yasake daurawa akanta yatsanshi yakai kan fuskanta yana shafawa murya chan ciki yace "I've missed you Muna, why did you have to go and leave me alone at this stage of life"  shiru yayi tareda lumshe idanunshi again yaja wayan yakaishi kirjinshi ya rungume tsamtsam.

Karfe uku daidai kaman wata mayya tabude idanunta sabida azababben yunwan datakeji kaman wacce ta kwanta bataci abinci ba tsabagen yanda tasaba cin abinci tsakar dare, ga kanta dake wani kalan sarawa hancinta taji yatoshe da majina hakan yasa dabaki take numfashi ma, ahankali tabi dakin da kallo dan wutan dakin a kunne  yake, saukowa tayi daga gadon dasauri zuwa wajen kulolin dake dakin tashiga budewa amman babu komi cikinsu dan tas tacinye komi jiya da daddare, mikewa tayi tsaye tana kallon kofan dakin gabanta na faduwa saikuma ahankali tai wajen kofan gabanta nawani kalan mugun faduwa bude kofan dakin tayi kadan ta leka wutan corridor a kunne hakan yasa tafito da sauri tana gyara daurin towel din kirjinta kanta ba dan kwali, waigawa tayi takalli falon saman gabaki daya babu kowa ko'ina tsit, tafiya tafara ahankali tana taba cikinta da har wani ciwo ciwo yake mata yanadan kugi sabida yunwa stairs tayi tafara sauka tana kallon falon da wutanshi akashe yake gabanta nawani kalan fadi har hadiye yawu take tana sauke ijiyan zuciya takarasa sauka tana tafiya sadaf sadaf kaman wacce zatai sata tayi dining area dayake akwai dan haske dake haskowa daga wutan falon sama, ahankali kaman mai sata tashiga bubbude warmers na abinci dake kan dinning table din tana dubawa ganin akwai naman kaza soyayye dayawa dakuma rice a warmers din yasa tajuyo ahankali zata dauki plate daka cikin dankin wankakkun plate din dake kan dinning table din, mutum tagani tsaye abayanta yay folding hannunshi akirji kaman gunki, wani kalan zaro idanu tayi tawani kalan bude baki zata kwala ihu danta bala'in tsorata cikin zafin nama Abee yawani kalan fizgota tawani fado jikinshi taredakai hannunshi kan bakinta yarufe gam dan yasan tana ihu Hajiya zata farka dan batada nauyin bacci ko kadan tafito tagansu anan and that's the last thing he needs now, cikin wani kalan low voice kaman mai whispering yace "don't you dare scream" wani kalan zaro manyan cat eyes dinta take tana kallon fuskanshi dadan haske kadan din dake wajen wanda yazo daga falon sama jikinta ko'ina rawa yake jin gabaki dayan jikinta na manne danashi banda fuskanta dake facing nashi takasa kwace kanta gashi yataushe mata baki kamshin dayake narawa ni ratsa mata hanci, wani kalan kallon kwayan idanunta data zaro yake dudda the place is dark amman harwani kyalli suke, yanda yake kallonta batare daya zare hannunshi daga bakinta ba yasa taji wani kalan natsuwa nashiganta ahankali jikinta yadaina rawa hakan yasa tasaukar da idanunta kasa ahankali danta kasa jure idanunshi akanta, kaman wanda yatuna wani abu zare hannunshi yayi dagakan bakinta dasauri tareda tureta daga jikinshi tangal tangal tayi zata fadi tabuge da table kaman wacce batada stamina dasauri yakama hannunta yarike hakan yasa bata bugeba adan kufule yace "what are you doing here"? Dan kallonshi tayi adan tsorace akuma hankali cikeda sigan shagwaba tace "I

am hungryyyy" tai maganan tana kokarin kwace hannunta daya kama dayasa taji hannun yamata wani iri, sakin hannun yayi shima dasauri strictly yace "go back to ur room" kwabe kwabe tayi da fuska kaman zatai kuka saikuma tawuce dasauri batare datace komiba takoma sama kanta na bugawa sosai, shiga dakin tayi batare data kulle kofanba dan tsoro takeji takoma gado tazauna tana dafe kanta dakemata ciwo sosai tana numfashi da baki, kugin da cikinta yayi na yunwa yasa ta kwanta ahankali kan gadon tareda kife cikinta tajuyayar da fuskanta tana kallon mirror ta hakan yasa tajuyama kofan baya ahankali tana lumshe idanu wasu zafafan hawaye na sauko mata daga idanu sabida shegen yunwan datakeji gashi yakorota ciki, almost 5min tana kwance ahaka kaman daga sama taji kamshin turaren mai dadi nashiga hancinta dudda muran datake hakan bai hanata jin dadin turaren ba, ahankali tajuyo da kanta batare data tashi zaune ba dantaga waye yashigo dan ko kadan bataji alamun tafiya ba, Abee tagani tsaye bakin kofanta dauke da tray a hannunshi yana kallonta ba yawo ba fallasa, dawani kalan sauri takai hannunta tashare hawayen dasuke kwance kan fuskanta sannan ta yunkuro ta tashi zaune dan dafe kanta tayi tareda yatsine fuska sabida ciwonkan dataji kaman kanta zai tsinke yafadi, daukekai yayi daga kallonta batare daya shigo dakin ba yace "tashi kisa kaya" babu musu ta tashi gaban wardrobe taje tabude wani dogon rigan bacci tadauka sannan tajuya tadan saci kallonshi ganin yana tsaye inda yake har lokacin yasa ahankali tazo tawuce bathroom tamaida kofan tarufe, towel din jikinta ta cire tayi hanging sannan tasaka rigan baccin peach ne very decent ya tsaya mata iya knees dinta rigan yamata kyau sosai gadan katon tebanta daya fito daga rigan, gashin kanta dukya kara hargitsewa sabida yanda tasaka rigan dagaka, bude kofan tayi ahankali taleko cikin dakin, baya dakin amman ya ijiye mata tray abincin akan carpet, jellof rice ne da naman kaza kusan 5 akai sai tururi suke alamun yamata microwaving sai goran ruwa akan tray mara sanyi da spoon, da wani kalan sauri tafito har murmushi take ganin abincin zama tayi tadauki spoon dasaurinta zata fara ci daidainan aka sake bude kofan dakin dasauri tadaga kanta daidai tanakai rice bakinta hada ido sukayi da Abee dake rikeda kwalin magani guda biyu a hannunshi, ahankali tasauke kanta kasa tana ijiye spoon na abincin dazata kai baki tarasa mesa dazaran taganshi she use to become restless yatsunta tashiga wasa dashi batare dako motsin kirki takarayiba, karasowa cikin dakin Abee yayi har zuwa gabanta ya tsaya tareda ballo paracetamol biyu da actifed guda daya murya chan kasa kaman wanda bayason yay magana yace "take" dan kallonshi tayi ganin kallonta yake ba wasa kan fuskanshi yasa kaman wata yar yarinya tabashi hannunta, palm dinta yafara kallo sannan yasamata pills din aciki raurau tayida idanu tana kallon magungunan babu abinda ta tsana arayuwanta kaman magani, bottle water daya kawomata mara sanyi yadauka yabude yabata hannu tasa takarba shima sannan tadan kalli fuskanshi kaman mara gaskiya awani irin hankali akuma tsorace tace "in sha?" Wani mugun kallo yamata yace "no kishafa" raurau tasakeyi da idanu, sannan ahankali ta daura pills din kan cinyanta tadauki guda daya rak acikin guda ukun tana kallo sannan takalli fuskan Abee adan tsorace ganin ita yake kallo yasa dasauri ta dauke kanta takai maganin ta wurga baki taredakai ruwa ta kurba wani kalan kakarin amai tahau yi Abee dake kallonta yace "kikamin amai anan saikin lasheshi tass" yay maganan yana fizge ruwan daga hannunta ganin tana shirin zubarwa, sauran pills din yadauka daga kan cinyanta yarike a hannunshi sannan yakai ruwan bakinta ahankali yace "open your mouth" babu musu tabude bakin zuba mata ruwan yayi aciki sannan yace "raise your head" daga kanta sama tayi sannan yadan matso kusada ita faduwa gabanta yashigayi sosai amman tadaure,  watsa mata pills din acikin bakin

yayi dasauri tahadiye tana wani kalan tabe fuska da baki kaman taci kashi tadauki spoon tadebi rice dasauri takai bakinta tanaci hawaye yayi fall acikin idanunta, AC dakin yakalla ganin akashe yasa yakalleta har lokacin tabe fuska take irin na wanda yasha magani yace “da ruwan sanyi kike wanka”? Kaman daga sama taji tambayan, dan kallon fuskanshi tayi saikuma ta gyadamai kai ahankali kafin tadauke kanta tace “ban iya kunna ruwan zafi ba” dan shiru yayi yana kallon yanda take magana, jin baice komiba yasa tadago kanta hada ido sukayi dasauri tadauke kai, mikewa tsaye yayi yawuce bathroom nata yabude ya tsaya daganan bakin bayin yana kallon ciki bayin is very clean towels ne kusan guda 5 ta shaya ajikin hanger juyawa yayi yakalleta ganin tana zaune inda take bata tashiba yace “sainace kizo zakizo” dago kanta tayi tadan kalleshi saikuma ta taso ahankali dauke kai yayi yashiga bayin tabiyoshi ta tsaya daga nan bakin kofa nuna mata yanda zata kunna hot water yayi sannan yajuyo yace “kingane”? Gyadamai kai tayi ahankali kanta akasa ganin yana tahowa yasa tafice daga bayin dasauri takoma wajen abincinta tazauna tafaraci shikuma yafito daga bathroom din yawuce yafita daga dakin.

Tass tacinye abincin da naman tasha ruwa sannan tahau gado sai bacci.
4:30 Abee yafito cikin jallabiya yatada mutanen gidan batare daya shiga dakin Lujain ba, yawuce masallaci.
Wuraren 7 nasafe Hajiya tafito falo taxauna kan kujera daidai Kausar dake cikin kitchen tafito da kula zata ijiye kan dinning Hajiya tace “Kausar jeki cema Auntyn ki Lujain tashirya tsaf ta sauko Babanku zai kaita yasata a makaranta yau” Gyadamata kai Kausar tayi tawuce sama.
EPISODE2️⃣4️⃣

Knocking kofarta Kausar tayi jin shiru yasa tabude kofan dakin akan dadduma taganta dan yanzun nan ta tashi ganin tana salla yasa tace “Hajiya tace ki shirya kizo kasa” tana maganan tajuya tafita daga dakin.
Saida ta idar da salla tai azkar sannan ta tashi bathroom takara shiga tai wanka da ruwan zafi sosai ciwon kan datakeyi yatafi batajinshi kuma saidan hancinta dayay blocking shima kuma yaragu sosai dan tana iya numfashi da hancin yanzu bakaman jiyaba, fitowa tayi daure da towel tazo gaban wardrobe tabude tana kallon kayan wajen, wani abaya tajawo black ne gabaki dayanshi mai kyau kana ganinshi kaga saudi abaya, yauma bata saka bra ba singlet tasa da pant sannan tadaura abayan akai bayan tashafa mai, tadau gyalen abayan tadaura akan yamutsassen gashinta  tabude kofa tafito ahankali tafara tafiya chak ta tsaya ganin Abee na hayowa sama idanunshi akanta hakanan jitayi gabanta na faduwa sosai, saida yazo daidai dap da ita bakinta yadan fara rawa takasa ma magana, wani kalan kallo yamata daga sama zuwa kasa sannan yace “go back inside kidauki hijab kisa” yana maganan yawuce yabarta awajen, saida taji karan ya maida kofan dakinshi yarufe sannan tajuya ahankali takoma dakinta, wardobe taje tabude tana kallon hijaban wajen wani maroon hijab tadauka tasaka yamata wani kalan kyau kaman balarabiya ne tasaka hijabin sannan tadauki takalmin da Baba yasaya mata

tasaka dan babu wani takalmi adakin shima hala dan ba'asan size nata bane tafito ahankali take tafiya tazo stairs sauke kanta kasa tayi sabida yanda suka cika falon duk ana shirin yin breakfsat tunda tafara saukowa idanun Hajiya kyam akanta maroon hijabin datasaka ba karamin kyau yamata ba deep down tana addu'a Allah yasa suzo juna itada Imrana dan tanamai mugun kwadayin Yar yarinyar nan, murmushi tayi tace “Lujain an sakko” dago kanta Lujain tayi tadan kalli Hajiya wani kalan kunyan matan taji hakan yasa tamaida kanta kasa takarasa wajenta saida tazauna akasa kusada ita murya chan kasa tace “ina kwana Hajiya” murmushi tamata tace “har yanzu muran bai sakeki ba? Duk muryanki ta chanza kinsha magani kuwa”? Gyadama Hajiya kai tayi ahankali, Hajiya tace “waya baki maganin”? Dan shiru tayi dan batasan yaya zata kira sunan Abee ba hakan da Hajiya ta lura yasa tace “Imrana yabaki”? Gyadamata kai tayi ahankali, Abdallah dake saukowa kasa gaban Hajiya yazo yace “Hajiya natafi yau ina azumi bazanyi breakfast ba” yakalli Lujain da kanta ke kasa yace “good morning Anty Lujain” dago kanta Lujain tayi ahankali tadan kalli Abdallah dake kallonta yana murmushi sauke kanta kasa tayi tama rasa mezatace itane wannan babban yakira da Anty, Haiiya dake murmushi tace “Antynku Lujain badai kunya ba” murmushi yayi yace “natafi” “Allah bada sa'a Abdallah” Hajiya tafadi tana hararan Kausar datazo ta zauna gefen kujeran da Babanta ke zama rikeda plate na chips itama ta shirya makaranta hijabi kawai zata saka tafita, fitowa daga kitchen Anty Binta tayi itada Maman Aneesarh ganin Lujain yasa tai wani kalan murmushi tazo wajen suka ajiye kuloli tashafa kumatun Lujain hakan yasa tadago kanta dan murmushi tama Anty Binta tace “good morning Anty” morning Lujain bari nahada miki tea” tea tahada mata a big cup this time sannan tazuba mata chips a plate da fried egg da pepper soup, ahankali tafaracin chips din tanashan tea ahankali dan yanada zafi ba kaman wanda Gwaggo kemata ba, kamshin turaren Abee da yacika falon yasa tasan yasauko ne dan ko kadan bakajin footsteps nashi, zama yayi Anty Binta tace “Ya Imran coffee ko shayi Wanne kakeso”? “Coffee” yafadi ahankali yana duba agogon hannunshi, Hajiya dake kallonshi tace “zubamai da chips da farfesu Binta ni bantaba ganin makiyin abinci irin Imrana ba saisa gashinan Abdallah kaiya dauko” Baice komiba kawo mishi Anty Binta tayi a tray tadaura kan table dake gabanshi coffee yadauka yafara sha daidai nan Kausar tagama tamike takalli Abee shima kallonta yayi yanashan Coffee, kaman zatai kuka tace “Abee ban iya assignment dina ba” wani mugun kallo yamata yace “and u are telling me now” sauke kanta kasa tayi sabida mugun kallon dayamata ahankali tace “Abee kayakuri baran karaba” Hajiya dake jinsu tace “ke wlh fitinanniyan yarinya ce Kausar, ke kinci abincinki kin koshi saida shi yafaracin nashi shine zakimai batun assignment salon karyaci, tunda aka haifeki Babanki yadainacin abinci yakoshi” kaman zatai kuka tace “ai nace sorry ko Abee” ijiye coffee yayi ahankali yamika mata hannu alamun tabashi book din dawani kalan sauri tabude jakanta tadauko book din takawomai maths ne kan probability ne, ahankali yace “come here” kusadashi tazo cikin 2min yanunnuna mata yanda zatayi yamata solving daya yabata second question din yace tayi yagani zama tayi tafara shikuma yacigaba da breakfsat nan da nan tayi takawomai dubawa yayi yaga tayi daidai hakan yasa “now get ready, Hamza na jiranki a car” hada jakan tayi tasa hijabi tafita dagudu, saida yagama breakfast dinshi sannan yatashi yadan kalli Lujain data gama itama amman kanta akasa hakan yasa Anty Binta dake kallonsu tace “tashi kutafi Lujain” tashi Lujain tayi tadan kalli Anty Binta saikuma takalli Abee dake tsaye, juyawa Abee yayi yay kofa yace “Hajiya natafi” Hajiya tace “Allah bada sa'a bishi Lujain” binshi Lujain tayi itama tabude kofa tafito waje duk su Hajiya suka bita da kallo, wajen wata mota

daban yayi bmw baka ba jeep din jiyaba budewa yayi yashiga gaba hakan yasa takarasa wajen kirjinta bugawa yake kawai to ina zasuje baya tabude ahankali zata shiga suka hada ido wani mugun kallo daya mata yasa tamaida kofan tarufe tadawo gaba tabude gently tashiga cikin motan gabanta nawani kalan fadi, motan kamshi kaman ba mota ba, ganin credentials nata a motan yasa tadan bude idanunta takalli file din datasan Gwaggo kadai ke boyemata dan awajen Gwaggo suke acikin katon akwatin bununta taboyesu, ga birth certificate dinta, primary certificate dana JSS Ce dakuma na indigen da Nin dinta duka awajen, dan juyawa tayi takalli cikin gidan to Gwaggo tazone batasani ba, bude musu gate akayi suka fice dudda motan tinted ne gani take kaman zaa ganta hakan yasa ta sauke kanta kasa, sun danyi tafiya mai nisa wani hadadden school yakaita da baida wani nisa sosai da company shi yasan mai school din sosai childhood friend nashi ne, kashe motanshi yayi a parking space yasa hannu yadauki file nata yabude kofa yafito, kasa bude kofan tafita tayi sai kallon cikin school din take da student keciki gabanta nafaduwa yanzu nan ma za'a faracemata Yar iska ne dan yanzu ko'ina ansanta hawaye ne yacika mata idanu, juyowa Abee yayi ganin bata bude kofaba har lokacin yasa yazo ta wajen bude mata kofan yayi dasauri takalleshi lips nata har rawa suke murya chan kasa tace "ni……banason school, dan Allah kada kasani, wlh banaso" tai maganan hawaye na zubomata daga idanu dasauri takai hannu tashare yana wani kalan kallonta yace "why?" Dan kallonshi tayi saikuma tasauke kanta ahankali tace "nan ma zasuce ni yar iska ce maibin maza, everybody will be looking at me ana nunani ana cewa nice a video nan" fashewa da kuka tayi yace "don't you dare cry for me anan" dasauri tahadiye kukan tana goge fuskanta da bayan hannunta, cikin kakkausan murya yace "akwai wanda yadaukeki yakaiki sama ne when all the rest of the students na reception akasa? Akwai wayanda yakaiki bayin maza ne?" Girgixamai kai tayi wani abu na tokaremata zuciya, wani kalan dan tsaki yaja yace "kin zaci inason Auren nan da akamin dakene kokuma I fancy you one bit?" Shiru tayi yace "the way I am dealing with you dudda I don't consider or regard you matata kema haka zaki shiga school din nan deal with anything that comes ur way and study hard" gyadamai kai tayi ahankali tanaji kaman tafashe da kuka danji tayi tabama kanta tausayi, anatse yace "futo" fitowa tayi daga motan ahankali ta matsa gefe maida kofan motan yayi yarufe sannan yakalleta yace "ke" kallonshi tayi kaman yanda shima ke kallonta, calmly yace "karki dauki Auren nan da akamin dake as anything, ke ba matata bace and bazaki taba zama dayaba, as far as Imran is concern I don't have a wife! Dan haka do whatever you want, idan kinga wanda kikeso talk to him, mingle with your fellow students, dazaran komi settle down zan rabu dakene u will be back to your parents house cus babu abinda zanyi dake" yakarashe maganan yana tabe baki ahankali yace "kin gane"? Gyadamai kai tayi ahankali sotake tayi kuka amman yahanata gaba yayi yace "let's go" binshi tayi tana tafiya ahankali, gaidasu masu gadi sukayi sannan suka shiga ciki ga mamakinta kusan rabi da kwatan student na makarantan turawa ne kadan daga cikinsu ne yan nigeria, sama sukaje wani babban office yabude yashiga wani babban mutum ne zaune yana ganin Abee yatashi yana bashi hannu yace "welcome Soja, ga waje ku zauna" zama duk sukayi yakalli Abee yace "itane student din"? Gyadamai kai Abee yayi yace "bani file nata" bashi Abee yayi yadudduba sannan yakira secretary nashi yabata tamai photocopy documents nata duka yabaama Abee original, agabanta tanaji Abee yabiya 5.7M school fees nata da kudin textbooks nata da kudin Waec da neco dan yace yanaso tayi a SS2 din nan idan taci shikenan, secretary aka kira ta tafi da ita changing room dan saka uniform shikuma mutumin yacigaba da magana

da Abee yace “I assure you this babu wanda zaiyi bullying nata a school dina, her image will be well protected, sannan kaman yanda kamin bayani awaya last night zata dinga special lesson din 4 idan ta tashi saikazo kawuce da ita gida, and lunch dinta will be given to her, kabata one week zakaga tasake jikinta tashiga student da kyau without fear na being bullied ko kirata names, Ya guy din ankamoshi kuwa?” Daidai lokacin secretary tashigo tareda Lujain data saka kayan makaranta skirt ne dark blue da Riga sky blue long sleeve sai jacket dinshi dark blue, dakaramin farin hijab sai farin safa da black shoes, uniform din sun mata wani kalan kyau she looks chubby and sooo cute, tashi mai makarantan yayi yace “Soja muje mu kaita ajinsu tare” raurau tayida idanu tana kallon Abee daya dauke kanshi daga kanta yamike shida mutumin sukai gaba itakuma abaya wani class mai kyau SS2 suka tafi ajin duka turawa ne mutun 3 ne Nigeria sai ita yanzu ta hudu ga teacher a ajin shiga mai makarantan yayi yasa aka mata warm welcome sannan yakaita sit nata agaba tazauna ahankali tasake dagakai takalli Abee dashima kallonta yake wani kalan lankwashe kai tayi ashagwabe hawaye yacika idanunta tam har kyalli suke dawani kalan sauri Abee yabar wajen mai makarantan yasallami ajin yafito yasameshi agaban office suka karasa magana sannan yawuce yafita daga school din yashiga motanshi yawuce company shi that is just few blocks away.

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
EPISODE2️⃣5️⃣

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/

Inner Sanctum

Zaune yake agaban wani drawer shi kadai acikin sanctum din sanye da jersey na riga green da farin wando, an rubuta Mandawari abayan rigan, farin guy ne kal dashi siriri baida kiba ko kadan, kanshi irin wannan askin nan na yan kwallo ne anyi murde murde ajikin tarin gashin da abin yay kaman kitso dan twisting ne, wayanshi ne a hannunshi yana dubawa daidai an bude kofan sanctum din an shigo wasu players ne kusan su 13 duk sun shigo ciki suna zufa kowa yay wajen zamanshi goal keeper su yace “Man! What happen is like yau bakaine a field ba is another different person, what’s happening Bro”? Wani guy ne kamanshi daya zaune kusa dashi yana kokarin cire takalmin kwallon kafanshi mai suna Olusay yace “ai Man is going through a heart break this is the second week his stalker batamai magana tamai dropping love messages ba” wani mugun kallo Mandawari yama Olusay, yan dakin dukansu kowa barin abinda yakeyi sukayi sukataho gaban Olusay dasauri sukace “yanzu Mandawari daman yanada budurwan dayakeso”? Dan dukansu are finding it unbelievable, dan dariya yayi yace “yes” wani kalan mikewa Mandawari yayi cikin fushi yace “ubanwa yace maka sonta nake” dariya Olusay yayi sosai sannan yamike tsaye tareda cire riganshi yay hanging yajuyo yakalle team members dinsu yace “wlh mugun sonta yake na rantse amman he feel mutum irinshi mai over 400M followers can not love a girl like her shida har manyan top celebrities irinsu Kim ke sonshi amman yarasa wanda zaiso sai yarinyar nan he’s even ashame to admit sonta yake barima na nuna muku page dinta kugani kuyi following nata” yakai hannunshi zai dauki wayan Mandawari wani kalan rikemai hannu yayi yana huci yace “how many time zan gayamaka kadainamin irin abin nan Abdulaziz” cikin fushi Olusay yace “how many times zan gayamaka shi so babu two ways about it idan kanason abu kanaso ne idan bakaso bakaso ne admit cewa bawata Cinderella dream girl Allah yajarabeka da so ba, normal common girl Allah yajarabeka da so Muhammad” wani kalan mugun kallo Mandawari yamai yace “and so”? Olusay yace “dan haka kadena jan aji slide into her dm and respond to all her messages and confess your feelings Bro koba hakaba guys” duka yan team nasu sukace “hakane” daya daga cikinsu mai suna Obi yace “I can’t wait to see babe din da Man keso yanda yakema mata wulakancin nan I know she must be the most beautiful girl on earth” dan tsaki Mandawari yayi yace “you guys should stay away from me and my business” yay maganan yana cire nashi rigan ya chanza kayanshi zuwa normal Riga da wando black yadauki wani big jacket yadaura akan kayan dan sanyi akeyi a Greece thank God yau zasu koma nigeria, yana gama shiryawa aka shigo akace bus nasu is ready fita duk sukayi koda sukakai bus din shida yasaba zama da Olusay yau bai zauna wajenshi ba baya yawuce yazauna abinshi Olusay baicemai komiba.

Airport suka wuce business class aka biamusu dayake shida Olusay ne zasu Nigeria sauran kowa yay garinsu, saida jirgin sannan ya kwanta wayanshi yabude yashiga chat dm din Lujain yana dubawa tun 2019 tafara turamai messages har zuwa yanzu dasuke 2022 amman baitaba amsata daidai dasau dayaba, fitowa yayi yashiga Fred dinta yana duba hotunan ta, 5 pictures ne kawai tai posting, daga wanda tasaka scchool uniform sai wanda take itada Gwaggo, sai wanda tayi ranan salla da Ya Samira, saikuma wanda tayi ita kadai tayi bala’in kyau a hotunan

duka pink lips dinta ya tsare da idanu kaman tasaka pink janbaki, fitowa yayi yawuce wani blog a instagram yakara bude video ta na sex video nan da yanzu zai iya cewa yakalla yakai sau 20, saikuma ahankali yafito yashiga video da blog din still sukai posting na debunking news din cewa mutumin mijinta ne ga shaida daga wajen iyayensu, jazur idanunshi sukayi har jijiyoyin kanshi suka fito kashe wayan yayi ya runtse idanu ahankali murya chan kasa yace “you are mine Lujain! You love only me! You belong to me”…
*****

Har aka tashi daga makarantan tana aji, da kyar wuraren 1 ma tafita shima cafeteria officials nasu ne sukazo suka kirata kan tazo ta amshi lunch haka taje lafiyayyen abinci aka bata da drink harda kaza ga student awajen babu ma mai kallonta haka taci tadawo aji, malaman sai nan nan da ita suke yan ajinma namata magana itane ma bata amsasu da kyau kawai duktabi ta tsargu, 4 daidai aka gama musu special lesson din aka tashi kowa yashiga daukan jakanshi banda ita dake zaune inda take saida kowa yagama fita yarage ita kadai a ajin yasa tashiga hada books nata ajaka tamaida komi saikuma tai shiru tana kallon jakan yau kwana hudu kenan bataji muryan yan gidansu ba, bata gansu ba, koda su Baba dasu Mama dasu Ya Abida basu damu da ita ba Gwaggo fa? Yanzu Gwaggo barata nemeta ba, daman da gaske takosa takadata daga gidansu shikenan batada kowa, wannan wani kalan rayuwa ne da rana daya kawai tajefa kanta? Jitake kaman tadawo da hannun agogo baya ta chanza duka abinda yafaru ranan, babu wani abu datakejin dadinshi arayuwanta, ita batada waya, ita gidan nan babu wanda zai yarda yabata wayanshi balle takira Gwaggo ma, ita school dakomima baya mata dadi yanzu sabida batada Mama ne saisa abu haka ke damunta? Inda Mamanta na raye tasan barata wahala hakaba tunda gashi yanzu ma Gwaggo batasonta kaman Mama wasu kalan hawaye masu zafine sukazo mata tundaga yatsun kafanta kawai kife kanta tayi akan kafafunta tafashe da kuka sosai Abee yadade tsaye gaban ajin yana kallon yanda takife kanta kan kafanta tana kuka sannan yadanyi gyaran murya da sauri tadago jajayen idanunta, ganin Abee yasa dasauri tashare hawayen da bayan hannu ta mike tsaye ahankali tareda daukan jakanta ahankali ta goya sannan tafara tafiya kanta akasa ta taho gaban kofan, baice mata komiba yayi gaba hakan yasa tabishi abaya har zuwa waje, mota yashiga itama tabude gaba tashiga tazauna har lokacin idanunta jazur, harzai tada mota saikuma yajuyo yakalleta bayabo ba fallasa yace “why are you crying”? Dan juyowa tayi takalleshi yanda ya tsareta da idanu saitaji takasa mai karya lips nata har rawa suke tace “kewan yan gidanmu nake…...” Wani kukan ne yazo mata dasauri takife kanta kan jakan makarantan da akabata a school tafashe da kuka sosai cikin kuka tace “babu wanda ya nemeni cikinsu da Baba da Mama, dasu Ya Samira harma Gwaggo basu nemeni ba sun kawoni gidanku I am all alone babu wanda ke sona, kowa haushina yakeji, I am so scared mutane su ganni kar adinga nunani babu abinda kemini dadi, I just wish inama zan mutu maybe namaga Mamana achan naji dadi, babu wanda ke sona har Gwaggo na” tunda tafara maganan kallonta yake tabashi tausayi sosai inda Kausar dinshi ne fa in this situation, “wayace miki Gwaggon ki bata sonki” dago kanta tayi dasauri da rinannun idanunta takalleshi dauke kanshi yayi yakunna key tareda tada motan yaja motan sukabar wajen, saida suka shiga titi ahankali tace “inda tana sona dabatamin auren nan ba ni inada wanda nakeso” dan kallonta yayi saikuma yadauke kai yakalli titi kusan 3min babu wanda yace

komi acikin motan kaman daga sama yace “shi kike kallo rannan abayi”? Gyadamai kai tayi dasauri tana goge hawayen kan fuskanta da bayan hannu tace “eh sunanshi Muhammad Mandawari, ni shinakeso na aura” yana kallon hanya yace “kinfadama Babanki” gyadamai kai tayi tace “eh yasani” ahankali Abee yace “to mesa basu aura miki shi ba”? Dan rage murya tayi looking so sad tace “ai baitaba amsa messages dina a instagram bane ba” batare da Abee yakalleta ba yace “do you have phone”? Girgizamai kai tayi tace “a’a da wayan Ya Samira nabude instagram nai following dinshi rannan dana fara ganinshi a tV dakin Gwaggo yana buga kwallo” “kinason kwallo”? Abee yay maganan yana kallon titi, ahankali tace “eh inason kallon kwallo kuma inason Mandawari sosai, nasan inda yau zan ganshi all my problems will be gone zaije wajen Baba yace shine zai aureni bakaiba sai ka sakeni amini aure dashi natafi wajenshi muyi zamanmu” daidainan sukakai gaban wani saloon yakashe motan yadan kalleta ganin tana kallonshi kaman tasami tV da manyan idanunta masu kala dana mage yasa yadauke kai wayanshi yadauka duk tana kallonshi komi nashi  anatse yakeyi baitaba mata dogon magana ba sai yau kuma kaman magic sai yan maganganun sukasa ta manta da bakin cikin datakeyi, ijiye wayan yayi yajuyo yakalleta jin alamun ana kallonshi dasauri tadauke kai tana wasa da yatsunta, dauke kai shima yayi daidai nan Anty Binta tafito daga saloon din tazo bangaren Lujain tabude tace “Iyye yan makaranta oyoyo” murmushi Lujain tayi, Anty Binta tace “ke baki gajiya da kuka ne look at your eyes fito muje to a gyara miki gashin nan dabaki iya tajewa da kanki a kitsashi, kawo jakan nan nasa abaya Ya Imran yawuce miki dashi gida” fitowa tayi tamaida jakan baya itakuma Anty binta tazagayo ta bangaren Ya Imran tace “Yaya bamu ATM card dinka zandan yima Lujain siyayyan kaya dasauran yan kananun abubuwa na mata da batadashi” wani dan iskan kallo yamata sannan yadauki ATM card nashi yabata yace “6701 is the pin” murmushi Anty Binta tayi tace “thanks Big bro” jan motanshi yayi yawuce itakuma Anty Binta yakama hannun Lujain databi motan nashi da kallo suka wuce ciki.EPISODE 2️⃣6️⃣

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/

Shuku Anty Binta tasa akamata mai bala’in kyau, mai style yan kanana nan da nan tayi kaman ba itaba, tasa aka wanke mata kumbunan kafa da hannu Anty Binta sai kallon yatsunta take both nakafa da hannu sunada bala’in kyau gasu so chubby sannan yatsun farare dogaye, mace

mai ni'ima kana iya ganewa daga yatsunta both na kafa da hannu, bakaramin addu'a take kan Ya Imran yafara son yarinyar nan ba dan Lujain is a gift from Allah, kyautanta Allah yamai bayan wahalan rayuwan dayayi, 13yrs ba mata sai zaman kadaici da bautan Allah saisa Allah yabashi Lujain cus babu abinda Lujain batadashi gatada shiga rai, bala'in shiga rai, daga zuwanta saloon din nan harsun fara sonta, mai saloon din harda cema Anty Binta tanason sister nan nata tamata influencing saloon din nan adauki pictures nata zata biyata da kyau, saida tanuna musu matan aure ne mijinta bazai yarda ba sukabar zancen.

Biyan kudi sukayi sannan suka fito wani babban super market sukaje jakunkuna Anty Binta tasaya mata da takalma masu kyau da yankune da agogo, bracelets irin na yanmata dinnan, da kayan sawa english wears masu kyau sosai su sexy gowns, shorts, shirts, jeans dan sotake tadinga sawa Ya Imran yasoma dawowa hayyacinshi, takara mata abayoyi, da turaruka, harzasu fito tace "Anty su Chocolate" wajen chocholate sukaje sai alokacin Lujain tafara deban chocholates dasu biscuits dabama tasan dasu aduniya ba ita Anty abin dariya ma yabata tace "ai saisa kike kiba sweet tooth ni mutafi" biyan kudi sukayi aka kaimusu kayan mota sannan suka tafi bayan magrib suka shigo anguwan Anty Binta ke tuki gidan dake kusada nasu sukaga an bude ana shiga da sababbin furnitures Anty Binta tace "kowaye yasai gidansu Maman Adam oho" kallon gidan Lujain tayi dayake abude sai gyare gyare ake har fenti anyi, Anty Binta dake tuki tana kallon gidan tace "Maman Adam makotan mune sunada kirki gidansu ne amman sun saida sabida mijin zai koma US yasami aiki a chan" daidai anbude musu gate suka shiga cikin gidan, parking tayi suka fito zare hijab din school Lujain tayi tadauki ledan chocholate dinta tayi gaba mai gadi natayasu daukan sauran kayan sallama tayi tashigo falon ahankali daga Hajiya sai Musty da Abee afalo Musty ne ma yadago shi daga masallaci dabai shigo gidan ba sai bayan isha'i, kallo daya Abee yamata yadauke kai Hajiya tace "yan makaranta an dawo" Gyadamata kai tayi batare data karasa wajen ba tace "ina wuni" sannan takalli Musty ahankali tace "ina wuni" murmushi yamata yace "lpy lau" Hajiya tace "aiko kitson yay kyau mekika riko mana a leda" ledan takalla for the first time dan murmushi tayi tace "chocholate dina ne" dan dariya Hajiya tayi tace "sabida bakiso kibani ne kike cewa chocholate dinki ne ai shikenan jekisha Lujain" akunyace tadan sunnar da kanta kasa kaman mai koyon magana tace "Allah ni zan baki Hajiya" shi kanshi Musty dan murmushi yayi jin yanda tai maganan Hajiya tace "to nagode Allah amfana jeki cire kayan makarantan saikizo kici abinci" Gyadamata kai tayi tawuce sama, tana shiga dakinta taga jakan school nata an ajiyemata waje daya, bayi tawuce tacire kayan school nata tareda jefawa a washing machine sanan tai wanka da ruwan zafi tafito daidai Anty Binta na shigowa dakin rikeda manyan ledojin kayanta Maman Aneesarh ma natayata dan kallon Lujain din Maman Aneesarh tayi yanda kitson yamata kyau tace "Ya school"? Ahankali Lujain tace "lafiya lau ina wannan baby"? Murmushi Maman Aneesarh tayi tace "tayi bacci" sannan tawuce tafita daga dakin, Anty Binta saida tajera mata kayan tass dan ita bata salla sannan tawuce tafita itakuma tana idarwa zama tayi kan gado tabude ledan chocholate nata tashiga sha saida tasha daban daban kusan guda 7 sannan ta tashi tasakeyo alwala tafito tahau kan dadduma tana salla shigowa Anty Binta tayi ta ijiye mata abinci a kula tana idarwa taci batawani ci dayawa ba sabida yanda tasha chocholate din nan hawa gado tayi ko 3min batayiba sai bacci danta gaji.

Wuraren 2:30 tabude idanunta ahankali sabida shegen yunwan datakeji, dakin da hasken wuta hakan yasa ahankali ta tashi zaune sauka tayi daga kan gado tabude kulan abincinta dabata ci jiya da daddare ba, yatsine fuska tayi danji tayi batasoncin abincin tamaida tarufe ledan chocholate nata ta dauka tabude ciro chocholate guda uku tayi sannan tabude jakan school nata tafito da books dinta tana duba abinda aka musu tanaci saida tacinye tass sannan ta tashi ahankali tasake hawa gadon nan da nan bacci yay awon gaba da ita.

4:30 Abee yafito saida yatada kowa sannan yakoma dakinta knocking yayi tareda bude kofan ahankali ledojin chocholate daban daban kusan 10 dayagani akasa yasa yakalleta tana kwance kan gado tadan rufa tana bacci ta peacefully, katon ledan chocholate din yakalla dahar ya rage yawa sannan daganan inda ya tsaya yace “Ke! Kee!” Firgigit tabude idanunta ahankali tareda dan turo baki saikuma chan kaman wacce ta tuna abu bude idanubta tayi tass ganin Abee ne ba Gwaggo ba yasa dasauri tamike tsaye tawuce bayi Abee yajuya yafice.

Wuraren 7:00 tabude kofan dakinta ahankali tafito ta shirya tsaf cikin kayan makarantan dasuka mata mugun kyau tagoya jakanta abaya hannunta rikeda farin hijab din dabata sakaba tanabin saman da kallo daidai Abee ya hayo sama kallo daya yamata yadauke kai itakuma ta tsaya chak inda take takasa koda motsi saida yakaraso daidai inda take yace “today should be the last time dazan ganki a falo babu hula ko lullubi” yana maganan yawuce dan turobaki tayi tasaka hijabin sannan tawuce tasauka kasa saida tafara gaida Hajiya sannan tai breakfast sosai taci abincinta baruwanta tashi tayi Hajiya tace “ina zaki Imrana dazai saukeki baima fitoba” ahankali tace “zan zauna awaje ne inga rana” murmushi Hajiya tayi tace “tom jeki” wucewa tayi tabude kofa tafita waje Kausar tabita da harara ahankali take kallon ko’ina na tsakar gidan tana kallon yanda gardener dinsu ke zubama flowes ruwa, juyawa tayi tayi wajen gate nasu tabude karamin gate din kadan tana leken waje batasan mesaba hakanan taji kaman wani abu na janta zuwa wajene ahankali tasa kafanta tafita waje wani sanyi taji yashigeta ahankali tadaga kanta tana kalle kalle titin estate din shiru babu motoci dan duka duka yanzu is 7:15, jitayi kaman ana kallonta ahankali yasa ahankali tajuyo da kanta takalli gidan dake kusada nasu chak taji numfashinta ya tsaya.

Mandawari tagani yana tsaye gaban gate nasu sanye dawani rigan jersey na Liverpool dark blue dawani farin short bathroom slippers ne a kafanshi hannunshi rikeda iPhone 14 dayakai kunnenshi da alamu waya yake amman idanunshi kyar akan na Lujain dabai taba tunani zai gani ba dan duka duka ko 20min baiyi da zuwa duba aikin da akeyi agidan ba.

Wani kalan sauke numfashinta Lujain tayi takai hannayenta dasauri ta goge idanunta dan tanaso takara gasgata ba gizo idanunta kemata ba Mandawari take gani yanzu haka agabanta jingine dawata mota black yana waya, ganin still shine yasa taji gabanta nawani irin mugun gudu takasa koda motsi, kusan 2minutes sukayi tana kallonshi yana kallonta yana waya sannan yazare wayan daga kunne awulakance yamata alamu da hannu datazo nan, nuna kanta tayi tace “ni?” Gyadamata kai yayi batare dayace eh ba, gabanta nafaduwa sosai tafara tafiya

ahankali takarasa gabanshi ta tsaya tana kallonshi, cikin sigan yanga yace “why are you looking at me like that kinsanni ne”? Wani kalan lumshe idanu tayi tabude ga muryanshi nan sak wanda takeji idan yana live video batare daya kyafta ko idanu ba tana kallonshi tace “nasanka” tsareta yayi da idanu hakan yasa tace “you are Mandawari, kana buga kwallo, kai player Liverpool ne, sannan kana bugama Nigeria, ina following naka a IG, my name is Lujain and I am your biggest fan” takarashe maganan tana gasping breath tana wani kalan kallonshi kaman zata hadiye shi da idanu, dan yatsine fuska yayi yadau wayanshi yadan daddana batare daya kalleta ba yace “my biggest fan can’t be this ugly” dasauri takalleshi looking confuse, janye wayan dayake dannawa yayi daga fuskanshi sannan yakalleta awulakance yanunata da wayan dake hannunshi daga sama har kasa yace “I mean look at you, you are so soo fat, I don’t think ko mai cikin 5 months takaiki katon teba, so please excuse me go and loose weight saiki dawo kimin magana” yay maganan tareda juyawa yabude kofan motanshi ya shige tareda jan motan da gudu yawuce yabar anguwan  daidai hawaye na zubomata sharrrr, “ana kiranki” taji muryan Kausar hakan yasa tajuya da sauri hada idanu sukayi da Kausar, Kausar zata juya takoma ciki dasauri Lujain tace “Kausar” hakan yasa Kausar ta tsaya tana kallonta karasawa wajenta Lujain tayida sauri, bakin Lujain har rawa yake cikeda wani kalan damuwa tace “Kausar dan Allah kifadamin gaskiya, please inada kiba”? Tsayawa Kusar tayi tana kallon fuskanta ganin yanda idanunta sun cicciko da hawaye ga damuwa karara afuskanta yasa tace “ke baki sani bane kike tambayana” juyawa Kausar tayi zata wuce dasauri Lujain tarike mata hannu tace “dan Allah kifadamini gaskiya nasan you don’t like me so you will tell me the truth” dan shiru Kausar tayi yanda taga she really wants to know yasa tace “eh kinada kiba Lujain” kaman jira Lujain take hawayen idanunta ne suka zubo dan zaro idanu Kausar tayi tana kallonta tace “Waike lafiyanki kalau kodai kinada aljanu ne” sakin hannun Kausar tayi daidai lokacin Abee yabude kofa yafito Kausar tayi wajenshi tace “Abee waje taje tana kuka” dan kallonta yayi yanda take tsaye awajen gate takai hannunta kan fuskanta tana sharewa kawai yawuce wajen motanshi hakan yasa Lujain ta taho tashiga motan Abee yaja motan suka tafi harsuka kai school baice mata komiba sauka tayi tashiga ciki yabita da kallo kafin yatada motan yawuce shima.

EPISODE 27

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Ranan har aka tashi daga school tarasa abinda kemata dadi koda taje lunch takasa cin abinci sosai, 4 suka tashi tadauki jakanta tafito daga ajinsu tundaga nesa tahango Abee tsaye jikin motanshi yana sanye da suit nashi black yasaka wasu bakin glass a idanunshi wayanshi akan kunne yana magana ahankali take tafiya harta karaso inda yake tasauke kanta kasa tana wasa da yatsunta murya chan kasa tace “ina yini” wani kalan kallo yamata sannan yashiga cikin motan itama zagawa tayi tashiga yatada motan suka tafi, tunda suka shiga estates nasu take kallon gidan Mandawari dataga gate din arufe horn Abee yayi aka bude musu gate suka shiga cikin gidan parking yayi tareda kashe motan dan juyowa tayi ta kalleshi daidai shima yadan kalleta ganin bata bude kofa tafita ba, sauke kanta tayi kasa tashiga wasa da yatsunta kaman yabude kofa yafice abinshi saikuma yace “me kike bukata”? Dan dago kanta tayi takalleshi ganin ita yake kallo yasa ahankali tasauke kanta kasa tana wasa da cute white chubby fingers dinta dakenan gyare tsaf murya chan kasa kaman batason abinda zata fadi tace “dama….dama…..” saikuma tai shiru batasan tayaya zata tambayeshi kudiba, dan dago kanta tayi ganin kallonta yake yasa tadauke kanta dasauri tace “I…..don’t have any money Uncle……” taidan shiru realizing this is the first time take kiranshi kumama wai Uncle abin yamata wani banbaran abaki, dan kallonshi tayi kadan suka hada idanu dan lankwashe kai tayi kaman wata macijiya murya chan kasa tace “kuma…..kuma magani nakeson in saya” kallonta yake kyar batare dayace komiba, dan dago kanta tayi suka hada ido murya chan kasa tace “uhmmm….maganin rage ki…kiba” dan lumshe idanu yayi yakalleta sannan yace “a ina ake saida maganin”? Dan kallonshi tayi kana ganin kwayan idanunta kasan batasani ba, ahankali tace “nima bansani ba amman ai za’a samu a kasuwa” wani kalan kallo dayamata yasa tamaida nata idanun kasa yace “kintaba ganin yaran gidanmu sunje kasuwa?” Girgixamai kai tayi, ahankali yace “kin taba zuwa kasuwa?” Sake girgixamai kai tayi tace “amman Gwaggo na na zuwa tana sayo magunguna da yawa nasan zan samu nima innaje” tunda take maganan yake kallonta yace “did anybody told you kinada kiba a school ne”? Sake girgixamai kai tayi tace “a’a” ahankali yace “maisa kikeson kisha maganin rage kiba”? Batasan mesaba hakanan taji takasa fadamai karya ahankali tace “Mandawari bayason mace mai kiba” yadade yana kallonta harsaida tadago kanta takalleshi dan gajeren tsaki yayi yace “yabaki maganin rage kiban to” yay maganan yana yunkurin tashi dasauri tace “namishi magana”? Dan tsayawa yayi saikuma yajuyo yakalleta yace “I told you zaki iya kome kikaga dama I don’t consider you my wife and you are not my wife, dazaran this whole thing yalafa aka kamo yaron zan rabu dake” wani kalan murmushi tayi daya lobar mata da dimples nata tace “thank you Uncle” tai maganan tana bude kofa tafito tawuce ciki tana tafiya ahankali yadan bitada kallo.

Hajiya kadaine a falo da Maman Aneesarh ahankali tace “ina yinin ku” murmushi Hajiya tayi tace “sannu da zuwa” Aneesarh data gani taduka tadauka tana murmushi tace “zomuje dakina” murmushi Mamanta tayi tace “wanan saita batamiki daki wlh da barna” murmushi tayi tace “dan Allah kibarni natafi da ita Allah ina sonta” Maman Aneesarh tace “shikenan kuje” wucewa sukayi sama Abee yashigo shima gaida Hajiya yayi, Hajiya tace “sannu da zuwa Imrana” ahankali Maman Aneesarh tace “sannu da zuwa Yaya” Gyadamata kai yayi yawuce sama, Maman Aneesarh takalli Hajiya tace “Hajiya Ya Imrana is so nice towards this girl” Hajiya tace “Imrana

has always being nice to kowa, banbancin Babba mai hankali kenan da kananun yara samari, Lujain is just like Kausar kozai wulakantata bazai iyaba dan kaman diyar cikinshi ne bazai iya imagining wani ya wulakanta mai Kausar ba, nasan Imran dina dudda bayason Auren nan bazai taba cutar da ita kokuma yaga abin cutarwa yabari ya cutarda ita ba" Maman Aneesa tace "saisa yasata a makaranta mai tsada ko su Kausar ba makarantan turawan nan sukayi ba" Hajiya tace "inba irin makarantan nan ba awanne za'a sata yarinyar da fuskanta ya zagaye yanar gizo so kike kullum adinga dukanta ta tsani makaranta gabaki daya taki fita" ahankali Maman Aneesarh tace "Hajiya ni tausayi yarinyar ke bani koda zamuso zamansu da Ya Imran tayaya zata fara kula da Ya Imran? Babu abinda ta iya wannan saidai shi yakula da ita ai" Hajiya tace "daga next week duk idan tadawo daga makaranta zan dinga sata tana shigowa kitchen kuna koyamata abu daya biyu haka harta kware" kallonta Maman Aneesarh tayi tace "Mama kinason auren su ne?" Hararanta Hajiya tayi tace "kin isheni da tambaya amman abu daya zan fadamiki babu Babba dazai cemiki yanason mutuwan aure duk Auren da aka daura fatanmu shine yadaure har abada, idan zamansu tare Alkhairi ne Allah yahada kansu kullum shine addu'a na".

***

Olusay ke tuki suka shigo estate din, horn yayi gaban gidan gateman yabude musu suka shiga ciki Olusay yace "wow gidan yay kyau wlh Man" yadan kalleshi ganin yana cikin IG, karasa parking yayi ganin Mandawari baima saniba yasa gently yakai hannunshi yadaura akan shoulder nashi hakan yasa dasauri Mandawari yakalleshi yace "ohh harmun shigo"? Olusay yace "kanachan kana kallon hoton stalker naka yaza'ayi kasani" kallonshi Mandawari yayi, ahankali Olusay yace "can I talk to you Man I am serious"? Dan yatsine fuska yayi yana cire sitbelt yace "what"? Dan jim Olusay yayi dan baisan how he's going to take the magana ba ahankali yace "first of all Muhammad I don't know your reason na sayan gida right next to gidan da stalker dinka ke aure, nabiyu you saw everything mezakayi da matan aure yarinyar data Riga tayi aure? Thirdly kasan your Mom bazata taba bari ka auri yarinyar that went viral online hakaba, and nahudu kariga kayi loosing chance dinka da bakin wulakanci for the past how many years yarinyar nan namaka magana wulakancinka yahanaka kulata sai yanzu bayan an mata aure ne zaka fara sonta what's all this Man? Mezakayi da wannan yarinyan kanada thousands of mata har yan film dake sonka sai wannan da aka mata unfortunate Marraige din nan zaka wani fara so" shiru Mandawari yayi saikuma chan yace "you want an honest answer?" Gyadamai kai Olusay yayi ahankali yace "I buy this house triple amount na gidan nan because of the girl dan wasu harsun sayi gidan nakara kudade, sannan kai kanka you just call the marriage unfortunate one kawai anyishine dan ayi blocking mutane from saying shit akan honest mistake datayi well koma Iskancin tayi da mutumin I know he must be the one to force her dan that girl love only me, and again what made you think Mom harta isa tagayamin ga wanda zan aura ga wanda bazan aura ba bayan ita taje tayi aurenta da Dad dina yarasu? She have no right over me, lastly kowa yarinyan nan ta aura I don't bloody care she belongs to me! Just me, watch and see how I win my girl and shape her to abinda nakeso that fat everything she will loose it, idanma takasa dakaina zan kaita amata tummy tuck" dan murmushi yayi yace

“how is my welcoming party going”? Tabe baki Olusay yayi yace “I know how stubborn you are just be careful, mijin yarinyan nan is not our mate that’s number one tsoho ne, nabiyu kuma he’s a soldier, a retired old soja” dan dariya Mandawari yayi yace “that’s more of the reason why I want to save her, mezatayi da tsoho dakeda yaran dasuka girmeta? She’s to young and fresh for him, bata sonshi ni kadai takeso, just sit back and watch how I open her eyes and show her the world” “hmmmm” Olusay yace da mamaki yabude mota yafito shima Mandawari yafito Olusay yace “ni bantaba ganin mutum irinka ba yarinyar dabaka nuna mata so bamaka kulata” dan tsaki yayi yace “leave me alone please, kaji da kanka” taba yaciro yakunna yanasha Olusay yawuce ciki abinshi, saida yagama sha ya yarda karan ya shiga ciki.

EPISODE 28

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Wuraren magrib tabude kofanta tafito tana daure dawani pink towel a kirji rikeda Aneesarh datai bacci Kausar tagani dazata shiga dakinsu dasauri tace “inane dakinsu Aneesarh”? Kallonta Kausar tayi saikuma tamata pointing dakinsu Aneesa wucewa tayi tashiga Maman Aneesarh naciki tace “laaa tayi bacci” gyadamata kai tayi tana kallon wayan Maman Aneesarh dake kan gado, karban Aneesarh tayi ta kwantar da ita sannan ta tashi takalli Lujain dake kallon wayan tace “Ya akayi Lujain”? Ahankali tace “dan Allah na ari wayanki nakira Gwaggo na”? Dan murmushi tayi tace “to dauka kije ki kirata” wani kalan tsalle tayi cikeda farinciki tace “nagode Mom Aneesarh” daukan wayan tayi da gudu tafita tana saka number Gwaggo data haddace aciki tai dialing tabude kofan dakinta tashiga daidai wayan na ringing Gwaggo tadauka cikeda ihu yanda take waya tace “hello” dan murmushi Lujain tayi dayasa hawaye yataru akan idanunta murya chan kasa tace “Gwaggo” cikeda ihu Gwaggo tace “jama’a muryan Lulu nakeji”? Gyadamata kai Lujain tayi kaman jira take tawani kalan fashe da kuka itama Gwaggo fashewa tayi da kuka tace “wlh inda badan Babanki nina haifeshi ba da tuni na tsine mishi, tun Washegarin ranan da aka kaiki gidan miji naji ina baran iya rayuwa bakiba, ranan kasa bacci nayi nayi nayi da Babanki yakawoni gidanki yaki da asussuba kafin natashi yake fita baya kara dawowa sai dare bayan nai bacci, keto ya isa daina kukan hakanan kinji” gyadama Gwaggo kai tayi ahankali, murya chan kasa tace “Gwaggo dan Allah kizo kitafi dani gida” Gwaggo tace “namiki alkawari ko ana ha maza ha mata sainazo kafin satin nan yakare nadubaki kinji daina

kukan kinashan maganin dana daddaka miki nasa miki a akwati"? Turobaki tayi ashagwabe tace "ni baram sha….." daidai lokacin aka bude kofan dakin Abee ne yana tsaye sanye da kananun kaya riga da jean sun mishi wani kalan kyau sai kamshi yake ganinshi yasa dasauri tace "Gwaggo bye bye" takatse wayan dasauri tana zaro idanu, wani kalan kallo yamata tareda mikamata hannu alamun tabashi wayan, tashi tayi ahankali tazohar gabanshi sannan tabashi wayan yajuya yafita.

Koda akai magrib Abee zamanshi yayi a masallacin danjin ta'aleem da akeyi kan zamanta kewa da hakkoki mutane, saida aka gama tass malam yabada daman tambaya daga baya wani yadaga hannu hakan yasa Malam yace "yi tambayanka" dan sosa gemunshi yayi sannan yakalli Malam yace "Malam ni sonake nasan hukuncin tsofaffin dake auremana yammatan mu" duka jama'an masallacin juyowa sukayi suna kallonshi yahade rai banda Abee dake duba littafin hannunshi, Malam dake kallonshi yace "ban gane tambayanka ba yan samari" dan yatsine fuska Mandawari yayi yace "yanzu saikaga tsofaffi misali irinku malam na auren mata dakun haifesu kusan sau biyar mukuma yara mekukeso mu aura me atambayata dabaka ganeba"? Sai alokacin Abee yadago kanshi dan tambayan sounds so disrespectful to Malam dan Malam ba karamin mutum bane, shima Mandawari kyar idanunshi akan Abee, yanda yake kallon Abee yasa Abee ya gyara idanunshi akanshi, gyaran murya da Malam yayi a speaker yasa Mandawari ya janye idanunshi dagakan Abee dake kallonshi kyar yakalli Malam, Malam yace "shidai aure na farko Halas ne yan samari, dudda dai bansan mesa kayi irin wannan tambayan ba dan ba darasin mukeba amman dai abinda nasani shine wacce baraka iya aura ba aduniyan nan shine wacce take muharamman ka, idan kuma ana maganan Auren yara ne annabin mu Annabin Tsira Muhammad tsarki yatabba agareshi ya auri Yar yarinya Aisha kuma mu koyi mukedashi, jama'a atashi sahu" tashi sukayi akai salla ana idarwa Abee yafito dan yanada business meeting dazaiyi a zoom by 9, harya zo zaishige gida yaji ance "Yallabai" chak Abee ya tsaya saikuma yajuyo ahankali, Mandawari ne yataho tareda Olusay dayay hanyar gate nasu, jallabiya ce ajikinshi yakaraso gaban Abee hannu yamikamai yace "kasanni"? Wani kalan kallo Abee yamai tsaf yaganeshi from the first glance dayamai a mosque, hannu Abee yakawo zai bashi kaman jira Mandawari yake with so much disrespect and humiliation yajanye hannunshi yarugume hannunshi a kirji, hannunshi Abee yakalla daya kaimai su gaisa dake nan acikin thing air ahankali yaja hannunshi ya maida jikinshi yazubama Mandawari idanu, baisan mesaba jiyayi gabanshi yafadi amman daurewa yayi with so much courage yace "you took something that belongs to me Mr Imran, kuma na tabbata fada da kananun yara irinmu dazaka iya yara damu is not ur thing dan haka I come to tell you in peace ka saki babe dina daka daura lokacin da abin nan yasameku I wasn't in Nigeria yanzu nadawo I want my woman back I want to marry her" wani kalan kallo Abee yamai saikuma yay folding hannunshi akirji yana kallonshi, Mandawari yace "yanzu ma nasameka ne namaka magana out of respect inba hakaba" anatse Abee yace "mezakayi"? Kallonshi Mandawari yayi yace "I will defame you! I will scatter everything you've ever stood for" dan murmushi Abee yayi iya lips nashi sannan yajuya yawuce anatse wani abu Mandawari yaji ya tsayamai awuya kaman yabishi ya chakamai wuka sai yanzu daya tsaya gaban Abee face to face kawai yaji yawani tsaneshi wani kalan mugun kishi nacinshi dan ko kadan mutumin doesn't look old gashi he's so handsome gashi so neat kayan

dayake jikinshi tundaga kan slippers na kafanshi are designers, kamshin dayake koshi dayake takama yafi kowa using turare baikai Abee kamshi ba, wani kalan dunkule hannu yayi yadaki iska sannan yajuya yawuce gida, akan benci mai gadi yasami Olusay zaune Olusay na ganinshi yamike tsaye yace "Man nasanka to be stubborn tun muna yara, but idan kasan kazo anguwan nan ne to make trouble ni zan tattara nabarmaka gidanka, this man baida any business to do with you and yet you want to make trouble dashi akan mene ubanme yamaka eh" cikeda ihu Mandawari na tafarfasa yace "he stole my woman from me abinda Yamin kenan" cikin sauri Olusay yace "woman din dabaka taba cema kanaso ba or respond to her messages, this is not good Man, trust me this is not good at all" hannu Olusay yakai zai tabashi wani kalan bugemai hannu yayi yawuce ciki yana tafarfasa tsayawa Olusay yayi so worried Kodai yakira Mom yafada mata abinda ke faruwa ne amman yay haka Man will never forgive him, shi yasan Man always view her message dan shinema yafadamai about Lujain amman baitaba fadamai yana sonta ba saima wulakanci dakin kula yarinyar, saida wannan sex tape da news na aurenta ya yada social media shine fa tundaga ranan Mandawari yafara having sleepless night.
***

Falonsu yashiga da sallama chan kasa Musty yagani da Harun sunacin tuwo, Hajiya kadai yagaida yamusu mugun kallo yawuce sama, Hajiya tace "kudai kuna kokari da wannan abokin naku" tashi Musty yayi yace "cigaba daci Harun bari najawoshi ya sauko kasa" daidai Abee na zama gaban desk nashi Musty nashigowa ciki yace "waikai tunda kayi auren nan nakasa gane kanka" wani mugun kallo Abee yamai yace "I told you Musty, kasanni Musty banson aure let's not even go there idan wata ne maybe I can even manage Auren na zauna not Auren little girl like this da dan karamin yaron saurayinta zai tareni this night yana threatening dina, what is all this rubbish what kind of mess kuka sani ciki haaa? At this stage some stupid small boy da aka haifa jiya jiya zaizo yatareni yanamin maganan banza can you imagine"? Yanda Abee ke magana zakasan he's really pissed hakan yasa Musty yace "wait Imran I don't understand me kake cewa? Waya tareka wani boyfriend kake magana"? Cikin dan ihu kadan Abee yace "her boyfriend dashine the reason behind abinda yasa taje toilet na maza mana taxauna tana kallon live video nashi Muhammad Mandawari" shiru Musty yayi yana kallon Abee dan shi dama dayashigo anguwan dazu Hamza ke fadamai sunyi neighbor wani footballer baima tsaya jin waye ba sabida Hajiya daketa kwalamai kira, one thing da Abee ya tsana to the core arayuwanshi is raini ya tsani raini da rashin kunya, dafe kanshi yayi saikuma yadago yace "how far about the tracking dasu Abdul keyi idan bazamu iyaba zan turama contact dina number a USA cus I can't wait for all of this shit to be over narabu da yarinyar nan data shigo rayuwana tahanani kwanciyan hankali I am tired Musty I am tireddd" yay maganan yana kabar da keys na motanshi da wayanshi dake kan desk din kasa, dasauri Musty yazo yadafashi trying to calm him down yace "calm down Imran, fushinka is not good for you and kowa dake tareda kai, calm down please" dan ajiyan zuciya Abee yasauke ahankali Musty yace "what happen tell me" kaman Abee bazaiyi magana ba saikuma yafadamai komi shima Musty baci ranshi yayi yace "I don't care koshi waye what gave him the gut dazai tare soja yanamai magana anyhow, lemme go and lock him up wlh sainai uselessing kafafuwan nan nashi na kwallo " Musty yazo zai wuce dasauri Abee yarikeshi yace "common mu yarane dazamu biye musu, he's just a child let him

be please, is not easy karasa abinda kake so cikin dare daya to some extend I understand how bittered he's" dasauri Musty yace "her grandmother told me baitaba kulata ba all this childish crush Lujain kemai" yatsine fuska Abee yayi yace "that's non of my business, I've taken care of her, nasata a school da babu wanda zai bully nata, nayi securing waec nata and neco I am just waiting waiting for the whole thing to be over nagaji" yay maganan ahankali, murmushi Musty yamai yace "ya isa tashi muje falo muci tuwo tare" yatsine fuska Abee yayi yace "baran ci ba" Musty yace "Allah saikaci" badan yasoba yatashi yabishi suka fita falo tare, sai wajajen 11 sukabar gidan hakan yasa yarufe ko'ina yawuce sama ko dakin da Lujain keciki bai kalla ba.
EPISODE 2️⃣9️⃣

Jama'a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Around 1 tafarka daga bacci sabida mugun yunwan datakeji rabonta dacin abinci tun lunch dataci a school shima ba sosai ba taci, yanda Mandawari yagaya mata tacika kiba taje tarage kiba kafin takulashi yadameta tayi alkawarin zata rage kiba, barata dingacin abinci sosai ba, kulolin abincin da aka kawomata jiya da daddare takalla amman taki zuwa wajen, kife cikinta tayi ahankali tanajin yanda cikin ke sokanta amman tadaure tana lumshe idanu, ganin yaki denawa yasa ta tashi tadauki bottle water tabude tasha sosai sannan takara kwanciya tana shafa cikinta da hannunta dake cizonta cikin wani kalan murya tace "wayyooo cikina wauyooo" juyi kawai take akan gado sai wajajen 3:00 bacci yay awon gaba da ita, 4:30 Abee yafito, tada kowa yayi saida yatada Kausar yace "jeki tashi yarinyar nan" gyadamai kai Kausar tayi tawuce tafita shima Abee yafita yasauka kasa.

Bude kofan dakinta Kausar tayi takarasa gaban gadon tana mamakin yanda koda yaushe tana daure da towel bubbuga gadon tayi hakan yasa tabude idanunta ahankali Kausar dake kallonta tace "Abee yace kitashi kiyi salla" tashi tayi ahankali ta zauna itakuma Kausar tawuce tafita daga dakin, mikewa tayi ahankali tashiga bayi wanka tayo tafito tai salla sannan ta tashi tashiga saka kaya tana tunanin yau jumma'a zata huta, kayan makarantan ta tasaka batare datasa safa

ko hulaba tafito sai kamshin turarukan data fesa take masu bala'in dadi, gaban dakin Kausar taje tadade tsaye sannan tabude kofan ahankali tashiga ciki Kausar dake saka dogon Riga tajuyo dasauri takalleta ta tace “mehaka kika shigo mini daki” girgiza matakai Lujain tayi saikuma ta taho cikin dakin zuwa gabanta ahankali tace “mesa kika tsaneni baki sona”? Tai maganan tana kallon fuskan Kausar hararanta Kausar tayi takarasa saka riganta tajuya tadauki dan kunne tasa ahankali Lujain tace “eh mesa” juyowa Kausar tayi dasauri tace “kinason ki sani, to sabida ke sunan Babana Abee yabaci aduniya, because of you mahaifina is suffering, bayan komi laifinki ne, kene kikazo kampanin shi amman ba'a duba hakaba sannan aka kuma kakabamai Auren ki akanshi sabida mugunta irin naku da yan gidan ku” hawaye ne yazubo daga idanun Lujain dasauri tasa hannunta ta goge takalli Kausar tace “kinsan mesa naketa son miki magana sabida ke kadai nagani agidan nan datake nan kaman matsayin yayyuna su Ya Samira, kin dauka I am happy with all this ne, kaman zan mutu nakeji, nima nagaji nagaji dakomi” saikuma tafashe da kuka wani iri Kausar taji dan tanada bala'in tausayi dauke kanta tayi tace “nidai me kikazo mini adaki mekikeso” hannunta Lujain tasa tashare hawayen fuskanta tass tace “sonake kiduba min recipes na rage kiba awayanki kibani narubuta inaso narage kiba ne” dan kallonta Kausar tayi ganin yanda take kallonta yasa Kausar tace “kiba halitta ce, haka Allah ya yiki maisa kikeson wahalar da kanki”? Girgiza kai tayi tace “nidai dan Allah kidubamini inda inada waya bazanma zo wajenki ba” bala'in tausayi tabama Kausar wayanta tadauka tashiga google tamata browsing sannan tabata wayan da memo da byro tace “write it down” zama tayi abakin gadonta tashiga kwafewa da saurinta Kausar duk tana shiryawa tana kallonta komesa takeson rage kiba oho kuma kiban yamata kyau sosai da chubby kumatunta yanzu idan tarage kiba tai muni fa oho itadai baruwanta, gama rubutawa tayi tamike tsaye tana ijiyemata wayan akan gado tai murmushi sosai dayasa Kausar ta tsareta da idanu sabida yanda dimples dinta ke lotsawa tace “thank you Kausar” sannan tawuce tafita, dakinta takoma tadauko jakanta da hijab tashiga saukowa lokacin babu kowa a falo jakan ta ijiye akan kujera sannan takalli kitchen dinsu datagani abude tawuce tashiga ciki Anty Binta datagani tsaye tana aiki yasa tai murmushi tabi kitchen din da kallo ganin yanda tahadu tace “good morning” murmushi Arty Binta tayi tace “kin tashi lpy Lujain mekikazo yi a kitchen”? Dasauri tai wajen Anty Binta paper tanuna mata tace “weight loss smoothie zan hada” kallonta Anty Binta tayi tace “kewayace miki kirage kiba so kike Gwaggon ki taganki tace bamu baki abinci” murmushi tayi batace komiba Anty Binta tace “ai shikenan fruits duka na fridge ga blender anan” dasauri tai fridge, celery tadauko, da green apple, cucumber dakuma ginger tahada tai blending Anty Binta sai kallonta take one thing datagani is tanada tsafta kaganta zaka dauka bata iya komiba amman ta iya danta yayyanka abinta tasa a blender ta blending Anty Binta dakanta tabata bottle mai kyau da straw tajuye aciki tace “Allah bada sa'a nidai banga me zaki rage ba” dan turo baki tayi tace “flat tummy da fats” dan hararanta Anty Binta tayi tai murmushi takai bittle na baki tazuko tasha taba tabe baki ko kadan baimata dadi ba amman sabida yanda takeso ta burge Mandawari rufe ido tayi ta shanye tass sannan tawanke giran da blender dasauran kwanukan wajen Anty Binta tace “debi chips naki kije dinning kici” girgiza mata kai tayi tace “a'a ni nakoshi” wani kalan kallo Anty Binta tamata tace “Lujain what's all this kaman wacce tai wani mafarkin abu yunwa kikeso kifara hora kanki dashi sokike naje nafadama Ya Imran abinda kikeyi”? Dasauri Lujain ta girgiza kai tace “to zanci Anty please karki fadama kowa” tai maganan tana daukan plate chips kadan tadeba tasa kwai ma kadan kaman ba Lujain ba Anty Binta tace “tea fa” girgizamata kai tayi

tace “idan nadawo shi zan sha” a kitchen din tazauna kan kujera taci abincin tass sannan tawanke plate ta taya Anty Binta kwaso kula tafito dasu falo Hajiya sai murmushi take tana samata albarka afalo duk akaci abinci banda Abee dabai dawobama yana gym dinshi ita tana kitchen wajen Anty Binta, Kausar ne tashigo kitchen din tace “Uncle Hamza yace kizo mutafi yau shizai kaiki school” wanke hannunta tayi tace “Bye Anty” bye Anty Binta tamata tana murmushi sanan tawuce tafita zama afalo tayi tasa safa da takalmin makaranta sannan tasaka hijab tagoya jakanta tafita itada Kausar dake daddanna wayanta motan Uncle Hamza suka shiga, motar mai kyau benz amman ba tinted bace, murmushi yama Lujain yace “Amaryan Ya Imran” sauke kanta tayi kasa bata sake cewa komiba suka fito, tsaye taga Mandawari a kofar gidanshi yauma yana sanye da wani rigan jearsay da gajeren wando, hada idanu sukayi ga mamakinta wani dan karamin murmushi yasakin mata batasan lokacin dataji wani farin ciki ya lullubeta ba, hannu yadaga mata alamun bye bakaramin mamaki tayi ba noke kanta tayi batare datamai bye ba, ita suka fara ijiyewa a school sannan yawuce yatafi da Kausar school.
EPISODE 30

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Wuraren 11 yay parking motanshi wata crazy Brabus jeep agaban school din, yadan dade aciki sannan yabude kofa ahankali yafito sanye yake da kayan kwallo farare sun mishi kyau sosai kitson kanshi ya gyara ya shafa mai sai kyalli suke, zare glasses na idanunshi yayi yakarasa zuwa wajen security dake gaban gate din suna kallonshi daya daga cikinsu zaro idanu yayi yace “ohhh my God Mandawari look guys” dasauri sauran securities din suka kara kallonshi dukansu bashi hannu sukayi dan murmushi yayi daya bayyana hakorin makkan bakinshi daya daga cikin security yace “Selfie please Mandawari” murmushi yayi yace “yeah sure” daukan hotuna biyu sukayi yace “it’s okay sauri nake” dasauri sukace “mekazo yi makarantan mu”? Dan murmushi yayi yace “wajen sister na nazo sako zan bata it’s urgent” security yace “laaa kanada sister a school din nan wacece what’s her name”? “Lujain Muhammad” daya daga cikinsu yace “wani class Kodai sabon zuwan nan da aka kawo” dudda baisani ba gyadamusu kai yayi, dayan

yace “let’s go kashiga office kazauna akira maka ita” girgiza musu kai yayi yace “naah zan jirata anan jikin motana sako kawai zan bata” Babban su yace “jeka kira mishi ita yisauri” murmushi Mandawari yayi yaciro bandir na yan 1k sababbi fil yabama babban cikinsu sai murna suke suna godiya yawuce yakoma jikin motanshi ya tsaya tareda folding hannunshi akirji yana kallon gate din.

Tana zaune a aji cikinta ciwo yake sosai sabida yunwa amman takicin abinci har awurin lunch, daga bakin aji security ya tsaya yace “Lujain Muhammad yayanki na waje come with me” teacher dake koyarwa juyawa tayi takalleta tace “tashi kije” ahankali ta tashi gabanta hakanan taji yafadi to me wannan Uncle din yazo yamata yanzu, ahankali take tafiya Security nagaba tana bayanshi harsuka fita gate din ko kadan bata lurada Mandawari ba security ne yamata pointing inda yake tsaye yace “ga yayanki chan jeki karbi sakon” juyawa tayi takalli inda aka nuna mata ido da ido tayi da Mandawari wani kalan faduwa gabanta yayi ta tsaya chak tana kallonshi, dan murmushi yasakin mata hakan yasa ahankali tasaki wani kalan cute smile batare dataje wajenba dakai yamata alamu datazo gently tafara tafiya tana tahowa yabi cikinta da kallo dayaga baiyi girman dayayi jiyaba harta karaso gabanshi ta tsaya tana murmushi akunyace, tsareta yayi da idanunshi she’s breathtakingly beautiful, gawasu cat eyes manyan dayaji yana neman yasashi ya shide daurewa yayi yahadiye murmushin dayakeyi yace “har yanzu kinacin abinci dayawa ko cus you are still very fat” wani iri taji ahankali takalleshi batare datace komiba, hannunshi yasa acikin aljihun wandonshi yaciro iPhone 12 Pro max yamika mata, kallon wayan tayi dasauri saikuma takalleshi murya chan kasa tace “mezanyi dashi”? Tsareta yayi da idanu yace “I want to talk to you today ko bazaki amsa bane”? Girgizamai kai tayi ahankali batare data amsaba tace “mezance agida”? Dan daure fuska yayi yace “ke yarinya ne dakowa saiyasan nabaki waya karba kada raina yabaci inba hakaba zance nafasa auren ki” dawani kalan sauri takalli fuskanshi, gira daya yadaga mata yace “ko kindaina sona yanzu”? Wani kalan murmushi tayi ahankali akuma dan kunyace tace “inayi” murmushi yamata yace “to karba” ahankali tasa hannunta dake rawa sosai ta karba gabanta nafaduwa zuciyanta yaki natsuwa, kallon security dake kallonsu yayi yace “hide the phone and go back to your class I will call you by 7 dot na yamma bye” yajuya yashiga motanshi, gently ta tura wayan aljihun uniform nata tajuya takoma aji tana tafiya ahankali she’s super happy to see him amman kuma wani bangaren zuciyanta sai tsinkewa yake idan ta tuna she just  collect phone from his hand wayama IPhone zuciyanta yaki natsuwa harsuka tashi by one na rana.

Jakanta tadauka tareda goyawa abaya tafito ahankali take tafiya tundaga mota Hamza ke kallonta, Lujain nada wani kalan kyau da idan ka daura idanunka akanta barakaso kadaina ba, batada fada baiganta dawani damuwa ba, deep down he wish Ya Imran will settle down da yarinyar yadaina kallon karantan ta zaiyi farin ciki hartazo tabude kofa baisani ba saida ahankali tace “ina yini” sannan yayi murmushi yakalleta yace “ya school kinyi karatu da kyau dai ko” murmushi tamai tareda gyadamai kai bata kara cewa komiba sundanyi nisa akan titi yace “do you need anything nasaya miki” girgizamai kai tayi tace “a’a nagode” murmushi shima Hamza yayi ganin bata sake dashi ba batare daya kara cemata komiba har sukakai gida sai kallon kofar

gidansu Mandawari take she just wish inama zata ganshi, parking yayi tasauko tawuce ciki Hajiya kadaine a falo tanajan charbi ganin Lujain saida tai murmushi itama dan murmushi Lujain tayi tazo wajenta tsugunnawa tayi ahankali tace “ina yini Hajiya” shafa addu’a Hajiya tayi tace “sannu da zuwa Lujain, jeki chanza kaya kiyi wanka zansa mai aiki ta kawomiki abinci sama ya makarantan” ahankali tace “Alhamdulillah Hajiya” “sannu kinji Allah miki Albarka” ahankali tace “Ameen” tashi tayi ahankali tanadan yatsine fuska sabida yanda cikinta kemata ciwo tawuce sama dakinta tashiga dayake a gyare tsaf kayan makaranta tacire tashiga bayi wanka tayi tafito hijabi tasaka tai salla akan dadduman ta kwanta tana kallon jakan makarantan ta da wayan ke ciki gently tasaka hannunta tajawo jakan budewa tayi taciro wayan tana juyawa tana kallon daga ganin wayan sabo ne ba’a dade ana amfani dashi ba kunna wayan tayi ahankali hotonshi ne a screensaver tadade tana kallon hoton dan murmushi tayi tarasa mesa take sonshi duk idan taganshi wani kalan farinciki takeji bude wayan tayi ganin babu password tashiga gallery duka hotunan shine wanda yake buga ball da sauransu fita tayi takoma dial calls number dayane awajen da akai saving da Mandawari tadade tana kallon number kaman magic dailing number tayi yana ringing dasauri ta katse gabanta na duka uku uku kirane yashigo wayan ganin shine yasa ahankali tasa hannunta tai picking call din tareda kai wayan kunnenta tai shiru.

Daga dayan bangaren yace “baki iya gaisuwa ba”? Dan murmushi tayi ganin yanda yakeson girma murya chan kasa tace “good afternoon” shiru yayi baice komiba hakan yasa tace “hello” dan lunshe idanu yayi harcikin zuciyanshi yakejin muryanta ahankali yace “tell me everything that happen, karkimin karya kikamin karya I will hate you Lujain, so what happen daga farko zuwa karshe dahar yasa aka auramiki wannan tsohon” dan shiru tayi kaman mai tunani saita shiga bashi labarin duka abinda yafaru har zuwa yau, dan ijiyan zuciya taji yasauke ahankali yace “yataba rike miki hannu” girgixamai kai tayi tace “a’a” dasauri yace “kwana fa a ina kike kwana” ahankali tace “awani daki ni bansan inda yake zama ba” shiru yayi saikuma chan yace “kinason na aureki Lujain”? Dan lumshe idanu tayi tabude su ahankali sannan ta gyadamai kai ahankali tace “eh” murmushi yayi yace “to kicemai yasakeki basai ankamo mutumin ba I am here now kina fitowa zan aureki and make you mine mubar Nigeria” murmushi tayi sosai cute fararen hakoranta suka bayyana lumshe idanu yayi yana sauraron sautin murmushinta dan lunshe idanu yayi yabude yace “nabaki 1 week ki kashe Auren nan kifito lemme marry you, sannan kirage cin abinci look good katon cikinki yakoma flat kinada shape mai kyau amman katon cikinki yahana shape din nunawa dan haka work on yourself kinajina” gyadamai kai tayi ahankali dan murmushi yayi yace “bakice kina sona ba kodai a chat kika iya fadi” dan murmushi tayi zuciyanta namata wani kalan sanyi dan hararanta yayi kaman tana gabanshi yace “tell me now” Murya chan kasa akunyace tace “ina sonka Mandawari” dan dariya yayi datakejin dariyan daga cikin wayan  yace “I am inviting you to my welcoming party gobe zan tura miki address din awaya kizo da bolt zan biya kudin kika iso makesure you look good kada kici abinci sabida cikinki yay flat” cikeda damuwa yace “please loose weight I hate mace mai kiba kinajina” yay maganan authoritatively dasauri ta gyadamai kai tace “to naji” yace “don’t eat anything again sai fruits da daddare and sleep only fruits fruits zaki dingaci yanzu kinji” gyadamai kai tayi tace “tom” ahankali yace “bye saina kira anjima da daddare”.

EPISODE3️⃣1️⃣

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Bin wayan tayi da kallo sannan ahankali ta ijiye wayan akarkashin gado tareda kife cikinta dake mata ciwo sosai sabida yunwa tunda take arayuwanta bata tabajin yunwa irin na yau ba chocholate dinta takalla dake leda lips dinta talashe tareda lumshe idanunta bacci ne ya saceta sai around 6 ta tashi kulan abinci tagani ankawo a injiyemata tashi tayi tawuce bayi alwala tayi tazo tai sallan la’asar sannan ta tashi tareda cire hijabi tana gyara towel din jikinta gaban kulan taje tabude su ahankali, biryani rice ne dayaji naman rago baja baja aciki wani kalan kugi cikinta yayi batasan lokacin data fashe da kuka ahankali ba tana kallon abincin cikinta nawani kalan murdawa dawani kalan sauri tarufe kulan tareda juyama abincin baya tadaura kanta saman gado, bude kofan dakin akayi hakan yasa ahankali tadago kanta Anty Binta ne idanunta kadai takalla tace “why did you cry Lujain menene”? Girgizamata kai tayi alamun babu komi sai kuma hawaye yazubo mata sharrr binta Anty Binta tayi da kallo ganin yanda tai zuru zuru yasa Anty Binta tace “kinyi lunch a school”? Girgixa mata kai Lujain tayi ahankali dan ita har yanzu bata iya karya hakanan ba, hakan yasa Anty Binta tabude kulan datagani adakin na abinci ganin bata tababa yasa ran Anty Binta abace tace “wai what is this behavior Lujain? Cikin gidan nan akwai wanda yamiki complain angaji da abincin dakikeci ne koko muncemiki munaso kirage kibane why will you be hurting yourself like this eh Lujain”? Wani kalan matsiyacin yunwa takeji dayasa takasa hadiye kukan, Anty Binta tadauki kulan gabaki daya takawo gabanta tareda saka mata spoon akai tace “dau abincin nan kici” girgixa mata kai tayi tana kauda kanta gefe tace “ni baran ci abinci ba” shiru Anty Binta tayi tana kallonta tace “sokike nabata dake ko Lujain” girgixa matakai Lujain tayi tana goge hawaye tace “kiyakuri Anty” tashi Anty Binta tayi tace “shikenan nima yau zan tattara nakoma gidan mijina dama sabida ke nadan zauna agidan nan sabida kisake amman tunda you are so stubborn kina neman yima kanki illa shikenan ke kadai kiyi amman zanje yanzu nafadi ma Hajiya sannan nafadama Ya Imran shima” tana maganan tamike dasauri Lujain tarike mata hannu tana kuka sosai tace “dan Allah kada kifada musu Anty” fizge

hannunta Anty Binta tayi tafita daga dakin dan sosai ranta yabaci kana ganinta kasan bala'in yunwa takeji barinma ita da yawanci ita kebata abinci tasan yanda Lujain kedacin abinci all of a sudden tana neman kashe kanta, fuuuu tawuce tasauka kasa Hajiya na zaune tareda Abee da shigowanshi kenan ganinta kadai yasa Hajiya tace "lafiya ranki abace Binta" cikin fushi Anty Binta takalli Abee daya zubamata shima yana jira yaji meke faruwa tace "Ya Imran ga matanka chan na neman kashe kanta" wani kallo daya mata yasa tadan lumshe idanu tabude tace "I mean Lujain tun safe bataci abincin kirki ba, smoothie tayi na celery wai na weight loss, yanzu ma takicin abincin da aka kaimata sai kuka take, Ya Imran kamata magana please" wani kalan kallo yamata Hajiya tace "Imrana jeka mata magana haka yara yanzu suke su kawai su gansu sun dawo kaman tsinke Allah day ya kyauta jeka mata magana" wayanshi yaciro batare daya dagokanshi ba yace "kubarta taji yunwa zataci abinci da kanta" baki Hajiya tabude zatai magana yamike tsaye yace "I have to go Hajiya".
EPISODE 3️⃣2️⃣

Jama'a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Fita yayi daga dakin yawuce gym dinshi dake compound din dayake all kayanshi na workout na wajen saisa baimaje sama dan chanza suit na jikinshi ba.

Kallon Binta datai zamanta anan kusada Hajiya tayi tace "tashi kije ki kiramini yarinyar nan munaji muna gani barinta zamuyi ta kashe kanta" tashi Anty Binta tayi ahankali tawuce sama tun kafin takai wajen dakinta taga kulan abincin agaban kofanta tsugunnawa Anty Binta tayi tabude kulan ganin kotaba abincin batayi ba yasa ta murza kofan zata bude taji kofan arufe ita abinma dariya yabata tace "ohhh sabida kada asakici abinci shine kika rufe kofan ko, to Hajiya na kiranki" tashi Lujain tayi ahankali tana rike cikinta tawuce bayi dan batamaso tanajin maganan Anty Binta, maida kofan bayin tayi tarufe ta tsugunna awajen ita kanta mamaki take mahaukacin yunwa takeji bana wasaba tunda uwarta ta haifeta bata tabajin yunwa irin wanda takeji yau din nan ba, amman ita wlh saita daina cin abinci sabida ta rame Mandawari yakara

sonta sosai.

Anty tadade tsaye awajen ganin taki bude kofan yasa tajuya takoma kasa Hajiya tace “ina take”? Ganin yanda Hajiya ta damu yasa tace “Hajiya karki damu zataci abincin yanzun nan” cikeda damuwa Hajiya tace “dan Allah Binta koma wajenta ki tabbata taci, hankalina bazai taba kwanciya ba ace yarinya na wajena takicin abinci awani dalili ita ba azumi ba sai bama kai yunwa, yooo ita kibar har guda nawa ke gareta bandama shirme irin na yarintar Lujain, kiba kyau ne azamanin mu idan kinada kiba ba kowani kalan mutun nema zaizo neman aurenki ba sai masu kudi sabida ansan Kinacin abinci mai kyau gidanku babu yunwa ke Yar gata ce, azamaninmu da zaran an ganki mara kiba ramammiya cewa ake gidanku da yunwa baku samun abinci kuci, ni wannan zamanin nema naga gayu ake da siranta kiga yarinya kaman zaka hure da iskan bakinka tafadi wai shine gayu, to wlh bada niba, ni baran miki karyaba Binta ranan da mahaifin Lujain yakawota nan gidan da daddare dana fara daura idanuna akanta abinda nafara cewa shine Masha Allahu yarinya bulbul da ita son kowa kin wanda yarasa akan mene takeson bata kanta, ita batasan rama bazai mata kyau ba, sotake iyayenta suganta ace bamu bata abinci yarsu dukta tsotse jesama idan bataci abinci ba kizo kifadamin dan saina saba mata daga ita har Imran da akacemai taki cin abinci yakama hanya yay gaba abinshi” ganin yanda Hajiya tabata rai yasa Anty Binta tace “a’a Hajiya ai baimakai hakaba zataci ma bari naje” Hajiya tace “kada mata shayi ki tafin mata dashi” kitchen Anty Binta tawuce tahada mata tea a babban flask tadauko a tray da cup tawuce sama gaban dakinta taje ajiye tray tayi akasa tai knocking tareda murza kofan amman har lokacin a kulle at this point Anty Binta jitayi itama ta damu sosai, bubbuga kofan tayi hakan yasa Maman Aneesarh dake daki tafito tace “Ya Binta lafiya” dan murmushi Anty Binta tayi da idanu tamata alamu data koma daki kar Hajiya taji hakan yasa takoma daki itakuma Anty Binta tawuce dakinta dan dauko waya dauka tayi tafito Hajiya dake kasa tace “taci kuwa”? Dasauri tace “eh Hajiya taci” gaban dakin Lujain taje takira number Ya Imran dan shine spare keys ke hannunshi amman har wayan ya katse bai daga ba kusan 3 miss calls tamai bai dagaba sake fitowa Maman Aneesarh tayi jin yanda Anty Binta ke knocking kofarta tazo har wajen tace “Anty Binta wai menene”? Abincin dake gaban dakin tanuna mata tace “Lujain refuse to eat she wants to loose weight kuma yunwa takeji kaman ba gobe” kallon abincin Maman Aneesarh tayi tace “harwani kiban dazata rage takedashi tanadai so tama kanta wani illan kin fadama Ya Imran” cikeda damuwa Anty Binta tace “kema kin sanshi ko kulamu baiyiba danake gayamusu” Kausar da tun dazu tadawo daga school tana bacci bude kofa tayi tafito daga bakin kofa ta tsaya tace “ni wlh dukkan hanani bacci, ku barta mana Anty Binta maybe cikin nan nata yakoma flat kaman nawa” tai maganan tana dariya dakuwa daga Anty Binta har Maman Aneesarh suka mata daidainan Abee yashigo saman kallo yabisu dashi daki Kausar tawuce dasauri Dan babu hula akanta tace “welcome Abee” wani kallo yama Maman Aneesarh da Anty Binta strictly yace “I don’t wanna see any one of you anan” sadaf sadaf kowa yawuce Abee yace “it’s time for magrib” duk dakunan su suka shiga, yace “Fateema” dasauri Anty Binta tafito tadawo har gabanshi anatse tace “na’am Yaya” strictly yace “call your husband kiwuce kitafi gidanki” dan murmushi tayi tace “to Ya Imran” wucewa yayi yashige dakinshi batare daya kalli kofar dakin Lujain ba, wanka yayi yafito ya shirya cikin wasu fararen shadda riga da wando dayawani kalan haskashi yasaka, Wandon as usual iya idon sahu

rigan kuma jumper babu aiki ajiki hannun rigan yakamashi hakan yanuna murdaden hannunshi irin full nan dinnan turare ya feffesa jin an tada salla yasa yasaka slippers yafito dasauri yasauka kasa a compound yaga Hamza da Abdallah na alwala shigowansu kenan wucesu yayi yawuce yafita suma suka biyoshi abaya, sai bayan isha'i yafito daga masallacin yana tafiya ahankali Mandawari dake tsaye gaban gidanshi tunda Abee yafito daga masallaci yake kallonshi tunda yake in his life baitaba ganin mutumin da he feels so insecure about ba kaman Abee, tundaga kai har kafa yake binshi da kallo yakasa ganin makusa, gashin kanshi dana gemunshi baki sidik shida yake yaro shine ma yakeda yan furfura akai, tundaga nan kofar gidanshi yana iyajin hadadden kamshin da Abee keyi, hada idanu sukai da Abee daya kalleshi sau daya ya daukekai dasauri shima yadauke kai yana tsaki yace zaiga kaman na damu dashine, kaman daga sama yaji muryan Olusay yace "are you scared kar babe dinka tafara son mijinta danni wlh mutumin nan yafi mini kai kyau sau dubu, just look at a matured classic cool guy dan Allah ga naira, kai kaga shaddan jikinshi kakosan shaddan Oman ne wannan special edition din nan just guda 10 ne aduniya gabaki daya nidakai ba munje siya ba but bamu samuba thats what he is wearing, Mandawari a word of advice this guy no even send you so back off" dawani kalan sauri Mandawari yajuyo azuciye chakumeshi yayi hakan yasa Olusay yadaga hannuwanshi sama alamun yay surrender sannan yamai alamu da idanu kan ana kallonsu masu fitowa daga mosque sakinshi yayi yawuce cikin gidanshi yashige fuuuuu.

EPISODE33

Afalo yasami Musty yana zaune kusada Hajiya rikeda radio nata da screw yana gyara wata Yar waya data katse ciki, dago kanshi yayi jin kamshi dakuma sallaman Abee yace "shine zaka koramin mata to ai gani nan nazo daukanta ko angaya maka nima so nake tana zama agidan dakake zaune bayan kowa yasan you are bad energy" wani kalan mugun kallo Abee yamai batare dayace komi ba, Musty yace "Hajiya kinga irin kallon dayakemini kuwa kimai magana" juyowa Hajiya tayi takalli Abee hakan yasa ya gyara fuskanshi da sauri tareda dan sosa kai yayi yasami waje ya zauna Musty yagama gyara radio tareda kunnawa radio yafara magana yace "gashi Hajiya angama" cikeda jin dadi Hajiya tace "nagode Mustafa Allah ya shimaka albarka" dariya yayi yatashi bayin falo yashiga tareda wanko hannunshi yafito kusada Abee yazauna yana kallon fuskanshi yace "how far"? Kallonshi Abee yayi shima yace "what"? Dan kallon Hajiya yayi ganin hankalinta nakan radio ta yace "about that small boy"? Dan yatsine fuska Abee yayi yace "ohh I can't even recall his name" dan murmushi Musty yayi yafi kowa sanin halin Imran aduniyan nan this answer kadai na nufin baikarabi takan yaron ba yaron kuma bai karamai magana ba, abinci Kausar takawo musu bayan ta gaida Second Dad dan haka suke kiran Musty tawuce sama.

Wuraren 11 shida Anty Binta sukabar gidan Hajiya tuni ta shige dakinta, tashi Abee yayi yarufe kofa tareda kashe wutan falon yawuce sama abincin dake gaban dakin Lujain yabida kallo dahar lokacin ba'a tababa yawuce dakinshi wanka yasakeyi ya chanza kayanshi zuwa pajamas dark blue, coffee da aka ijiyemai adaki yabude flask din yazuba a mug yadauka ya jingina da

gado tareda kaiwa baki yay sipping, drawer shi yabude yaciro novel din dayake karantawa yacigaba da karantawa yanashan coffee.

Wuraren 1 tabude idanunta daga wahalallen baccin datayi dudda wutan dakin a kunne amma wani kalan jiri jiri take gani cikinta namata wani kalan ciwo dabazata iya misiltawa ba sabida yunwa, rabonta da abinci tun chips da Anty Binta tasa taci dan kadan dasafen nan sai ruwa kawai data dingasha, kokarin tashi tayi zaune amman jitayi takasa cikinta yamata kaman gyambo takasa mikewa wani kalan fashewa tayi da kuka ahaka, kofan dakin take kallo da idanunta da key kofan data ijiye gaban madubi tana tunani yanda zata tashi taje tadauki key tabude kofa tadauko abincin bakin kofan taci, da duka dan energy daya rage mata tayi yunkurin tashi wani kalan ciwo da cikinta yamata batasan lokacin data saki wani karaba tafado kasa akife tafashe da kuka sosai…..

Gently Abee yamaida novel din hannun nashi yarufe yay dan jim yana saurarон yanda take kuka wanda kaman akunnenshi takeyi, ijiye novel din yayi akan side drawer ahankali ya yaye bargon daya rufe kafanshi dashi yasauko da kafafun kasa yasaka bedroom slippers sannan yamike tsaye yana kulle boturan gaban riganshi da kyau ahankali yayi wajen kofa, bude kofanshi yayi yafita yana tafiya a natse yafito daga corridor ya tsaya gaban dakinta taredakai hannunshi ya murza handle na kofan jin har lokacin a kulle yasa yay dan jim saikuma yajuya yakoma dakinshi wani drawer yaja da keys daban daban keciki yadauki wani key yatashi yafito gaban dakin yazo yasaka key aciki ya murza sannan yabude kofan ya tsaya chak inda yake batare daya shiga cikin dakin ba, daga ita sai wani dan pink towel data daura kanta babu dan kwali tana kwance akasa ta kife cikinta da hannunta kekai tana kuka sosai dabaima fita da kyau tsabagen yanda ta galabaita idanunta akulle, sai hawayen dake fitowa daga cikinsu kana ganinta kaga wanda yunwa ya mugun galabaitar, juyawa yayi yakoma dakinshi karamin fridge dake cikin dakinshi yabude wani goran almond milk yadauko yamaida fridge din yarufe yafito dan tsayawa yayi agaban dakinta kaman wanda ke tunanin shiga ciki saikuma yashiga ciki ahankali tareda maida kofan dakin yarufe yakarasa zuwa gabanta, gently ya tsugunna tareda ijiye goran Almond milk din agefe, hannunshi yakai ahankali zai daura akan shoulder dinta saikuma ya tsaya tareda maida hannunshi yarufe ahankali yana kallon fuskanta yace “Ke” ahankali take bude idanunta kafin tagama budesu tass tadaurasu kan Abee, jiri take gani sosai amman dudda haka tagane fuskanshi, kwayan idanunta kadai yakalla da yanda sukeyi yagane jiri take gani, with a very calm and light tone yace “sit up” girgizama mai kai tayi dawani kalan sigan shagwaba tana turo pink lips nata, cikin wata kalan murya yar karama tace “carry me” dan kallonta Abee yayi dasauri kaman wanda baisan abinda taceba, ahankali take kuka tana kara kama cikinta dake yakushinta sosai tana kallonshi da idanunta dasuka kankance sosai suke juyawa, gently yazaro hannunshi yamika mata hannun guda daya batare daya tabata ba alamun tarikeshi ta tashi zaune, hannunshi takalla that is so clean ahankali kaman wata yar karaman yarinya tadaga dayan free hannunta dabata kama cikinta dashi ba, gently takai hannun saitin hannunshi dayake bata idanunta na ganin jiri takai hannun awani kalan hankali tasaka hannunta cikin hannunshi hakan yasa soft tafin hannunta yasauka akan tafin hannunshi

har cikin brain dinshi Abee yaji wani iri hakan yasa ya lumshe idanunshi kafin yabudesu ahankali yadaura kan cute chubby hand nata dake cikin nashi farcenta farare fat dogaye kaman tana wankesu da farin fenti, ahankali yadan kama hannun da kyau sannan yajawota tashi zaune tayi tawani kalan fashe da matsanancin kuka tayi tace “wayyoo cikina ciwo, Uncle zan mutu” wani kalan mugun kallo yamata baice komiba hannunshi dayan that’s free yamika yabude goran almond milk din sannan yadauka yajuyo tareda mikamata yace “karba kis……” wani kalan kawo fuskanta tayi da sauri takama hannunshi hade da goran takai bakinta tanasha dawani kalan sauri kaman irin yaran dasuka dade basuci abinci ba sunajin extreme yunwa, ahankali yabi hannunshi data rike gam da kallo tanashan milk din zuwa fuskanta gently yadaura idanunshi kan goshinta da gashin kanta suka kwanta lub lub wasu kuma sunyi coiling ga kitson da akamata kanana dasukai bala’in kyau bakin jelan gashin sun soma warwarewa da kansu sosai sabida santsi, idanunta duka biyun a lumshe sai dogayen gashin idanunta dasuka jike sharkar da ruwan hawaye, dauke idanunshi yayi daga kallonta saida ta shanye milk din tass sannan ahankali tasaki hannunshi tana komawa baya ta jinginar da bayanta da gado tana kama cikinta dataji yawani kalan daure mata fiyedana da tana lashe lips dinta dan almond milk din yamata dadi bata tabashan irin madaran ba, hannunshi Abee yakalla sannan ya ijiye goran akasa yakalleta kana ganin yanda take kasan ciwon yakaru ne yace “gobe ma you should starve yourself” hannayenta duka biyun takai kan fuskanta tafashe da kuka sosai dayasa Abee kawai ya tsaya yana kallonta yarinyar nan badai shagwaban banza ba, yunkurawa yayi zai mike tsaye dawani kalan sauri tazo gabanshi kaman zata shige cikin jikinshi dan komawa baya yayi dasauri kaman wani matsoraci yace “Ke what”? Cikin wani kalan kuka tone tace “har yanzu yunwaaaaa” dan hararanta yayi yatashi yajuya yafita daga dakin yamaida kofa yarufe tsugunnawa yayi abakin kofan ya kwashe kulan abincin da flask yawuce yasauka kasa yana tafiya ahankali, bude kulolin dinning yayi babu wani abinci daya rage hakan yasa gently yajuya yakalli kofan kitchen dinsu ahankali yabude kitchen din, rabon daya shiga kitchen dinan harya manta ko ranan a microwave na dinning yadumama abincin yakai mata, dan tsaki kadan yayi yashiga kitchen din ruwa yasa a kettle sannan yay shiru yana tunanin meya iya dafawa mezai kaimata? Idanunshi ne suka sauka akan egg, guda two yadauka yafasa saikuma kaman wanda yay tunanin wani abu yakara two again yafasa yasa pan a wuta da oil juye kwan yayi dayadan soyu yajuya sannan yakwashe a plate yakashe gas din yataho yahada mata tea mai kauri yasa a tray yadau bread yafito yawuce sama yana tafiya ahankali, bude kofan dakinta yayi ahankali tana kwance inda yabarta ganin yashigo da tray da sauri tamike tana zaro idanunta dasuka kankance tana kallon tray daya shigo dashi, karasowa gabanta yayi ya ijiye tray akasa dawani kalan sauri tadauki tea zatakai baki dasauri yace “Ke is hot” fashewa tayi da kuka sosai da abin yaso yama bashi dariya dan girgizakai kawai yayi danbaimasan mezaice ba yace “give it to me” karban mug din yayi yajuya tea tareda daukan bottle water mai sanyi dayasa akan tray yakara ruwa kadan aciki sanan yasake juyawa yadauka yabata dasauri takarba takai bakinta tafarasha, bread yabude yaciro one slice yabata sauke tea tayi daga bakinta da sauri ta ijiye akasa takarbi bread din, da spoon yadebo fried egg din yadaura mata akan bread din dasauri tai folding nasu takai bakinta ta gutsura gadai kwan da zafi amman ko gishiri babu a kwan bare Maggi, dan dago idanunta ahankali tayi takalleshi hada idanu sukayi dasauri ta maida kanta kasa tacigaba dacin bread din da kwan ahaka sannan tadau tea tasha, bread yakara daukowa yabata zai samata kwan ta girgixamai kai alamun a’a bari yayi ta karbi bread din taci, kusan 9 slice of

bread ta cin ta shanye tea tass sai alokacin taji ciwon cikin yadaina sosai, half fried egg dake plate din takalla saikuma tadan kalleshi hada idanu sukayi karaf kai tsaye yace “what” dan zaro idanu tayi tareda dan turo baki kadan kaman mai tsoron fadin abinda zata fadi murya chan kasan makoshi tace “you can’t…..cook Uncle” takarashe maganan wani short smile na kubuce mata abaki dayasa dimples dinta suka wani kalan lotsa duka biyun dawani kalan sauri Abee yadauke kanshi yashiga hade komi a tray sanan yamike tsaye batare daya kalleta ba yace “is that your thank you”? Wani kalan sunnar da kanta kasa tayi akunyace tace “thank you” dan dago kanta tayi jin bataji any motsi ba hada ido sukayi wani mugun kallo yamata dayasa ta sauke kanta kasa dasauri yajuya yafice daga dakin, sauka yayi yana maimaita abinda tacemai wai you can’t cook uncle, children of now adays ba basu da at all, kitchen yashiga ya ijiye tray din harya juya saikuma yajuyo hannunshi yakai ahankali ya gutsuri fried egg din kadan yakai bakinshi dawani kalan sauri ya tofar sai yanzu yatuna baisa komi a kwanba kawai ya fasa ne ya soya, wani kalan kunya yaji girgiza kai kawai yayi yawuce yafita daga kitchen din yahayo sama kallon kofar dakin nata yayi yawuce yashiga dakinshi bayi yashiga dan dauro alwala dan yanzu lokacin sallan daren shine.

https://chat.whatsapp.com/DinmgBAo43r4mDZSIUvrBb
Exquisite world collections

Muna sai da jakakkuna da takalma masu kyau wanda idan kuka siya ba lallai ku sake ganinsu wani wuri ba . I assured you. Ku siya ku godemin daga baya domin ingancin kayana. Ina turawa ko ina kike ni kuma Ina Abuja.

Wannan shine instagram handle dina.

I'm on Instagram as shukhria. Install the app to follow my photos and videos.
https://www.instagram.com/invites/contact/?i=ithkqozo1zuq&utm_content=oeu4f73

08108517010 wannan shine number wayana kuma dashi zaku sameni a whatsapp.

## EPISODE 3️⃣4️⃣

Wuraren 6 tabude idanunta ahankali sosai tayi mamakin yanda babu wanda yatasheta yau tashi zaune tayi ahankali tana taba cikinta dataji baya mata ciwo kuma tamike tsaye ahankali tawuce bathroom dan dauro alwala ganin small blood yasa tai brush tareda wanka tafito daure dawani towel daban zama tayi abakin gado tai shiru tana tunani tunawa datayi da wayan Mandawari yasa tasauka kasa dagudu tana leka karkashin gadon jawo wayan tayi tana dannawa ganin 6 miss calls dinshi dakuma 2 messages from him dasauri tabude messages din.

“Ke kinsan waye ni? Dan kinma samu ina kiranki shine baraki dagamin wayaba dan kina tareda wannan Baban mijin naki don’t ever call me again”
Wani kalan faduwa gabanta yayi gently tashiga second messege din.

“Wlh idan kika bari yamiki wani abu kokuma kika yaudareni Lujain saina wulakanta miki rayuwa! You belong to me Muhammad me only!”
Wani kalan faduwa gabanta yayi duk zuciyanta yamata badadi dialing number shi tashigayi daidai lokacin taji ana shirin bude kofanta dawani kalan sauri ta tura wayan karkashin cinyanta ta gyara zama tana kallon kofan daidai lokacin Kausar tashigo takalleta tace “Hajiya tace ki sauko muyi breakfast ki shirya daganan zamuje hadda” juyawa Kausar tayi zata fice dasauri Lujain tace “Kausar” juyowa Kausar tayi takalleta batare datace komiba, ahankali Lujain tace “please kibani pad bandashi da maganin ciwon ciki anjima kadan cikina zai fara ciwo” dan hararanta Kausar tayi saikuma tace “ni banda maganin ciwon ciki dan banayi” tana maganan tawuce tafita bata wani jimaba tadawo dakin dauke da pad guda biyu masu kyau dan ita kanta Lujain bata taba ganin irinsu ba bata tayi hannu tasa takarba tana murmushi tace “thank you” juyawa Kausar tayi zata fice tace “kuma kiyi sauri” tana fita tamike tsaye tareda daukan wayan taduba gani tayi yama dauki call din but ya katse sake kiranshi tayi tawuce tana shiga bayi tareda maida kofan tarufe, saida wayan yayi kaman zai katse yadauka kafin tamace wani abu yace “who do you think you are Lujain sabida kin samu mutum kaman ni na kulaki bakisan I am doing you a favor bane? Tell me what is good about you? Kene yarinya a sex tape that went viral online, kene gaki nan kaman zaki fashe, yarinya babu shape babu kyau, anhadaki da tsoho yanzu still na tsaya akanki nace zan aureki amman harkin kai matsayin ni Mandawari the biggest footballer in Nigeria na kiranki baki dagamini ba, where were you danake kiranki”? Wasu kalan hawaye ne sukazo mata sabida yanda yake mata ihu yana masifa sosai kaman zai daketa daga wayan, jin yanda tai shiru yasa abin yakara tunzurashi yace “Lujain nike miki magana ni Mandawari kikama shiru kika share? Fine dagayau bani bak……” cikin wani kalan sauri bakinta har rawa yake tace “da……..dan Allah kayakuri” wani kalan lumshe idanu yayi yanajin yanda harshenta ke rawa alamun kuka take yarasa what’s so special about this local girl da Allah yajarabeshi da sonta, idan yatuna yakirata last night bata daukaba saiyaji wani mugun kishi ya turnikeshi, dan calming muryanshi yayi kadan dan baiso yamata ihu jin tana kuka yace “kina ina jiya da daddare bayan nagayamiki zan kiraki wajen mijinki kikaje? Meya miki did he hold your hand? Touch you did he kiss you koko yanzu finally kunyi sex din da akayi accusing naku dashi ne” dasauri tashiga girgizamai kai kaman yana gabanta tace “a’a” cikin ihu k aman yasamu yarshi yace “to me yamiki! Tell me” Yanda ya daka mata tsawa saida ta janye wayan daga kunnenta dan kaman zai fasa mata kunne, maida wayan kunnenta tayi ahankali tace “wlh babu abinda yamini jiya banida lafiya ne” ahankali yace “are you sure”? Gyadamai kai tayi tace “eh” dan sassauta muryanshi yayi yace “meya sami baby na what’s wrong with you”? Dan murmushi tayi jin yanda yakirata da baby ahankali tace “cikina ke ciwo I was so hungry” dan shiru yayi saikuma chan yace “waike akwai abinda kika sani sama da abinci kuwa aduniyan nan? Sabida nahana ki kada kici abinci shine zaki bingile da ciwon ciki, hope bakici abincin ba haka kika kwana”? Gyadamai kai tayi ahankali tace “eh” dan murmushi yayi yace “good baby,

that's why I love you" wani kalan murmushi tayi mai dan sauti yace "tom yanzu kije ki nika fruits kisha idan akwai salad zaki iya ci, daga yanzu salad su yayan ganye da yayan bishiya ne abincin ki kinji" gyadamai kai tayi tace "tom" ahankali yace "I want to see you today, 4 ne za'a fara event dina a city conference center zan turamiki address din, makesure you look peng okay" gyadamai kai tayi saikuma kaman mai tsoron magana tace "mutane zasu ganni suganene nice ta video" murmushi yamata yace "babu wanda zai ganki you are coming to see me akwai wanda zaizo yadaukeki yakawoki har private room danake ciki okay" gyadamai kai tayi tace "to" murmushi yayi yace "now go and have breakfast Mandawari's baby, I love you Lujain" wani kalan sanyi taji azuciyanta tadade tana mafarkin rannan da Mandawari zaice mata he loves jitayi kaman zata zauce, wani kalan murmushi tayi zatai magana taji ya katse wayan fitowa tayi daga bayin tawuce tadauki wani handbag cikin wayanda Anty Binta tasaya mata tasa wayan aciki sannan ta shirya tsaf cikin wani Riga da skirt na kanti milk skirt din yawani kalan fito da katon hips nata, inba kasan Lujain ba kaganta zaka dauka all this yaran nan dasuka kai 24/25 ne sabida yanda takeda girman jiki da gabobi saidai idan tayi magana kokuma ka kalli kwayan idanunta dan akwaita da zakin murya ga muryan Yar siriruwa, wani milk hijab sabo fil dake wardobe din tadauko tasaka takoma gaban madubi tana kallon fuskanta wayan hijabin yadan mata yawa kadan hakan yasa yadan zame baya kana ganin gaban gishinta da farko farkon kitsonta da hakan yasa tai bala'in kyau, babu abinda tashafa a fuskanta amman tai wani kalan kyau tai haske sai naman idanunta dasuka danyi ja sabida kukan datayi jiya da daddare dakuma yanzun nan, turarukanta ta dauka ta feffesa tana murmushi bakaramin dadi sukedashi ba, wani black flat takalmi ta zura kafafunta aciki dan yatsun kafanta sukai wani kalan kyau aciki sosai sannan tadauki jakan tafito tana kallon dakin dabata gyaraba dudda bawani datti sauka tayi kasa Hajiya ne kawai a falo sai Kausar dasu Aneesarh da yaran Ibro da Baban su yakawosu yanzun nan yafice, ganin Lujain yasa Hajiya tace "zonan Lujain karna karajin kince barakici abincin agidan nan ba kina jina, ke bakisan kiba rahama bace jibeki kaman asace agudu kina nema ki lalata kanki dawani rama, Allah shiya hallito sirara shikuma ya hallito masu kiba to akanme kikeso kice ke ga wanda kikeso? Kada nakarajin kinyi irin abinda kikayi jiya kinji" gyadama Hajiya kai tayi ahankali kanta akasa tace "baran karaba Hajiya kiyakuri" wani kalan murmushi Hajiya tayi tace "nayi yanzu jeki debo abincin ki kizo nan kici Hamza zai kaiku hadda mijin naki yafita ni banmasan inda yaje yau asabar da sassafen nan ba Imran dabai cika fita weekends ana kiranshi awaya yafice, tafi hado breakfast naki kizo" tashi tayi ahankali tawuce kitchen babu kowa a kitchen din, blending fruits tayi kaman jiya ta shanye a kitchen din tana bata fuska sannan tahada tea batasa madara ba ta debi kwai tafito kin zuwa falon tayi tazauna a dinning ta cinye tass sannan ta tashi takai komi kitchen saida ta wanke sannan tafito Hajiya tace "tashi Kausar kutafi Hamza na tsakar gida" tashi Kausar da itama ke sanye da hijabi tayi tadauki jakanta tai gaba Lujain tabita abaya tace "muntafi Hajiya" murmushi Hajiya tayi tace "adawo lpy" bude kofan tayi ahankali tafita daidai lokacin wani jeep na benz na shigowa cikin gidan motan tabi da kallo daga ita har Kausar suna sauka daga dakali, parking motan yayi bude gaba akayi aka fito Abee ne yana sanye da jean da wani t-shirt fari mai v neck daya kamashi sosai chest dinshi yafito broadly, kafanshi sanye da crocs black, kofan baya yabude ahankali Gwaggo tasauko daga motan tana wani kalan washe baki tana gyara dankwalin kanta dake neman zamiyewa hannunta rike dawata Yar purse da akayita da yadin atampan jikinta takalli Lujain dake kallonta saikuma ta taba Abee tace "jibin mini sha sha shan yarinyar chan taganni

kuma ta tsaya sangangan kaman gunki tana kallona uwa bata sanni ba" wani kalan murmushi Lujain tayi jin muryan Gwaggo batasan lokacin data wani kalan kwasa da gudu ba tana zuwa wajen wani kalan mugun tsalle tayi ta rungume Gwaggo tana wani kalan dariya da bala'in murna. "Oyoyoooo Gwaggooo na".
EPISODE 35

Exquisite world collections

Muna sai da jakakkuna da takalma masu kyau wanda idan kuka siya ba lallai ku sake ganinsu wani wuri ba . I assured you. Ku siya ku godemin daga baya domin ingancin kayana. Ina turawa ko ina kike ni kuma Ina Abuja.

Wannan shine instagram handle dina.

I'm on Instagram as shukhria. Install the app to follow my photos and videos.
https://www.instagram.com/invites/contact/?i=ithkqozo1zuq&utm_content=oeu4f73

wa.me/+2348108517010 wannan shine number wayana kuma dashi zaku sameni a whatsapp.

Ciro wata Yar katuwan jakan Gwaggo Abee yayi daga motan tareda maida kofan yarufe yadan saci kallon fuskan Lujain, today is the first time daya fara ganin all set na cute white short teeth nata duka sabida how happy she is ga dimples dinta dake wani kalan lotsawa kaman ana operating nasu da remote, ta kankame Gwaggo gamgam tareda lumshe idanu kaman wani zai kwace mata ita, dan dauke kai yayi tareda gyaran murya hakan yasa Gwaggo dake murna sosai ta tureta tace "cikani Lulu mun tarema mijinki hanya" sakinta tayi ahankali tana komawa gefenta batare data kalli Abee ba daidai lokacin Hamza da Kausar sun karaso wajen cikeda girmamawa Hamza yace "ina kwana Gwaggo" washe baki Gwaggo tayi tace "kaga yaro mai tarbiya ba irin nawa jikokin ba basu rusunawa idan zasu gaidani" ahankali itama Kausar tadan rusuna tace "ina kwana Gwaggo" wani kalan washe baki Gwaggo tayi tace "ana ganin kwayar idanunki anga na Babanki yaya sunanki yammata" ahankali Kausar tace "Kausar sunana" Gwaggo tace "Masha Allah Kausar ina zaku haka keda Lulu kukaci hijabia kaman matan limamai" murmushi tadanyi ganin Gwaggo is so lively tace "Hadda zamu" dasauri Lujain amugun shagwabe tana kara kama hannun Gwaggo tace "Gwaggo ni barani ba" ba Hamza da Kausar kadai ba har Abee saida yadan kalleta jin yanda tai magana yadauke kai dasauri, irin Gwaggonta tazo din nan mai taremata, itama Kausar dasauri tadan kalli Abee dasauri taje wajenshi hannunshi takama kaman zatai kuka tace "Abee dan Allah muhuta gobe saimuje eh Abee tunda Gwaggo tazo" dasauri Gwaggo tace "da sunana zakuyi amfani kuyi sabon Allah badaniba" saikuma tadan kalli Abee tace "adan barsu suhuta yau ko Imrana" adan kunyace yace "to Gwaggo" yana maganan yawuce rikeda jakan Gwaggo a hannunshi Kausar da Lujain sukahau tsallen dadi Hamza yace "Allah shiryeku" Gwaggo ta tabe baki tace "tayani fadi dan nan yara kiri kiri suki karatu wanda yafi na yahudun dasuke zuwa amfani, nidai ku kaini cikin gida" tai maganan tana mikama Kausar Yar purse dinta tace "rikamin naira dubu uku da dari

biyu da hamsin ne aciki dake na yarda nasan baraki cimin ba amman kinga wannan" tanuna Lujain tace "kuran kudi ce" dariya daga Hamza har Kausar sukayi Lujain ta daure fuska sukai cikin gida, daga Kausar har Hamza wani kalan dadin ganin Gwaggo sukaji, wani kalan uban sallama Gwaggo ta rangada afalo Hajiya dake zaune tareda Abee ta amsa tana murmushi tace "barka da zuwa Gwaggo" cikeda farinciki Gwaggo tace "nasameku lafiya ya Lula incedai bata tadaku da yunwan dare" wani kalan daure fuska Lujain tayi tasaki Gwaggo tawuce tasami waje akasa tazauna Gwahho ta kalleta tareda tabe baki tace "too danna fadi gaskiya shine zakiyi fushi dani aisai kiyi tayi" Gwaggo tai maganan tana zama akan 3 sitter daga Kausar da Hamza suka zazzauna kusada ita suna kallonta kaman sunga tV, Gwaggo tace "Hajiya kinga wannan jikan tawa fitinanniyan yarinya ce ga taurin kai da kafiya ina chan gidan dana amman ina tunanin halin dazata sakamini ku ciki" dan murmushi Hajiya tayi takalli Lujain dake kumbure kumbure tace "Lujain batada matsala bata taba daminmu ba gaskiya" dan dariya Gwaggo tayi tace "ai shine nan, bani jakata kagani Hamza" tashi yayi yadauko jakan yakawo gaban Gwaggo sauka tayi kasan carpet tashiga bude jakan dasauri Lujain dake fushi tazo wajen tace "mekika kawomini Gwaggo"? Hararanta Gwaggo tayi tace "yanzu kinga daman kulani" Gwaggo tai maganan tana ciro wani katon kwano data daka lafiyayyen yaji da bushashen nama da kayan kamshi tace "Hajiya ga yaji dakaina na dakashi kinga wayan nan gantalallun yara su Samira dazaran sunga zan fara aiki guduwa suke su labe hope ke baki kiwuya" tai maganan tana kallon Kausar dake kallonta dasauri Kausar ta girgiza mata kai tace "a'a banda kiwuya" baki Hajiya takama tace "Kausarrrr sannu da aiki" kwashewa da dariya Hamza yayi da Lujain harda kyalkyacewa Abee yadan saci kallonta yanda take kallon Kausar tana dariyan kasan tsokana ce, dan girgizakai kawai yayi yakai coffee shi baki yay sipping, Gwaggo cikeda lallashi tace "karki biyemusu ni ina ganinki nasan baki da kiwuya kin iya shan aduwa da goruba da magarya"? Dasauri Kausar ta gyada mata kai tace "eh" fito da ledojinsu Gwaggo tayi ga goruban duk an kankare jiki sunyi kyau tace "zoki debi naki kafin su wayan nan dake miki dariya" kaman Lujain zatai kuka tace "Gwaggo nifa" daga Abee har Hajiya dawowa yan kallo sukayi Gwaggo entertaining nasu kawai take agidan ana haka saiga Musty da Harun da Ibro da Anty Binta sun kawoma Lujain atampopinta da aka gama dinkawa haba dakin kachamewa yayi wawan goruba ake Musty da Harun harda Yar rige rigen dauka, sosai Musty ke lura da Abee yanda any magana da Lujain zatayi saiya kalleta kodan sabida bata taba magana da dariya irin na wanda takeyi yau ba ganin Gwaggo ta oho shi kanshi Musty kallonta kawai yake she's so adorable and a very sweet and beautiful girl, he just wish abokinshi zaizo yarinyar nan and open up his heart da yanzun ne xaisan soyayya.

Dan yatsine fuskanta tayi jin maranta ya murda, tashi tayi ahankali Ibro yace "ina zaki ana hira mai dadi dake babu wanda yataba jin muryanki agidan nan haka" Musty yace "sai yau da Gwaggon ta kenan ba" Anty Binta tace "to kishi kuke yarinya da Gwaggonta" Gwaggo tace "ai tunda aka kawota nan gidan ku nahuta jibi yanda tai haske takara kyau ashe haka kikayi sa'an zuri'a dan Allah jibi yanda kansu yake ahade kowa nada kirki, babu yanda banyi da ubanta yakawoni nan nadubata ba yaki kunsan idan yafita sallan asuba baya kara dawowa sainai bacci sabida karnace yakaini, shinefa na kira Hadi dole nasashi yasaka mini number Imrana awaya ta nakira Samira tamini saving nasa kiramini shi, kira daya nama dan albarkan nan jiya da

daddaren nan yace shikenan zaizo da safen nan ya daukoni, saiko gashi yazo aike Lulu kinyi miji" wani kalan kunya taji juyawa tayi tawuce stairs abinta tana tafiya ahankali Gwaggo kuma takara gyara zama tabude sabon chapter babu wanda baya dariya adakin nan sai Abee da kawai jinsu yake babu Uhm babu um um, Gwaggo sai zuba take ana dariya a falon harda hawaye.

Tashi ahankali Abee yayi Gwaggo tace "ina zaka Imrana" anatse yace "abu zan dauko a sama" dasauri tace "ayyooo tafi to abinka" stairs yayi Gwaggo tabishi da kallo saikuma takalli su Musty tareda rige murya kaman wacce zatai gulma tace "surukin nawa baida hayaniya kaman ku" haba mezasuyi banda dariya shi kanshi Abee dake stairs yana jinsu dan murmushi yayi yawuce abinshi Musty yace "ai Imrana Gwaggo tun muna yara haka yakeda miskilanci akwai shariya da rashin son magana" Gwaggo dake kallonsu tace "uhmmmm ba shakka" yanda tai maganan yasa suka kara kwashewa da dariya.

Karasawa sama yayi yana tafiya ahankali harya wuce kofan dakin Lujain saikuma yadawo baya ahankali ya tsaya chak gaban kofan yana sauraron sautin kukanta dayaji yakai kusan 1min tsaye awajen saikuma yasaka hannunshi ahankali yatura kofan batare daya shiga cikin dakin ba, tana tsugunne agaban bathroom na dakin da ledan pad da Kausar tabata a hannunta, dan dago kanta tayi tadan kalleshi shigowa cikin dakin yayi yana tafiya one one yakarasa inda take a tsaya akanta ahankali yace "what's wrong with you"? Gently ta janye hannunta taboye pad din hannunta abayanta sannan takife kanta akan kafafunta murya chan kasa tace "cikina ke ciwo sosai" yana kallonta ahankali yace "stand up" girgixamai kai tayi batare data dago kanta ba, kana ganin yanda take kasan cikin bakaramin ciwo yake mata ba, juyawa yayi yafita daga dakin yanajin yanda kukanta ke karuwa yafito da wayanshi Anty Binta na zaune a falo suna dariyan Gwaggo wayanta yashiga ruri ganin Ya Imran ke kiranta yasa dasauri ta mike tsaye tareda daga wayan takai kunnen tace "Hello Yaya" anatse yace "go and check on that girl" yana maganan yana katse wayan, dasauri Anty Binta takarasa sama dakin Lujain tawuce datagani abude ganinta a tsugunne har yanzu takasa tashi tana kuka sosai yasa tai wajenta dasauri tace "Lujain menene what's wrong" ganin pad a hannunta yasa tace "Subhanallahi maranki ciwo yakene"? Gyadamata kai tayi Anty Binta tace "tashi to ki kwanta kafin asayo miki magani" cikin wani kalan murya tace "kafana yarike ki kiramini Gwaggo na" dasauri Anty Binta tace "haka kafanki ke rikewa" Gyadamata kai tayi tana kuka, tashi Anty Binta tayi tafita dakin Abee tayi tai knocking tareda sallama, daga taciki yace "shigo" bude kofan tayi tashiga ahankali yana zaune gaban desktop dinshi, kusadashi tayi tace "Yaya she's having MP cramps ne sosai yana rike mata kafa Ya Imran zaka kaita asibiti ne ko zaka kira Dr yamata prescribing magani asayo?" Batare daya kalleta ba yace "you can go" juyawa tayi tafita daga dakin batare data kara cewa komiba.

EPISODE3️⃣6️⃣

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

Fita tayi daidai Gwaggo da Kausar data rike mata hannu na hayowa sama Gwaggo na salati tana sallallami tace “bani zaku maida kuturwa agidan nan ba, wannan bene haka haba” karasawa dakin Lujain din tayi atare dukansu ukun suka shiga dakin Gwaggo na ganin Lujain duke tace “ke kinfara ciwon cikin ne ohhh ni wannan ciwon ciki yaushe zaibar Yar nan, ina kukasa akwatinan nan nasaka miki maganin aciki, Binta da Kausar kutayani dagota ahankali kafanta yarike” da Anty Binta da Kausar ne suka dagota da kyar kwantar da ita sukai akan gado sannan Anty Binta takawo mata akwatinan Lujain din Gwaggo ta aika Kausar takawo ruwa, nan da nan Gwaggo tajika mata wasu magunguna saida sukai da gaske sannan tasha kadan Gwaggo tace “kunganta nan banga wanda yakaita laulayin ciwoba tun tana yar yarinyan ta amman tafi kowa tsanan magani” bacci ne ya kwasheta Gwaggo tamike takalli Kausar dake kallonta tace “zomuje ki kaini bayi” daga Kausar har Anty Binta dariya sukayi Kausar tanuna mata kofan bayi tace “ga bayi nan” ahankali Gwaggo takarasa tabude bayin tana kallon komi naciki saikuma tajuyo takalli Kausar tace “yoo ta ina na iya amfani da kalan wanga bayi kaman a film” kaman abinda Kausar da Anty Binta ke jira kenan dariya sukayi Kausar tashiga bayi ta gwadama Gwaggo komi sannan tafito suna duk suka fice yin salla.

Bayan anyi azahar Abee yashigo gidan sama yayi daidai Anty Binta nafitowa daga dakin Lujain dake bacci kaima Gwaggo abinci ledan magunguna yabata dasauri takarba taredayin murmushi tace “thank you Ya Imran” wucewa yayi abinshi itakuma tajuya takoma dakin Gwaggo tabama ledan tace “gashi Gwaggo mijinta yasayo mata magani” wani kalan murmushi Gwaggo tayi tasa hannu takarba tace “yayanku na kulan mini da jika da kyau Allah dai ya sakamai da alheri, idan ta tashi dakaina zan kiraki kizo kibata danni ba gane rubutun maganin asibiti nikeba” murmushi Anty Binta tayi tace “to shikenan” wucewa Anty Binta tayi tafita itakuma Gwaggo tabude kuka ta debi shinkafa da stew da soyayyun kaji dayawa tana murmushi tace “abinda ba’aci agidan ubanki kenan sai salla salla inbadai nina soyamiki” sosai taci tai kat tasha ruwa da lemu anan kasa bacci yay awon gaba da ita.

Vibration yatadata a bacci datakeji kaman a kunnenta bude idanunta tayi ahankali tana dube

dube saikuma chan ta hango waya akarkashin gado nakawo haske yana vibration hannu Gwaggo tasa tace “waya manta da wayanshi adakin nan gashi sai kira ake” tashi tayi tafice rikeda wayan dake vibrating bude kofa tayi daidai Abee da dawowanshi kenan daga sallan la’asar a masallaci yahayo saman ganin Gwaggo yasa ya sunnar da kai kasa ahankali yace “ina yini Gwaggo” murmushi Gwaggo tamai itadai bakaramin kima da mutuncin shi take ganiba tace “kaga Imrana bansan ko Binta ko Kausar bane sukabar wayansu ba bacci fa nake naji giririrriii natashi shine naga waya akarkashin gado anata kira itakuma tana bacci balle nabata takawo musu gashi katayani basu bari naje nai salla tunda wayan yatadani” ahankali Abee yakarbi wayan daidai number da akai saving da Mandawari na kira Gwaggo kuma tajuya takoma daki tareda maida kofa tarufe Abee yadade yana kallon wayan harta katse daidai nan kuma yaga hoton Mandawari ajikin screensaver, yakai kusan 2min yana tsaye awajen kallon wayan yake yaji zuciyanshi nawani kalan tafarfasa dayarasa dalilli kafin ahankali yafara tafiya yawuce dakinshi, Binta IPhone 14 take amfani dashi, kannenshi da yaranahi dukan su 13 pro max garesu har Kausar Wanan ne kawai 12 agidan nan, yana shiga dakinshi ijiye wayan yayi kan desk yawuce yafada bayi.

Wuraren 5 tafarka ita kadaine adakin amman tana iyajin muryan Gwaggo anan falon sama tana zuba sai waka takema jikokin gidan su Aneesarh, gently ta tashi zaune tanajin ciwon cikin nadawo mata sabo fresh, sauka tayi dagakan gadon ahankali tawuce bayi wanka tayi da ruwa mai zafi sosai tafito daure da towel shiryawa tayi tsaf tadauki wani simple gown mai spaghetti hand anytime take period she don’t use to feel comfortable at all takurama rayuwanta yake ba kadan ba dan batason saka pant naturally, kuma batason zama da kaya, feffesa turaruka tayi tana kallon kulolin abincin dake dakin amman bakinta baya mata dadi daga kanta tayi tabi dakin da kallo idanunta ne suka sauka kan agogo 15min after 5, wani kalan zaro idanu tayi tamike tsaye dasauri tai wajen gado taleka zata ciro wayan da dazu tacire daga jaka ta tura karkashin gado amman bata gani ba, tashi tayi dasauri taje ta dayan side din gadon tana leka karkashin gadon amman bata ganiba jin anbudo kofa yasa dasauri ta dago Gwaggo ne, zaro idanu Gwaggo tayi tace “ke ciwon cikin keneman sakaki shigewa karkashin gado, zokisha magani mijinki yasayo miki kici abinci” shigowa Anty Binta tayi  tace “sannu Lujain kinji Zokisha magani” girgixakai Lujain tayi tafashe da kuka tace “ni naji sauki basainasha magani ba” Gwaggo tace “hakafa take sainai da gaske yarinyar nan keshan magani, ballo maganin kigani Binta” ballo magungunan Anty Binta tayi guda hudu ne tana gani Lujain tawani kalan fashewa da kuka mikewa tsaye tayi dawani kalan gudu tabude kofan tafita daidai Abee dake waya yazo zai wuce wani kalan fadawa jikinshi tayi one two three Abee yay tangal tangal, baya Abee yayi kaman zai fadi saikuma yay sauri yay standing on his feet waya na kunnenshi still yabita da kallo yanda ta rirrikeshi ta kulle idanunta gam danta dauka fadi zatayi ana hello hello awayan da Abee yake yakasa cewa komi hakan yasa gently tadago kanta jin hello da akeyi hada idanu sukai da Abee dake mata wani mugun kallo dawani kalan sauri tafita daga jikinshi takoma baya, Anty Binta da Gwaggo dasuka fito dasauri Gwaggo tace “yauwa Imrana kaga magani take guduwan mawa haka hartanacin karo dakai gashi mugun ciwon ciki take” kallon Anty Binta dake rikeda maganin da ruwa a hannunta yayi babu alamun wasa a muryanshi yace “bata tasha” mikamata Anty

Binta tayi tace “gashi” karba tayi ahankali tana wani kalan shagwababben kuka daga Abee har Gwaggo da Anty Binta kallonta suke, Anty Binta sai murmushi take dan gown din datasaka yamata wani kalan kyau shape nata yafito sosai, ruwa tasaka abaki sanan tadau daya zata saka Abee yace “drink all” gyadamai kai tayi ahankali takara sautin kukan datake Gwagho tace “aisai kiyi nagode ma Allah da yanzu inada maganin ki” watsa maganin tayi abakinta tana yunkurin amai Abee yace “don’t you dare” hadiyewa tayi tana batarai tawuce tashige dakin dasauri Abee yawuce yasauka kasa abinshi, abinci taci badawani yawaba dan bakinta badadi gabanta sai faduwa yake tarasa ta yanda zata tambayi Gwaggo wayan haka taja bakinta tayi shiru tun cikin namata ciwo harya daina.
Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

EPISODE3️⃣7️⃣

Bayan salla isha’i ta tashi daga kan gado tanajin dariyan Gwaggo dan turobaki tayi tarasa ganekan wajenta Gwaggo tazo ko wajen yan gidan nan tana gama bata tea yanzun nan takara fita, wanka tawuce tashiga tadade abayin tafito shiryawa tayi tsaf bayan ta shafa mai ta feffesa body spray tasaka wani rigan bacci orange yana nan kaman t-shirt a iya knees dinta kanta babu dankwali saitayi kaman wata Cinderella, sake tsugunnawa tayi taleka karkashin gadon tana kara duba wayan Mandawari but still bata ganiba, wuraren 10:30 Gwaggo tabude kofa tashigo dakin ganin yanda Lujain take daddaga filoli da bargo tana neme neme yasa Gwaggo tace “nashige su mehaka kika juyamin daki wai mekike nema haka kinbar mijinki shi kadai adakinshi ke kina nan tun dazu yatafi ya kwanta” turo baki tayi tazauna ganin bakin gadon tai tagumi ganin bataga wayan ba, karasowa dasauri Gwaggo tayi gabanta takama hannunta tareda mikarda ita tsaye tace “yo wai ke wace kalan yarinya ne Lulu iyye? Oya wuce kitafi dakin mijinki” turobaki tayi tace “ni anan nake kwana” baki Gwaggo tasaki saikuma tamata dakuwa kaman zata tsokale mata idanu da sauri ta kulle idanunta Gwaggo tace “aida kin barshi bude kiga yanda zan tsiyaye miki wayan nan idanuwan magen naki tunda bakida hankali, wuce kitafi dakin mijinki” akufule Lujain tace “ni bansan dakinshi ba Gwaggo kumani ki kyaleni” hararanta

Gwaggo tayi kawai ta finciki hannunta tayi waje da ita tana masifa tace “da girmana billahillazi barakisa nayi abun kunya ba nazo gidanku inaji ina gani kizonan ki kwana dani barakije ki kwana da mijinki ba” duk yanda Lujain ke turjewa kin sakinta Gwaggo tayi har gaban dakin Abee kai tsaye Gwaggo tabude dakin tareda wurgata ciki itama tana shigowa Abee dake zaune gaban study yadago kanshi yakallesu yanda Lujain ke makema Gwaggo kafada alamun barata zauna anan ba Gwaggo ta washe baki tana kallon Abee tace “Imrana zan lallasa matar nan naka akanme sabida taganni barata kwana dakin mijinta ba sai wajena, kibiyoni kiga abinda zan miki” Gwaggo tawuce tafita tareda rufomusu kofan tsayawa wajen tayi chak kanta akasa hawaye ya gangaro daga idanunta takai hannayenta tanajan riganta kasa she’s so uncomfortable, Abee cigaba da abinda yakeyi yayi batare daya kara bata second look ba, gajiya tayi da tsayuwa ganin kafafunta na neman rikewa ta tsugunna ahankali akasa saikuma tazauna awajen kaman marainiya tarasa abinda kemata dadi, wuraren 11 tafara gyangyadi awajen.

12 daidai Abee yagama aikin dayakeyi tass yakashe computer sannan yajuyo ahankali yadaura idanunshi akanta gabaki daya atakure take tana gyangyadi kanta na lilo awahale. “Kee!” Wani kalan mugun firgita tayi tabude idanunta dasauri tareda mikewa tsaye tana kallon Abee awani kalan tsorace, mikewa tsaye yayi ahankali tareda zuba hannayenshi acikin aljihun wandon dake jikinshi yafara tafiya yana tahowa inda take, batasan mesaba wani kalan faduwa gabanta yashigayi yawani kalan cika mata idanu yamata mugun kwarjini kasa jure kallon dayake mata tayi dawani kalan sauri tasauke kanta kasa, karasowa yayi gabanta ya tsaya chak hannunshi zube a aljihu yana wani kalan kallonta, tunda take bata tabaganin mutumin dayamata rumfa kaman yanda Abee yamata ba ganin yanda ya tsaya daf da ita ko Baba baya mata rumfa haka, hakanan jikawai tayi kafafunta sun kasa daukanta, dukewa tayi awajen dasauri tana wasa da yatsunta, kallonta yayi cikin kakkausar murya yace “stand up!” Babu musu ta mike tsaye kirjinta nawani kalan bugawa babu kakkautawa bata tabajin kalan faduwan gaba datakeji ayanzu ba wani kalan zati da kwarjini Abee yakedashi da ita kanta bazata iya bayani ba, ganin yanda takasa dago idanunta takalleshi yasa strictly yace “look into my eyes!” Dago idanunta tayi tadaura akan nashi kasa cikakkun 3secs tayi ganin kalan kallon dayake mata zata sauke idanubta kasa azafafe yace “don’t you dare!” kafeta yayi da idanu yana tura hannunshi cikin aljihu yaciro wayan Mandawari tareda nunamata wani kalan ijiyan zuciya tasauke saida yaji saukan numfashin akan fuskanshi gashi ya tsareta da idanu bayako kyaftawa daburcewa tayi daburcewan dabata tabayiba tunda tazo duniya kawai fashewa tayi da kuka, yatsanshi yakai kan lips nashi hakan yasa tawani kalan hadiye kukan tass, anatse yace “kuka nace kimini”? Girgixamai kai tayi tanawani kalan sauke ijiyan zuciya gwanin ban tausayi, ganin yanda take numfashi kaman zata shide yasa ya sassauta murya ahankali Yace “what did I say?” Adaburce tace “kace wayan waye wannan?” Tsareta da idanu yayi alamun yana jiran amsa, lips dinta har rawa suke kaman an jonamata electric shock tace “Maa…….Man…….d…..wari yab……b……bani” tafada dukta burkice, wani irin kallo dayamata yasa taji cikinta ya murda batasan lokacin datace “a school din nan yakawomini” wani irin kallo Abee yamata yace “ina jinki” kuka ne a muryanta sosai amman yahanata yi in that crying tone tace “ina aji security guy yazo yace Yayana nakirana I thought kaine naje naga shine, he asked me yanda akai auren mu, saiya bani wayan yace zai kirani and he’s inviting me to his welcoming party, da……daz….zu

ma yaaaaa…..kir……rani” Abee jiyayi kaman ta watsamai garwashin wuta azuciyanshi, nunata yayi da yatsa yace “listen here girl babu abinda zanyi dake, I don’t consider you my wife one bit, ko anjima aka kama yaron nan I will be sending you back to your father’s house batare dana bari kin kara koda kwana daya agidan nan ba, but listen here dagayau don’t ever bring wani abu that belongs to wani namiji into my house kinajina” gyadamai kai tayi dasauri tana tagwayen ijiyan zuciya idanunta na mugun kyalli sabida yanda suka cikada hawaye, cikin zazzafan murya Abee yace “nine nace you can live anyhow and talk to duk wanda kikaga dama and that same me yau na janye! Inhar kina gidan nan kina zama karkashina karki kara kula wani, idan kika kara koda kallon that small boy saina baki mamaki kinajina” gyadamaikai tayi dasauri tace “eh naji” cikin fushi sosai Abee yace “just sit and be praying akamo mutumin nan so that you will get out of my life forever nagaji dake! I am tired of you! Pray akamoshi sabida narabu dake only then you can do duk abinda kikaga dama and talk to duk wanda kikaga dama Imran doesn’t care! Understood” gyadamai kai tayi dasauri, hakan yasa yawuce fuuuuu yafada bathroom nashi, wanka yayi yafito sanye da kayan dayashiga dasu bayin yana fitowa yabude kofa yashiga dakin closet nashi yadan jima aciki sannan yafito dawasu pj dark blue ajikinshi yana wani kalan kamshi hannunshi rikeda wani babban bargo batare daya kalleta ba yace “jeki kwanta akan gado” dan dago kanta tayi takalleshi ganin yay kan dogon couch din wajen yana shirin kwanciya yasa ta tashi ahankali tai kan gadon har wani tsoron hawa gadon take, gadon fes fes bedsheet din fari kal amike kaman ba’a kwana akai, kaman wacce bata bata ganin gado ba tahaukai ta kwanta gadon nawani kalan kamshin turarenshi, bargo taja ta lullube sabida yanda dakin keda sanyi, kashe wutan dakin akayi hakan yasa ahankali tasauke ijiyan zuciya tareda lumshe ido.
Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

EPISODE 3️⃣8️⃣

Hakanan jitayi baccin yaki zuwan mata tarasa sukuni bakaramin damuwa ne aranta ba, yace zai

saketa dazaran gaskiya ya bayyana amman kuma yahanata magana da saurayinta mai sonta wanda zai aureta dazaran sun rabu, duka maganganunshi dawomata suke, wani kalan kukane yazo mata taushe bakinta tayi da bargon data lulluba dashi tadinga kuka, tarasa farincikin ta rana daya kawai sabida wani mugun shairi dawani mutum yahada mata, dudda Babanta baida kudi Babanta atampopi yake saidawa akasuwa gidansu babu Ac kaman wannan, gidansu is not mansion kaman wannan, babu motoci agidansu kaman irin manyan motocin gidan nan but she has always been a happy person, kometakeso takeci, Baba nadadewa kafin ya yanka musu kaji but Gwaggo koda yaushe tana cikin yanka mata kaji tana soyamata, dudda lokacin Mandawari baitaba kulata ba ko amsa messages nata still she's always happy, she's always at each she sleeps peacefully clinging to Gwaggo so tight, but rana daya she lost everything she lost her sweet life, kunya da tsoron fita take, zaman aure take dabama tagane kan Auren ba, zama take a inda batasan kowaba, Mandawari da sunan shine kullum acikin sallolinta biyar finally Allah yahadata dashi he loves her so much har yana bata iPhone IPhone dabata taba rikewa a hannu ba, but Mandawari yabata yay yay inviting nata but she couldn't show up duk sabida wannan kaddararren auren duk dan sabida wannan shairin da aka mata, Allah kadai yasan yanda Mandawarinta yake fushi da ita yanzu ina zatasa kanta taji dadi, babu abinda kemata dadi aduniya, cikinta ne taji yadaurenata kanta na sarawa, lallashin kanta tasomayi juye juye tadingayi akan gadon tarasa abinda kemata dadi aduniya, daga baya tashi zaune tayi gashi wutan dakin akashe abinda yakara kara mata damuwa kenan, yaye bargon tayi ahankali tasauke kafafunta sama dudda dakin ba duhu mikewa tayi ahankali tana shafa bango kaman mayya tana kokarin locating bayin dataga yashiga dazu, jin ta taba kofa yasa ahankali ta murda kofan tabude wani kalan farin bayine tsaftaccen gaske ita har tsoron shigama tafara dan karta mai datti da bayin ganin yanda hasken bayin ke shigowa cikin dakin yasa tadan juya atsorace takalli kujeran dayake kai ya lullube fuskanshi kadaine ke waje dasauri tashige cikin bayin tareda maida kofan ahankali tarufe, tana kalle kalle, wanke fuskanta tayi da ruwan sanyi takalli fuskan nata a madubi idanubta sunyi jajir sun kumbura sabida kuka, bayin tabida kallo ganin bataga towel ba wani drawer mai bala'in kyau datagani takai hannunta har rawa yake tabude towels tagani kusan guda 10 farare tass anmusu wani kalan rolling ninki sotake tadauka tadaura amman yanda taga an gyarasu awajen yasa tsoro ma yahanata tabawa, bayin tashiga kallo tana kallon sabulan wankanshi kadai kusan 13, different shower gel na maza, da scrubs dakuma set na bubble bath, abubuwan dayake dashi ko ita batadasu bayin sai kanshi yake bude kofan tayi ahankali tafito ta maida tarufe tana daddafa bango tawuce takoma gadon ta kwanta ahankali tacigaba da rolling still takasa bacci sai wajajen 2:30 bacci yay awon gaba da ita.

Tashi Abee yayi ahankali ya zauna dan all this while ba bacci yakeba yan addu'a yayi 3 dot as usual yatashi yawuce bayi alwala yayi yafito yahau kan dadduma yafara salla har zuwa 4:00 yanakan dadduma sannan yatashi bayi yashiga wanka yayi yafito da pj dinajikinshi yawuce closet nashi shiryawa yayi cikin wani jallabiya fara kal da hula sai kamshi yake zubawa yafito ko kallon gadon baiyiba dan yasan ba salla takeba yabude kofa yafito tada mutanen gidan yayi suka wuce masallaci.

Wuraren 6 tabude idanunta ahankali tanabin dakin da kallo daya kunna wutan ciki, gently ta tashi zaune kaman wacce ta tuna wani abu saikuma ta yaye bargo tasauka daga gadon dasauri tana kallon zanin gadon ganin bata batamishi ba yasa harwani ijiyan zuciya ta sauke, agurguje tashiga gyara gadon dan amike taga bedsgeet din kaman ba'a kwana akai, maida bargon shima tayi ta shimfida yanda tasameshi sannan tajuya tana bin dakin da kallo dakin komi white kar kar sai kamshi kaman kada kafita shi karan kanshi dakin nauyin kallo yake mata kaman mai dakin naciki, kaman yana kallonta daga wani waje wucewa tayi tafita daga dakin dasauri tawuce dakinta tabude kofa tashiga babu Gwaggo adakin ko ba'a fadamata ba tasan tasauka kasa ne bayi direct tawuce brush tayi tai wanka tafito tasake shiryawa tsaf wani gown tasaka very simple mai ruwan ganye daya tsayamata a guiwa sannan ta feffeshe jikinta da turare tasake kwanciya agado tanajin wani sabon ciwon ciki dan rabonta da magani tun wanda tasha jiya, bude kofan dakin akayi Anty Binta ne murmushi tayi ganinta sanye da gown idan tasaka kaya saitayi daban saita kara kyau, karasa shigowa dakin tayi da katon tray tace “sauko kiyi breakfast kisha magani bari nakawo miki atampopinki da aka gama dinkawa jiya daman sabida bakida lafiya ne nan baki ba” tana ijiye tray akasa tawuce tafita, saukowa tayi ahankali tazuba shayin a cup tana kallo, bude kofa Anty Binta tayi tashigo dawani katon ghanamasgo dan anan telan ta lodo kayan bin Anty Binta tayida kallo data wuce gaban wardrobe nata tashiga jera kayan itakuma ahankali tadauki tea ta shanye tasss, takasa cin daidai da kwai kawai babu abinda kemata dadi ko kadan dawowa wajen Anty Binta tayi tadauki magungunan ta tashiga ballo mata tace “ga maganin kisha tundadai yauma baraku hadda ba sai kuma next week ke ba lafiya Kausar kuma wai bazata ita kadaiba saikace da chan ba ita kadai ke zuwa ba” tabe fuska tayi ganin maganin da Anty Binta ke bata, Anty Binta tace “wlh ko kisha kona fita nakira miki Yaya Imran daman yadawo” hannu tamika mata dasauri kaman zatai kuka tace “ai zansha” runtse idanu tayi tasha kaman zatai amai da sauri Anty Binta tabata tea tasha sannan ta tashi zatahau gado Anty Binta tace “sauka kizauna bakisan babu kyau dazaran mutum yaci abinci Ya kwanta ba, baida kyau sannan yanasa kiba, yanasaka katon ciki, medically kuma yanasa abinci yadawo maka har hanci tashi muje falo ki gaida su Hajiya saiki dawo ki kwanta tunda bakida lafiya” Gyadamata kai Lujain tayi tamike tsaye ahankali tareda saka slippers zata fita Anty Binta tabita da kallo yanda manyan hips nata ke shaking a rigan are way too sexy, wani kalan crazy sexy shape ne da Lujain babu abinda batadashi all this chubby orobo fine yaran nan she's just one, gashi su Harun da Musty duka abokanen Ya Imran na falo idan akwai one thing datasani kan Ya Imran lokacin tun Mamansu Kausar na raye shine yanada bakin kishi dudda dai Lujain bawai sonta yake ba kokuma yadauketa matsayin mata bane still bazaiji dadi tafito falo haka gaban abokanenshi ba babu ko dan kwali gatada gashi duk wanda zai kalli kitson shukun kanta saiya kara sabida yanda yay kyau bakin kiston duksun warware ma tsabagen santsi sunyi coils, “Lujain” Anty Binta takirata dasauri ganin harta bude kofa, juyowa tayi Anty Binta takalleta tace “zoje dauki hijabi kisaka” Gyadamata kai Lujain tayi takoma tashiga cikin dakin tana tafiya ahankali Anty Binta na kallonta dan bata saka bra ba yau ko singlet dinma bata saba rigan kawai tadaura ajikinta Anty Binta tace “maisa baki son saka bra Lujain batun yau na lura ba bakison nonon ki zasu zube ba” karasa saka hijabin tayi tareda lankwaye kanta murya chan kasa dan yau ko magana ma bason yinshi takeba tace “ni damuna yake” yanda tai maganan

Anty Binta takalla saikuma tai murmushi tace “muje” mamaki kawai take da har yanzu Abee bai farason Lujain ba she’s damn adorable, yanda yake abubuwa ashagwabe, her expression, dan karamin pink lips nata, kumatunta are just so sweet and too cute to watch, she just wish inama Allah zai bata diya Yar chubby haka kaman Lujain daba karamin dadi zataji ba.

Tunkan takarasa saukowa Gwaggo dake falo suna hira dukansu Maman Aneesa, Ibro da matanshi, Hamza, Musty, Harun da matarshi Amina dakuma Hajiya, Gwaggo ta dama musu fura mai dan karan dadi har Hajiya saida tasa aka zubamata tanasha shima Abee na rikeda cup a hannunshi yanasha yanadan danna wayan dake hannunshi baya amsa hiran dasuke, ganin Lujain da Anty Binta yasa Gwaggo takafe Lujain da idanu saikuma tajuya takalli Abee da hankalinshi kekan waya tace “Imrana wai wani mai kasiyama Lujain ne haka kaga yanda takara uban haske kuwa wannan ai zabiya take neman zama Innalillahi” Anty Binta dahar sun karaso cikin falon da Lujain da kanta ke kasa sabida yanda Gwaggo tasa duk ake kallonta tace “Gwaggo man datake shafawa bayasa haske ko daya nima shinake shafawa kawai gyara jikine dashi yasa asalin kalan fatarka tafito bagashi ni ina shafawa ba amman ni baka ce” baki Gwaggo takama tace “ba shakka ai haka mahaifiyarta take nan fara tal usulin bafulatana, Maman mahaifiyarta takoya mini yanda ake fura da nono, toke rashin lafiyan har bakinki yakama ne Lulu kinzo kinga tulin jama’a baraki gaisuwa ba” sauke kanta kasa tayi ahankali tana wasa da fararen yatsunta tace “ina Kwanan ku”.
Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI

EPISODE 3️⃣9️⃣

Murmushi kowa na dakin yayi mata duk suka amsa suna mata yajiki ahankali ta amsa feeling so uncomfortable tarasa maisa kowa ke kallonta, zuwa Gwaggo tayi kusada ita tazauna tana mika mata cup dake cike da fura tace “ga huran ki to” makema Gwaggo kafada tayi tana turobaki dan haushin ta takeji sosai datasata taje ta kwana dakin Abee murya chan kasan makoshi kaman

munafuka dan batason wani yajisu tace “bara’a shaba din” ta harareta tareda juyarda idanunta karaf suka hada idanu da Abee da idanunshi ke kanta hannunshi rikeda cup na furan, wani kalan kunya taji dasauri tasauke kanta kasa, Gwaggo tace “to mekikeso nafa miki har farfesu iyyee Lulu wai mesa aduniyan nan da tsufa na idan baki bani wahala ba bakijin dadi ni kadai ne me jika aduniyan nan jibi Hajiya dan Allah bulbul da ita bata komi saidai amata amman nida nama fita tsufa nine kema jikata aiki, Allah ma zuciyata yagani yabani karfi izuwa yau ban gurgunce ba” kowa na falon danne dariyanshi yake Musty ne yace “Lujain mezakici to”? Dan dagokanta tayi tadan kalleshi saikuma takalli Gwaggo dukdan ta kule Gwaggo tace “tuwoo” baki Gwaggo takama tace “wlh karya take babu abinda Lula ta tsana kaman tuwo wahalar dani kawai takeson yi” for the first time dan murmushin mugunta Lujain tasaki murya chan kasa irin ta marasa gaskiya tace “ni kitashi kimin” tai maganan tana juyarda kanta gefe still tana murmushin muguntan karaf tasake hada idanu da Abee dake mata wani mugun kallo dasauri tadauke kanta Hajiya tace “Lujain zakici tuwo da gaske idan zakici saikuje kitchen dake da Kausar dakuma Maman Aneesarh ta nunnuna muku komi kuyi kidaina wahalar da kakanki babu kyau kinji” ahankali ta gyadama Hajiya kai, murmushi Hajiya tayi tace “zakici tuwon ne da gaske”? Girgiza mata kai tayi tace “a’a tea zansha” yanda tai maganan kaman ka cinyeta it was so sweet, Hajiya tace “tafi dinning Kihada tea kisha tea ki kinji” gyadamata kai tayi tamike tsaye ahankali tawuce feet nata Abee yabi da kallo kaman jini zasu fito wani iri yaji yanda kowa ke ganin kafan nata zai dinga sata tana saka safa, zama tayi a dinning tahada tea awani big cup tafara sha abinta sukuma yan falon sai hira suke, kowa na falon yay mamakin yanda Abee yazauna yanajin hiran dudda baya cewa komi but zaman kadai dayayi zai nunamaka yanajin dadin hiran.

Saida tagama shan tea danshi tasha sosai bataci egg da chips ba sabida yanda cikinta ya cushe, kitchen tawuce ta wanke cup datai amfani dashi ta ijiye sannan tafito tawuce sama tana tafiya ahankali tana kama karfen bene dan cikinta yafara ciwo daga cin abinci, tana shiga dakinta Hijabin tacire ta ijiye kan gado tareda tsugunnawa anan kasa tadaura kanta saman gado tarike maranta kaman wacce ke nakuda, jin cikin yafara usulin ciwo kaman zai kasheta yasa ahankali tafara. “Wayyoooo cikina Gwaggoooo” saikuma tafashe da kuka ahankali ko kadan batada dauriyan ciwo tun tana yarinyar kodan sabida yanda ko bigewa tayi Gwaggo tadinga riritata kenan yasa oho amman dai batada dauriya ko kadan.

Bude kofan dakinta akai ahankali hakan yasa dasauri tadago kanta tareda juyowa takalli kofan da rinannun idanunta Abee ne yana tsaye jikin kofan yazuba hannunshi a aljihu yana kallonta, kokarin mikewa tsaye tayi ahankali tana dafa jikin gado ahankali sannan tajuyo tadan kalleshi tana yarfe hannu, anatse yace “kinsha maganin ki?” Girgizamai kai tayi ahankali tana goge fuskanta da bayan hannunta, anatse yace “dauko maganin kizo nan” gyadamai kai tayi tajuya ahankali tafara tafiya dan magungunan nakan mirror, wani kalan dauke kai Abee yayi daga kallonta dayakeyi, daukan ledan maganin tayi tajuyo ahankali tazo dan nesadashi ta tsaya

tareda mikamai ledan sai alokacin yajuyo ledan yasa hannu Ya karba batare daya kalli fuskanta ba yace “ba’ashan magani da ruwa ko” dasauri tajuya wani bottle water na sabo tadauko tajuyo tadawo tasake tsayawa nesa dashi, dago idanunshi yayi yazubamata hakan yasa dasauri hannunta har rawa yake tashiga kokarin bude goran ruwan amman takasa dan ba karfi, hannunshi yamika mata alamun tabashi hakan yasa ta mikamai goran da sauri karba yayi murdawa daya yabude mata goran sannan yabata karba tayi ahankali takurbi ruwan magungunan daya ballo yabata a hannu kaman zatai kuka babu yanda ta iya ta watsa maganin bakinta tahadiye tana tabe fuska takai ruwan bakinta tashiga kwalkwala kusan rabin goran tasha sannan tasauke goran mika mata ledan magungunan yayi ahankali tasa hannu ta amsa yajuya saikuma ya tsaya chak batare daya juyowaba hakan yasa ta kalleshi, anatse yace “stop wearing irin rigunan nan agidana!” Yana maganan yawuce turo baki tayi tareda maida kofan tarufe murya chan kasa tace “nima kayan gabaki daya sun isheni” tai maganan tana komawa gado kwanciya tayi tana juye juye dan cikin ciwo yake mata ahankali yafara lafamata ahaka bacci yay awon gaba da ita.

Wuraren 1 tafarka ita kanta har mamakin baccin datakeyi take, Gwaggo tagani adakin tana karkada magunguna ganin ta tashi zaune yasa Gwaggo ta washe baki tace “sauko kizo kigani Lulu nadafa miki kaza da tantabara” hararan Gwaggo tayi tawuce ta tafi bayi, Gwaggo tace “wai baraki daina fushi dani ba Iyyee Lulu sabida namiki Auren gata, jibi yanda yan uwan mijinki keji dani, kinsan nawa abokanenshi suka bani, dukansu dubu Hansin Hansin fa, Mujittafa Hamsin, Haruna Hansin, saikuma dan sandan nan Abdul hansin, ai wlh kinyi saa kinzo katon gida ga jama’a aciki kuma kowa na sonki ni Allah ma makirin dan iskan nan daya batamuku suna Albarka dan abinda yayi yazame miki alkhairi” tana maganan wayanta yashiga ringing wayan ta kalla tace “ai nasan ubanki ne kome zakayi baran dawo gidanka gidan wahala ba, dana dinga rokonka ka kaini ka kaini ne ina ba saida nakira surukina ba da Allah yabani number shi da kyar ba oho saikuma kayi” tana maganan ta ijiye wayan tacigaba da abinda takeyi, fitowa Lujain tayi daure da towel taje gaban wardrobe nata ta shirya tsaf takara komawa bayi ta ijiye wannan towel din tadauko sabo blue ta daura tazo tazauna kusada Gwaggo data ijiyemata kula agabanta, bude kulan tayi tana turobaki sanan tashiga cin naman Kazan dana tantabara da Gwaggo tamata farfesu dudda farfesun magani ne amman bala’in dadi, tass ta cinye ta ijiye kasusuwa koba komi tayi kewan Gwaggon ta wani ruwa Gwaggo tabata na sayuwa tace “sha wannan babu daci ko kadan kaman ruwa ne” dandanawa tayi jin babu daci yasa ta shanye tace “Gwaggo me shi”? Wani Leda Gwaggo ta ijiye tace “ba’a fadima yara meshi, anjima zakisha wayan nan su Abida sunce na gaisheki ” wani kalan murmushi tayi tace “Gwaggo ai tare zamu koma ko”? Dan kallonta Gwaggo tayi saikuma tai kaman bataji ba, Ahankali Lujain tace “Gwaggo bana iya bacci agidan nan, ban sansu ba, bansaba dasu ba, Gwaggo kuraba auren Mandawari zai aureni” wani kalan dakuwa Gwaggo tamata tace “wlh idan kina kiramini sunan wani namiji kina matan aure saina makeki Lulu” kaman Lujain zatai kuka tace “toni nagaya muku ina sonshi ne, ni wlh Mandawari na nakes……..” empty farantin roban gaban Gwaggo data gama kwashe magungunan ciki ta dauka ta rapka mata akai tace “rufamini baki” wani kalan ihu Lujain tayi gabaki dayama ta manta ba a gidansu takeba dan haka take agida idan

Gwaggo ta bugeta Aiko ranan tashiga uku saita lallasheta da kyar sannan zatai shiru, wani kalan mikewa tsaye tayi da towel din tana kuka sosai amugun shagwabe tabude kofan dakin tafita Gwaggo data bitada idanu tace “aisai kiyi fitsarariya” daidai tana fitowa tana kukan ta kama kanta da Gwaggo tabugama plate daidai Abee nashigowa saman ita ko kadan batama luradashi ba, tundagakai zuwa kafa yabita da kallo yadan tsaya yay jim kaman yajuya yakoma falo saikuma yacigaba da tahowa ko kadan bataji sahun takalminshi ba as usual kamshin turarenshi kadai yagayamata yana wajen hadiye kukan tayi tass sannan tadago kanta kaman munafuka tana sauke hannayen kasa, hada idanu sukayi dawani kalan sauri tajuya zata bude kofan dakin tashiga yace “come here” dawowa tayi ahankali kanta akasa tashiga wasa da yatsunta dan she’s so restless, “what happen”? Taji Abee yamata tambayan muryanshi ataushashe, dago kanta tayi takalleshi saikuma ta kwabe fuska kaman zatai kuka taredakai hannunta saman kanta inda Gwaggo tabugama plate tace “Gwaggo ne tadakeni tabugamin plate akai” kanda ta taba yabi da kallo ga wajen har datti datti na abinda ke plate din ke wajen, kaman baraiyi magana ba saikuma ashanyaye yace “what did you do tadakeki?”.EPISODE 4️⃣0️⃣

Jama’a I am back! Wannan littafin nawa zaku sameshi a all my social media platforms 💃 idan kuma kuna bina a Instagram ko Tiktok su akodayaushe zai kasance sun wuce yan WhatsApp da page biyu💃💃

Ku danna link dinnan dan following dina a Instagram;
https://www.instagram.com/p/CnmsOO8I0XL/?igshid=MDJmNzVkMjY=

Ku danna wannan link din dan following dina a TIKTOK;

https://vm.tiktok.com/ZMYekGsQV/
DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINKAI
Dago manyan idanunta tayi ta kalleshi yanda ya tsareta da idanu yasa takai bayan hannunta tagoge fuskan nata tass murya chan kasa tace “sabida nace zan bita idan zata koma gidan mu” tunda take maganan lips nata da kumatu yake kallo, dauke kai yayi yace “jeki cemata nace takara miki” dasauri tadago idanunta takallai, wani mugun kallo yamata yace “tunda bakijin magana, what did I tell you about this thing” yay maganan yana pointing towel na jikinta da hannu, dasauri ta tura kofan dakin tashiga tareda maida kofan yarufe girgiza kai kawai Abee yayi yawuce yatafi dakinshi.

Tunda Gwaggo tashigo gidan gidan yakara wani kalan dadi da annashuwa Baba yay kiran dubiyan nan Gwaggo taki dauka wai ita barata komaba saitagama hutun datazoyi agidan nan koda wasa kuma babu wanda yataba muna ta isheshi koyagaji da ita saima dawowa datayi kaman itace asalin Gwaggon gidan.
Kullum dare Gwaggo saita kadata dakin Abee dakin Anty Binta take zuwa ta kwanta dan Anty

Binta ta tafi gidanta babu kowa adakin, ita rabon datasa Abee a idanu tun ranan Sunday dan Hamza ne ke kaita school yanzu, hakama Mandawari abin bakaramin damunta yayi ba bata ganinshi gashi babu halin taje koda kofar gidansu ne dan ba fita takeba.

Yau juma'a Baba cire kunya yayi shida Hadi sukazo har gidan bayan magrib awaje suka tsaya dan gani sukayi Gwaggo batasan abin kunya ba tazo gidan da jikanta ke aure ta tare tun ranan asabar haryau juma'a kwananta shidda kenan haba mana ai bai daceba.

Abee na masallaci Abdallah yazo yakirashi baiwani jimaba yafito tareda Abdallah har zuwa wajen su Baba cikeda girmamawa Abee ya gaidasu, Baba shima cikin mutunci yace "Imrana dan Allah kuyakuri da halin Gwaggo wlh fitinace da ita haba tazo ta tare taki tafiya" dan murmushi Abee yayi yace "bakomi bismillan ku" dasauri Baba yace "ai muna nan munriga munsa maigadi yakirata ta fito mutafi" danjim Abee yayi dan baisan mezaice ba, ahankali yace "dan Allah ku barta duk randa takeso saita dawo" dasauri Hadi yace "Bakasan Gwaggo bane Imrana bazata taba dawowa ba"……..

Sosai Gwaggo tafashe da kuka afalo kowa na falon lallashinta yake tanuna kanta tace "ni su Hadi kema bakinciki sabida nazo gidan jikata nahuta shine harda zuwa har kofar gida amaidani gida karfi da yaji ko…." Bude kofa Abee yayi yashigo Gwaggo takallai tana sharce hawaye tace "Imrana sunki tafiya sunce saisun tafi dani ko"? Dan shiru yayi yakalli yanda Gwaggo ke kuka dakuma Lujain dake gefenta ahankali yace "eh" saikuma yawuce sama baiwani dade saman ba yafito da bandir yan 1k guda biyu a hannunshi yazo har gaban Hajiya yabata alamun tabama Gwaggo, murmushi Hajiya tayi tabama tace "Gwaggo gashi Imrana yace abaki" ganin kudade mikakku farare fes yasa duk wani kuka da Gwaggo take ya tsaya tace "wayyo Allah na dubu dari biyu, Imrana nagode nagode Allah maka albarka ubangiji Allah yakawo ciki da goyo tsakaninka da Lujain bari natafi" tamike tana tura kudin lalita duka yan dakin murmushi sukayi, tashi Lujain tayi kaman zata bita tace "Gwag……" wani kallo da Abee yamata yasa dagudu ta juya tai stairs tana kuka Gwaggo tace "aisai kiyi tunda bakida hankali ne da aurenki zan tafi dake jama'a saduwan Alheri" duk rako Gwaggo sukayi har compund ta tafi Abee kuma yakoma masallaci.

Sosai Lujain tai kuka jitayi zuciyanta yamata nauyi da zafi Kwanan nan da Gwaggo kenan gabaki daya ta manta menene bakin ciki ko fushi har damuwan Mandawari ta manta dashi amman daga tafiyan Gwaggo saitaji komi yamata duhu sosai ahaka bacci yay awon gaba da ita.

Tun wajajen 3:30 tafarka tabude idanunta hakanan kawai gabanta sai faduwa yake abin namata kaman ma zazzabi zazzabi takeji, saukowa kasa tayi ahankali tareda daura kanta akan gado hawayene yazubo mata she's soooo sad and she's hungry again, all abinda takeso shine taganta agidansu.

Bude kofa Abee yayi 4 dot yafito sai kanshi yake yau Jallabiya ce ajikinshi fara da hula akanshi kofan Lujain ya kalla saiya karasa wajen anatse yabude kofan dago kanta tayi takalleshi suka hada idanu kafinma yamata magana ta mikeda sauri tawuce bayi dan haushin shi takeji daya hanata bin Gwaggon ta jiya dan jim yayi ya tsaya kaman mai tunanin wani abu saikuma yajawo kofan yarufe yawuce yatada su Abdallah yasauka kasa yajirasu suka fice tare zuwa masallaci.

Dayake yau asabar yadade amasallacin sai wajajen 7:00 nasafe yafito tareda Baba Liman dawasu jama'a na masallacin duk sun tsaya gaban masallaci suna magana kan Solar da Abee yasayoma masallacin daza'a fara aikin yau kaman an jefo mutun kawai wani saurayi suka gani agabansu ya tsaya yana sanye da jean da Riga bakake yasaka bakin facing cap da nose mask da bakin glasses dudda sunada yawa amman Abee yake facing, daya daga cikinsu yace "kaikuma Malam lafiya haka"? Tsugunnawa yayi agabansu ahankali tareda saka hannu yazare facing cap din kanshi, sannan yasa hannu yazaro shades din ya ijiye sanan yacire nose mask din ahankali ya ijiye kasa kafin gently yadago jajayen idanunshi dasuka kumbura suntum yakalli Abee dake kallonshi, dasauri jama'an wajen suka nunashi sukace "bakaine mutumin dayama Alhaji Imrana shairi ba ai munga hotonka a news" gyadamusu kai yayi ahankali sannan yahade hannayenshi yana kallon Abee dake kallonshi kuri saikuma kaman wanda ya haukace ya kwala uban kara cikin harshen turenci yace "mutanen estate din nan kufito dan Allah, gani nan nine nama Alhaji Imrana shairi nakuma kawo kaina da kaina" daidai lokacin Mandawari yafito daga cikin gidanshi zai tafi gudu chak ya tsaya yana kallon gaban masallacin da jama'a suka taru harda masu gadikan anguwan dakuma mutumin hakan yasa yakarasa wajen daidai Ibro shima yana karasawa wajen dan fitowanshi daga gidanshi kenan yazo zai shiga gidansu yaji muryan mutumin hakan yasa yashiga kiran Hamza, kallon duka mutanen dake kallonshi kuri yayi mutanen kuma suka cicciro wayoyinsu ana video yakalli Abee yace "dan girman Allah kayafemini wlh wlh bantaba sani hakkin wani abune mai girma ba sai bayan namuku kazafin nan kaida wannan innocent yarinyar" yay shiru dasauri Hamza yashiga kiran Uncle Abdul Police shikuma Ibro yashiga kiran Uncle Musty, cikin wani kalan yanayi na tsantsan nadama yace "tun bayan nai editing video nasaka a yanar gizo nakasa samin kwanciyan hankali dudda nai deleting amman a banza dan yarigaada ya yada duniya, bana iya bacci, banda sukuni banda natsuwa, kirjina da kaina wani kalan nauyi sukemin kaman an dauramini tankin ruwa akansu, tundaga ranan dana watsa video nan idanun nan nawa basu kara runtsawa da sunann bacci ba wlh wlh da wannan azaban gwara nakawo kaina ankaini gidan yari, nazone nafara rokonka da yarinyar gafara kafin nakai kaina dakaina police station dan Allah dan girman Allah kuyafemini, jama'a kutayani rokon gafara" yay magananan yana kallon kowa na wajen saikuma ya shiga babbbaka kuka sosai kana ganinshi kasan babu peace arayuwanshi, ko'ina najikinshi rawa yake yace "wlh wlh koda wasa ba fasikanci sukayi ba nine na maida abin yazama haka da editing na computer, wlh nine nan na shirya komi nahada wlh wlh shairin shaidan ne da ruwan ido da son abin duniya yakaini na aikata abinda nayima Ogana mutumin daya bani aiki nake samu naciyar da yan uwana tasanadiyanshi shine nama haka dan Allah kuyakuri" kallon Baba Liman Abee yayi yace "Baba bari nashiga gida" gyadamai kai Baba Liman yayi hakan yasa yajuya zai wuce karaf mutumin yakama kafarshi tareda kwanciya akasa awajen flat yana kuka sosai yace "dan girman Allah ka yafeni kona samu na rufe idanuna yau ko baccin minti biyu ne nayi dan darajan

